*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

*✍🏻✍🏻BAKAR FURA Ibr ne da yafaru da gaske, wanda yake dauke da Soyayya me kayatarwa, ga tarin Nishadi, ban al'ajabi tare da ban tausayi, gameda fadakarwa, wadan da abun ya faru dasu muna nan muna cigaba da rayuwa tare dasu cikin wannan duniyar tamu,Allah yabani ikon isar da sakon yadda ya dace.*

*Episode 1- 2*

BISMILLAHIR RAHAMANIR RAHIM

Cikin kasar CAMAROON (1995)👈

_Alif dubu daya da dari tara da casa'in da biyar_

Ke!! Ke!!! dakata maza ki tattara kafafuwan ki ki koma gida.

Cak yariyar da ake dakawa tsawan ta tsaya cikin yanayin rashin jin dadi.😔

Wasa ta shigayi da fararen yatsun ta, tare da zuba masu ido, saidai ko motsi batai ba bare ta juya kamar yadda matar dake zaune gefenta ta bukata.

Cikin fullaci matar ta sake mgn kamar yadda tayi da fari tace, " wai badake nake mgn bane kika min tsaye"?

Har yanzun yariyar na tsaye bata juya ba, ko motsi ma batai ba, fitowan wata dattijuwa tana fadin yaya akayi ne?, yasa su duk suka kalleta"

Itako wannan matar kawar dakai tayi can gefe.

Kallo tattijuwar tabi matar dashi sannan ta kalli kyakyawar yariyar dake tsaye tayi murmushi ta matsa gefenta tana fadin *Aysha* zo ki wuce.

Cikin sunkuyar dakai yariyar ta wuce, tana waigen wannan matar, bayan ta kulle ne matar tabi bayan yariyar da harara ganin dattijuwar na kallonta tai saurin dauke kanta can gefe cikin yanayin jin kunya.

Matsowa dattijuwar tayi kusa da matar tana fadi cikin harcen fullaci, " Fatima kibar kyaran ta"

Batare da matar ta juyoba tace " Innawo kina kallon fa yadda 'yan gidan su suke nunawa baro baro basu son shigowar ta.

Duk cikin harcen fullacin suke mgnr da alama fullacin kawai suke ji bisaga la'akari da yadda ya rike bakin su.

Me ya dame ki?, wani ne yaje ya kirata ne?, inace ita ta kawo kanta?, babu ruwanki, idan har basaso su dakatar da ita daga can.

Batare data juyo ba tace shike nan.

Zama sukayi suka cigaba da hira har tsayon wani lokaci, zuwa can *Aysha* ta fito hannunta dauke da littafai, inda suke ta kalla cikin sakin fuska tace, "natafi"

Innawo ce kadai ta amsa sannan ta wuce ta fita.

Hira Innawo sukaci gaba dayi, zuwa can na hango wani zafgegen saurayi, wankan tarwada shiba fariba Kuma ba baki ba, dogo, kwantancen saje gewaye da fuskarsa, kananan kaya ne ajikin sa yana takawa da karfi irin na jajartattun maza, idon sa tubarkallah, mayya ne, ko ince wadatattu, tafe yake fuskarsa kadaran kadaham, shiba fara'a yake ba, Kuma ba daureta yayi ba, wuce su Innawo yayi yana kokarin barin gidan yaji ance zonan"

Cak ya tsaya tare da dawowa baya yana binsu da kallon kasan ido yace gani"

Naga ka wuce ne kamar bakasan damu agurin ba?

Naga ganku, nace sannu ku ai"

Cikin lumshe ido matar tace bamuji ba.

Innawo ya kallah sannan yace Innawo kema bakiji ba?....

A'a babu ruwana, wannan mgnr ku ce naga dai kamar ka motsa leben ka ko?

Kawar da kansa yayi sannan ya juyo ya kalli matar data daure fuska sosai ya hadiye yawu tare da fadin, toh Ummi sannu ku"

Kawar dakai tayi batare data amsa ba, ganin haka ya dan sake kallonta yana sake fadin, bari naje na dawo"

Ahankali tace adawo lafiya"

Allah yasa, yafada sannan ya juya ya fita.

*******

*Aysha!!!*

Na'am Mama!

Mikewa tayi ta fito da littafanta a hannunta da alama karatu take yi"

Jikin mahaifiyarta ta fada cikin nuna tsananin so ta rungumeta tacin fullacin tace"

*Aysha* baki gajiya da karatu ko?, yau ko abinci banga kinci ba fah"

Mama banjin yunwa"

Inafa zakiji yunwa tunda kin rike littafai"

Karatu nake mun kusa fara jarabawa"

Littafin dake hannunta ta karba ta duba cikin yamutsa fuska tace"

Wannan ba rubutun ki bane, bayan littafi ta duba sannan ta kalli *Aysha* tace, littafin naki ne, rubutun fa na waye?

Dagowa tayi daga jikin  mahaifiyar tata tana me kallon cikin idonta cikin alamun rashin gaskiya tace"

Ya *Aliyu* ne ya rubuta min.....

Cikin zafi ta make bakin Aysha tana fadin, yaushe kika sirare kika fita?, wato ke bakijin mgn ko?

Rike bakin Aysha tayi idonta na tsiyayan hawaye tace, Mama idan banje ba waye ne zai koya min karatun?

Mama ta bude baki zatayi mgn wata tsohowa ta fito daga wani daki tana fadin"

Ai sai kinyi da gaske idan kina son ki raba Aysha da yaron nan, ai ina kallonta sanda ta fita zuba ido kawai nayi, tun dake kin bari ni yaya zanyi?

Nifa Umma bahaka bane, ai dole sai kun tayani, idan anga tayi abun da ba daidai ba a kwaba mata"

Cikin kawar dakai tace shikenan, abin da yafi Sam ahana ta shiga wannan gidan, gaba daya, idan mu kin rainamu baki tsoron mu nasan dawa zan hadaki, gaba daya yayyen uwar ki zan sanar abun da kike yi"

Ganin Inda Umma ta Kura mata ido ta kalli mama sannan tai kasa da kanta.

Umma kuwa haka taita maganganu yayin da Mama ke taya ta, *Aysha* kuwa saurare kawai take"

Washegari da misalin karfe 2 *Aysha* ce ke tube kayan makaranta sannan ta saka yar karamar riga da siket dinta daidai guiwa, irin me budewa gaba daya, littafinta ta ciro guda daya tare da biro ta zauna tana fakan idon su Umma dake aikin girki can bakin kitchen, ganin sun maida hankalin su sosai kan aiki ta wuce suf suf ta fice"

*******

Ahankali ta tura kofar bakinta dauke da sallama.

Dagowa saurayin yayi ya kalleta sama da kasa sannan yai saurin dauke idon sa ya maida kan yariyar dake zaune gaban sa tana rubutu cikin littafin dake gaban ta"

Karasowa tayi kusa da yariyar ta zauna yayin dataga saurayin ya sake dagowa ya kalleta akaro na biyu, kallo ta bishi dashi yayin dataga kamar yana motsa lebensa, kallo taita binsa dashi Kamar yadda shima yake binta dashi saidai bata ankara ba taji ya buga wata irin tsawa me rugugi wadda yasata sakin littafin da biron batare data shiryar ba, bata ankara ba sai ganinta tayi akofar gidan cikin yanayin haki ta tsuguna tana maida numfashi"

Dariya taji asaman kanta dan haka tai saurin dagowa ta kalli yariyar sannan tayi ajiyan zuciya tace"

Husna me namai?

Cikin matsanancin dariya wadda aka Kira da suna Husna tace yace kizo"

A'a nikam bazani ba"

Dariya Husna ta sake yi sannan tace tashi muyi sauri mukoma karyace mun dade, muje ba abun da zai miki"

Cikin rashin fahimta tace mena mai toh?

Ke dai muje mana"

Wlh Husna masifar tsoron wannan tsawar tasa nake"

Jikin Aysha Husna ta kalla yadda jikinta ke buga uban rawa ta kara fashewa da dariya tana fadin, " aikuwa kina da aiki"

Daker Aysha tace kemafa kina firgita idan yayita"

Ina firgita amman jikina baya rawa, waigawa tayi ta kalli fokar gidan nasu sannan tace kitashi muje.

Ahankali suka shiga dakin, Husna agaba *Aysha* nabinta abaya cikin tafiya ahankali har suka isa gaban shi"

Zama sukayi duk su biyun yayin da *Aysha* ke Satan kallon shi, ganin da tayi Kamar bashi ne ma ya buga tsawar dazon ba tayi ajiyan zuciya adaidai lokacin da yace, matso ke"

Cikin tsoro sosai ta matsa gabansa, wani irin radadi taji a tsakiyar kanta, dan haka tai saurin runtse ido tare da yamutsa fuska cikin yanayin dake nuna tanajin zafi"

Shikuwa Aliyu kalabar dake kanta ya rike tsoro biyu tun daga tushen su yake fadin meyasa baki rufe kanki ba?

Macewa nayi ya *Aliyu* kayi hakuri.

Mantuwa fa kika ce?, Shekarun ki nawa?

Dan Allah kayi hakuri bazan Kara ba"

Tambayan ki nake ai, shakaran ki nawa?

Kasancewar yana Kara matsewa hakan ke Kara sata rikecewa cikin sauri tace, goma sha

uku"

Kawar dakai yayi batare daya saki kan nata ba yace, toh kinji goma har sha uku, amman kika iya tsallako gida nawa kika taho ahaka, gida nawa kika tsallake kafin kikazo nan?

Wayyo Allah, dan Allah kai hakuri kaji"

Sakin kan yayi da sauri yana fadin nayi hakurin, amman karna Kuma ganin ki ahaka"

Kanta ta gyada tare da kokarin share hawayen ta.

Aliyu kuwa Husna ya kallah yace, kuje kibata zani da hijjabi, Amman kuyi sauri fita zanyi"

Cikin kankanin lokaci suka dawo sannan yai masu karatun kamar yadda suka saba, cikin lokacin dabe wuce awa daya ba suka gama, a tare suka fito cikin sauri yabar gidan yayin da *Aysha* ma ta nufi gida.

*******

Innawo!!!

Gaban Innawo ne ya yanke ya fadi jin Kira cikin fada da hargowa, fitowa tayi tana zare ido ganin Umma tsaye atsakar gidan yasa tace"

Au kece?, Lafiya kika shigo babu Sallama?🤔

Kashedi na kawo miki, *Aliyu* ya fita harkar *Aysha*, idan ba haka ba kuwa wlh zan dauki mummunan mataki akan shi"

Subuhanallahi, to wai me yake faruwa ne?

Babu komai kawai ni alakar tasu ce banaso"

Ai basu da wata alaka, Umma ki kwatar da hankali ki, inace *Aysha* gurin Husna take zuwa, so da yawa zatazo tasamu Aliyu nama Husna karatu dan haka itama tafara zuwa da dan littafin ta, ni banga abun tashin hankali ba anan"

Kece baki ganshi ba, nikam  na ganshi, banso ne Sam idan ba haka ba duk abun da ya faru karkuga laifina"

Babu abun da zai faru sai alheri, kuma jikarki indai baki son ta shigo gidan nan ki tare ta acan gidan ki dan nikam ba me gadin ki bace......

Muryan Ummi sukaji tace, "Umma jeki duk ranar da *Aysha* ta shigo gidan nan zan mata korar wulakanci"

Aikuwa dakin birgeni, juyawa tayi tanacigaba da fadin maganganu yayin da Ummi ta Kara kulewa sosai"

**********

Tsayon kwana biyu aka kwasa *Aysha* bata shigo gidan ba, yayin da duk Husna taji wani irin, domin ta saba kullum zasu hadu bayan sun dawo makaranta, gaba dayan su zaune suke a tsakar gida har Aliyu, Ummi ce ta kalli Husna tace, "waike meke damun ki?"

Ahankali tace babu komai"

Aliyu ne ya kalleta ta gefen idon sa tsayon lokaci kafin yace, ke me yake faruwa?

Ummi da Innawo ta kalla ganin basa kallon ta tai kasa da muryar tare da fadin, kwana biyu *Aysha* batazo ba, Kuma Ummi ta hanani fita"

Kallon Husnah yayi sosai sannan ya maida hankalin sa gurin kallon su innawo yana fadin jeki Kira min ita.

Wa za'a Kira maka?, Innawo tayi tambayan tana tsaresa da ido"

Kai tsaye yace *Aysha*"

Aysha?, *Aliyu* Aysha fa iyayenta bason shiguaarta gidan nan suke ba, ko shekaran jiya bayan kagama masu karatu nan kakarta tashigo taita fadar maganganu marasu dadi, ku fita harkar yariyar nan"

Wai akan me take mgnr wai, ya fada yana kallon fuskan Innawo"

Au tambaya keke ne?, Ana cemaka ku fita hanyarta kana tambayan dalili? Ummi ta fada hakan cikin tsare sa da ido, dan haka yadanyi kasa da kansa sannan yace

Naga ai karatu ne ke kawota ba wani abu ba, amman ni meye nawa, shiguwar tata mezata kara min?

Mikewa Ummi tayi tana fadin nima abun da nagani kenan"

**********

Abincin dake gabanta take ta juyawa tare da fakan idon aunty Murja dake gefen ta, tana bude

jakar makarantar ta ahankali ta jawo littafin ta wadda tasaba zuwa dashi karatu kowanni lokaci, rigarta ta daga ta tura shi cikin siket dinta, agogo ta kalla domin tasan ya Aliyu 3 yake fita gashi yanzun biyu har da kwata"

Aunty Murja taita satan kallo daga can taga ta mike ta shiga dakin Umma dan haka tai saf saf ta fice agidan.

*********

Babu kowa a tsakar gidan cikin siririyar muryarta ta shiga sallama daga can Husnah ta amsa mata.

Falon taji Muryan Husna dan haka can ta nufa inda ta hangesu Husna zaune akasa yayin da Ya *Aliyu* ke zaune kan kujera idonsa akan littafin Husna dake hannun sa"

Har Aysha ta zauna beyi mgn ba, Kuma be dago ido ba, ahankali Aysha tace " Ya Aliyu ina yini"?

Lafiya lau ya fada batare daya dago ya kalleta ba"

*Gyara adon mace, komai yanason gyara, idan kina dakyau kira da wanka, dan haka mata atashi agyara, akwai kayan gyara lada da kala sai wadda kika zaba domin gigita me gida, sabbabin amare ina da irin naku, yan mata masu shirin shiga daga ciki kuma akwai naku na musamman cikin rahusa mai sauki, ina aikawa kowanni gari, ina da tabbaci akan kayana, idan kika gwada saikin dawo insha Allahu, gamasu bukata su tuntubeni ta wannan no 07014197556*

Bayan yagama duba littafin Husna yace matso, gaban shi ta isa ta zauna, cikin nutsuwa yake Kara fahimtar da ita saida ya tabbatar ta gane sannan ya tura mata littafinta yana fadin, *Aysha* muga naki"

Mika masa tayi tunda ta shigo har yanzun beko kallesu ba, duk bayanin da yake idonsa nakan littafi, cikin kankanin lokaci ya tura mata littafin bayan ya tattabar itama ta fahimta, sannan ya mike yana sauke ajiyan zuciya.

Aysha!! Aysha!!! Jin wannan Kiran yai matukar firgita Aysha, mikewa tayi da sauri ta koma bayan Ya *Aliyu* tana zare ido.

Tsuhuwar ce ta sake fadin Aysha bazaki fito bane saina shigo na rafke kafafuwan naki sun dagargaje??

Juyawa yayi ya kalle bayan sa da Aysha take lebewa, kallo daya ya mata tai saurin fitowa ta isa gaban kakarta, yayin da tai saurin rike kunnenta ta murdeshi tana cewa, " ke wato kunnen

ki nakashi ne ko?, kullum ana gaya miki mgn bakiji ko?, Ko kullum ba gaya miki ake ki kiyaye wannan abun ba?

Cikin kuka take kokarin kwace kunnenta yayin da Husna take fadin Umma kiyi hakuri dan Allah.....

Ke dallah rufe min baki, da hakurin ta mutu Sadakan nawa kika bada?, ni kujimin mara kunyar yariya wai wani Umma yi hakuri, inyi hakuri in saki jikata sakaka saikace goyon gwauro ?, ba tsari ba lissafi dake ni fitsarriya ce, duk cikin harcen fullaci take mgrn tana iza keyar Aisha

Fitowa Aliyu yayi batare daya kalle inda Umma take ba yake kokarin ficewa daga gidan cikin tsawa Umma tace, "kai!! tsaya yaro"

Cak ya tsaya batare daya juyoba.

Waishin bakaji sakona bane?, nace bakaji sakona bane?, kake wani lumlumshe min idanun ka narashin da'a, nagaya maku gaba daya gidan nan ku fita hanyar jikata, idan baso kuke nai maku rashin mutunci ba"

Lumshe ido yayi sannan ya fara takawa yana kokarin barin gidan, ganin haka Umma ta fara fadin, " ninake mgn kana tafiya, lallai bakasan halina ba, amman zan gwada maka duk ranar da ka Kara kuskura ka kula jikata saikayi daka sanin zuwanka duniya, wawa kawai mara mutunci me zubin 'yan wuta.

Tafe yake tana binsa abaya tana surfa masa zagi harya bude motarsa ya shiga ya zauna yana jiyo ihunta, hankali kwance, yana motar yana me kallon gabansa kamar yadda ya saba, cikin gidan Umma ta koma ganin haka Aysha ta kwace hannunta ta nufi gida.

Kan Husna ta koma ta inda tashiga batanan take fita ba,  saida tagaji Dan kanta tabar gidan"

Sosai ran Husna yake abace, ita kadaice agidan dan haka tasa kuka"

Kusan minti 30 tana kuka sannan su Innawo suka dawo, Ummi ce agaba yayin data tsare Husna da ido, cikin tuhuma tace' " meya sameki kike kuka"?

Umma ce tazo taita zagina"

Cak suka tsaya, yayin da Ummi ke fadin, " zagi"?, akan wanni dalilin me kika mata?

Akan *Aysha* ne Innawo, har ya Aliyu tabi har waje tana zagin sa"

Cikin rashin kwarin jiki tace, " *Aysha* ta shigo ne "?

Eh ta shigo"

Dattijon dake bayan su ne yace wacece Aysha?

Innawo ce tace nan makwaftamu take, kawar Husna ce, gun Husna take zuwa idan taga Aliyu suna karatu da Husna take shiga itama ayi da ita, shine kakar tata bataso, fitinan yau daban nagobe daban"

Cikin tsananin bacin rai Ummi tace, ai Innawo duk laifinki ne, inda kin barni ko hanyar gidan nan akace *Aysha*ta kalla bazata biyo ba, Kuma bari ta sake shigowa gidan nan saina tsintsinka mata mari"

Da sauri wannan dattijon yace kul, karki Tama masu yariya, badai gurin Husna take zuwa ba, kawai Husna ta hado kayanta muje gida"

Shikenan kuwa, Husna dauko kayanki kibi ubanki, cewar Innawo taname cire mayafinta

Lallai yanzun sabo da wata can sai adauke Husna anan?

Cikin nutsuwa dattijon yace wani lokacin zata sake zuwa ai, yanzun dai kam haka ne kadai mafita, Kinga itama kawar tata zatai zamanta agidan su, da haka ne hankalin kowa zai kwanta, daman Husna ai bakuwa ce"

Badan ran Ummi yaso ba ta nufi dakinta cike da bacin rai, domin yayanta alhaji Umar kaifi daya ne.....

Fadeela Lamido✍️

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

*Episode 3 - 4*

Aranar Abban Husna ya wuce da ita kamar yadda yace, sai dai sosai hakan ya bata ran Ummi dan tare suke kwana gado daya da Husna"

Washegari gidan yai masu tsit daman husnan ce kadai yariya, misalin karfe 08:30am Aliyu ya fito cikin Shirin fita bayan ya gaidasu Innawa ya mike yana fadin, " ina Husna"

Ummi ce ta bashi amsa Husna takoma gidan su"

Da saurin sa ya kalli Ummi yana fadin, "sabo dame"?

Sabo da Aysha mana, koba jiya kakarta tazo ta kare maku zagi kaida Husna ba?

Jimmm yayi sannan yace, " saboda tsohuwar kuka tura Husna gida?, rikicin tsofa ne kawai ke damun matar nan ba wani abu ba"

Aliyu taje can tayi rikicin tsofan nata Amman ba anan ba, yadda nake ganin yanayin matar nan masharranciya ce gara mubita asannu"

Duk cikin harcen fullaci suke yin zancen nasu, tafiya Aliyu ya fara yana fadin, " zanje indawo da Husna"

Ficewa yayi yayin da Innawo da Ummi sukacigaba da tattaunawa akan halin kakar Aysha"

Bayan kwana biyu, Aysha ta nufi gidan su Husna kamar yadda ta saba, cikin sallama yayin da Ummi ta amsa sallamar sannan ta mike ta fito tana gyara daurin Dan kwalinta.

Ido ta zubawa Aysha, ganin yadda Ummin Aliyu ta tsareta da ido yasa ta kasa kallonta cikin sauri tai kasa da kanta tare da wasa da fararen yatsunta.

Ke dago idonki ki kalleni nan"

Ahankali ta kalleta kamar yadda tace' sai dai cikin sauri ta sake yin kasa da kanta"

Ke Aysha!!

Cikin faduwan gaba ta sake kallon Ummi akaro na biyu sannan ta sakeyin kasa da kanta"

Kibude kunnen ki dakyau kiji abun da zan gaya miki, daga yau karna sake ganin ki cikin gidan nan, tunda ba gidan ubanki bane, ko an hada da kwandala ta ubanki kafin aka gina gidan

nan??

Ahankali ta girgiza kanta tare da fadin a'a"

Toh maza ki tattara kafafuwan ki kibar gidan nan tunkan na karya wannan kafar taki me kama dana tantabara"

Juyawa tayi idonta akasa, yayin datajiyo muryan Innawo tana fadin, Aysha kidinga zama a gidan ku Husna ma takoma gidan Babanta"

Fita tayi batare datace komai ba, sai dai tana fita kofar gidan hawaye ya zobo mata, tana rungume da littafinta a kirjinta, ajiyan zuciya kawai take, yayin da hawaye ke zobo mata tana sharewa, sosai take shashshekar kuka tana tafe gefen hanya"

**********

Me aka mata take tafe take kuka haka?, Allah yasa ba mutuwa akayi ba, Aliyu ke wannan tunanin alokacin daya hangi Aisha na tahowa tana kuka"

Ganin tsayuwar mota gabanta yasa  tai saurin dagowa ta kalleshi sannan tai kasa da kai tana me share hawaye"

Lebensa taga ya motsa Dan haka ta kalleshi kawai ta sake share hawaye"

Cikin tsawa tare da daga murya ya sake cewa badake nake mgn bane wai, me aka miki??

Fashewa tayi da kuka saboda Kara rudewa datayi, cikin matsanancin kuka tace, Ummi ku ce ta koreni, tace karna kara zuwa gidan"

Jimmmm yayi yana kallonta tsayon lokaci sannan ya dauke kansa tare da fadin, " daura dan kwalin ki"

Cikin sauri ta dauki dankwalin dake wuyanta ta daura akanta"

Umarni ya sake bata akaro na biyu cewa ta share hawayen ta"

Sharewa tayi kamar yadda yace sannan ta dan kalleshi kadan"

Me kikajeyi agidan toh?, taji ya jeho mata tambaya batare daya kalli inda take ba"

Karatu 😭😭

Waigowa yayi ya kalleta nace kibar yi min kuka ko?

Jikina rawa ta fara share hawayen"

Ta gefen ido ya kalleta sanannan yace, baki san kawarki bata gidan ba?

Nasani, mun hado amakaranta ta gaya min"

Jimmm yayi, sannan yace toh me kika je yi gidan??

Wahawayen ta ne suka karo, yayin da suka balle kamar famfo harda majina, duk abun da take Aliyu na kallonta ahankali ya sake cewa ko gurina kikazo nai miki karatu???

Cikin sauri ta daga kanta"

Murmushi yayi kadan, sannan yace, ke baki da Yaya ne??

Kanta ta daga tare dajan majina"

Kannai fah?

Nikadai ce mamana ta haifa"

Wanni irin kallo yai mata na sama da kasa sannan yace toh nawa zaki dinga biyana duk wata.

Dagowa tayi ta kalleshi yadda fuskarsa take daure ya tabbatar mata shine yai mgnr, ni bani da kudi, saidai in dinga baka rabin kudin makaranta na kullum"

Lumshe idon sa yayi tare da tsotson sweet din da baya rabo da bakin sa,  yana fadin shikenan na amince, amman fa ki dinga rufe gashin ki banson ganin gashi sam"

Tam, tace ahankali"

Tada motar yayi yana fadin muje, gaba tayi yana binta da motar ahankali, kusan atare suka isa yayin data bude motar ya fito ya rike hannunta suka shiga gidan"

******

Kai!! kai!! Aliyu saki hannun yariyar nan tabar gidan nan"

Ummi karatu tazo, ya fada yana cigaba da tafiya"

Falon ya zauna sannan ya kalli Aysha yace zauna"

Zamanta yayi daidai da lokacin Ummi ta shigo falon tana fadin, " maza maza kizo kibar gidan nan ko bakijin yaren da nake ne, juya harce tayi daga fillaci zuwa french take fadin yi gidan ku"

Hawaye ta share yayin da Aliyu ya kalli Ummi yace, "haba mana Ummi kibar koranta karatu ne yake kawota ba wani abu ba"

Wani irin kallo Ummi tamai sannan tace waikai baka gudun zuciya ne?, Aliyu duk fa irin maganganun da kakarta take kasan dasu, me zaisa mubarta ta zauna, itafa take karuwa damu bamu ke karuwa da itaba, sannan azo ana gaya mana mgnr banza da wufi.....

Nidai bakomai Ummi, duk surutun da zata yi Babu abun da ya dame ni, Ummi yariyar zaki duba tana son karatu sosai fah"

Wani irin kallo ta masa afusace sannan tace, amakaranta ya cancanta tai karatu ba annan ba, Kuma ma wai meye naka tunda iyayenta basa so??

Zuwa wannan lokacin idon Aliyu ya fara canza launi daga fari kar zuwa jah dan haka ya lumahe ido kawai yana me lasan leben sa na kasa"

Meye naka Ummi ta sake tambaya?

Lebensa ne ya motsa, sarai tagane me yace amman sai tace ka bude baki kamin mgn"

Sumar kansa ya shafa sannan yace cewa nayi yariyar nason karatu.

Kallo tabishi dashi sosai dan haka yai kasa da kansa, ganin haka Ummi ta juya gun Aysha tace ke Kuma bace min dagani wawiyar yariya kawai me zubin mayo, banson naci wlh"

Ficewa Aysha tayi tana share hawaye sosai, bayanta Ummi tabi tana cigaba da gayawa Aysha duk wani abun da yazo bakinta, tanemejin tsananta har cikin ranta"

Aliyu kuwa cikin tsananin baccin rai ya nufi dakinsa ko kallon inda aka aje masa abincin ranar sa bayi ba.

*******

Toh fah, subuhanallahi"

Meya faru Innawo?

Yau waya taba min megida na, Kinga abincinsa narana beciba, gana dare ga Kuma nakarin kumallo Babu wadda yasa hannun sa akai"

Jimmm Ummi tayi sannan tace kada Allah yasa yaci, dan Allah Innawo daga yau karki Kuma bashi abinci, ai ba ubanshi ya kawo mana ba bare yace zai gwada mana taurin kai"

A'a nikam banson rigima, kowa da irin sa ai, Kuma nasan da akwai abun dake damun sa duk yadda akayi jiya kin masa fada"

Babu fadan dana mai Innawo, kema kinsan gaba daya halin Bello ya kwaso, har nema ma yake ya zarta shi"

Kema danaki ai, bari ya dawo naji dalilin kin cin abincin nashi"

********

Misalin 3 na rana Aliyu ya dawo gida, afalo yacin musu kamar kullum yai masu sannu sannan ya wuce su, binsa Ummi tayi da kallo harya kulle sannan ta tabe baki"

Itako Innawo abincin sa ta dauka tabi bayan sa, itama binta da kallo Ummi tayi har taga shiganta dakin Aliyu"

Kusan bayan awa daya ta fito rike da kulan abincin, fita tayi tsakar gidan ta aje kulan sannan ta dawo ta zauna kusa da Ummi tana fadin, " kinsan abin da nake so dake"?

Kai Ummi ta girgiza tare da fadin a'a"

Ko sau nawa Aysha zata shigo gidan nan Babu ruwanki da ita, karki sake koran ta"

Jimmm Ummi tayi cikin ya mutsa fuska tace Innawo biye mishi zaki yi?, yariyar nan macece fa bana miji ba, Kuma iyayenta sun nuna basa so, dole ne??

Ba wannan zaki duba ba, yariyar nason karatu, Kuma guda nawa Aysha take da zasu kasa tsareta agida, mu subarmu da yi masu gadi?, Kuma yariyar nan tana zuwa muna korarta bakin mu zata dinga gani har girmanta, yaro be manta abu, tunda sune basa so, su dakatar da ita da kansu.

Cikin tsananin bacin rai Ummi tace nidai Innawo bakomai, taga bakin nawa, tana shigowa gidan nan wlh tsanarta karuwa yake azuciya, ko Husna da suke kawance tahakura bareshi, meye nashi ne aciki wai, dan Allah Innawo kirabu dashi, ai gaba muke dashi bare yace yafimu hangen nesa.

Mikewa Innawo tayi cikin ya mutsa baki tace' toh me d'a, nafa manta ke kika haifeshi dole yabi Umar nin ki, ke kuma daga sama kika fado, sai kiyi abun da kikaga dama, ficewa tayi yayin da Ummi ta zaro idonta waje tare da mikewa da sauri tai waje, cikin kitchen ta samu Innawo dan haka tabita ciki tana cewa, " Innawo kiyi hakuri naga ranki ya baci, ba haka nake nufi ba, naga su duk yara ne ba......

Katseta Innawo tayi da fadin, ke guda nawa kike???

Lumshe idon Ummi tayi sannan tace shikenan kiyi hakuri toh"

Cigaba Innawo tayi da aikin ta cikin yanayin fushi dan haka Ummi ta sake cewa Innawo nace kiyi hakuri dan Allah, wannan karon ma shiru, dan haka Ummi ta nufita ta amshi tsintsiyar dake hannunta tafara karasa inda Innawo tafara sharewa tana me Satan kallon Innawo dake kokarin shiga falo, ajiyan zuciya Ummi tayi  dan ta tabbatar yanzun Innawo ta hakura"

Sai yamma Aliyu ya fito sannu yai masu kamar yadda ya saba Innawo kadai ta amsa har yakai kofar gida ya dawo, daf da Ummi ya tsaya Ummi nai miki laifi ne??

A'a tafada kai tsaye"

Naga nace muku sannu baki amsa ba"

Bakaji bane na amsa"

Lumshe ido yayi sananna ya sake cewa  to natafi kinji Ummi"

Daga murya tayi da Dan karfi tace adawo lafiya"

Allah yasa yafada sannan ya juya ya fice"

Bayan sati daya

Misalin karfe biyu na rana Innawo ta hango farin hannu yana rike labulen falon, adaga arufe har kusan sau biyar dan haka cikin daga murya tace waye nan?

Ahankali cikin wani irin zazzakar murya tace nice"

Kecewa?

Sakin labulen tayi ahankali tace Aysha ce"

Au Aysha kece kike leke, shigo mana"

Labulen ta daga ta shigo tana share hawayen fuskanta, gaida Innawo tayi sannan ta juya barayin Ummi tace, Ummi ina yini?

Lafiya Ummi tace cikin kawar da kanta tare da kirne fuska"

Innawo ce ta sake cewa Aysha kwana biyu, ya mamaki?

Lafiya lau"

Madallah, Innawo ta fada sannan ta sake cewa ai Kuna haduwa da Husna amakaranta ko?

Kai ta daga tare da fadin, " Innawo Ya Aliyu na nan inason ne zai dubamin wani abu?

Aliyu baya nan Aysha amman nasan ya daf daf da shigowa.

Idonta cike da hawaye tace tam, juyawa tayi tare da fadin sai anjima.

Abakin kofar fita sukaci karo da Aliyu yana kokarin shigowa gidan

Cikin sauri ta kauce ta bashi hanya ya wuce yayin data shiga wasa da yatsun hannunta, ganin yana kokarin wucewa abun sa yasata saurin cewa ina wuni cikin fullacin daya rike bakinta ram

Kallonta yayi yayin data karayin kasa da kanta yace, " lafiya ya gida"

Lafiya lau"

Kallon sama da kasa yai mata sannan yace, " meyasa kwana biyu bakizo ba"?

Kanta akasa yayin data tsananta wasa da hannun ta, kur ya mata tsayon lokaci sannan yaga ta saki hannunta tare da dagawa takai daya tana share hawayen fuskanta, tsayon lokaci ya dauka yana nazartanta zuwa can ya mika hannun sa ya zaro littafinta guda biyu dake tsakankanin kirjinta da cinyar hannunta, fuskarta ya sake kallo har yanzun hawaye ne ke tsiyayowa tana sharewa, dauke idonsa yayi sannan ya bude littafi ahankali ya fara duba shafukan, abun da ya lura dashi tun daga lukacin da tabar zuwa akwai ci baya a yanayin Makin da take samu lokacin da take zuwa bayan ya kare bude shafukan da akwai rubutun ta akai ya rufe littafi sannan yai mata wani irin kallo ya mika mata ta amsa tare da zuba mata rankwashi akanta sannan ya bude daya littafin kamar ba shine yai rankwashin ba.

Hawayenta ne ya karu, yayin da suke zubowa Babu kaukautawa.

Rufe littafin yayi domin shima dai irin dayan ne mika mata yayi ta amsa sannan ya fara takawa da sauri da sauri yana nufar kofar da zata sadashi da falon.

Cikin sauri tabi bayansa cikin kokarin son ta cin masa harsai da ta hada da gudu amman dun da haka kafin tashiga babban falon gidan har ya shige dakin sa.

Hake take sosai lokacin da tabbatar ya shige dakin sa, tsaye tayi tsakiyar falon sai yanzun ta kulla da hararan da Ummi ke zabga mata afakaice, cikin sauri ta dauke kanta ta mayar da hankalin ta kan kofar dakin Aliyu.

Ba jimawa ya fito ya zauna afalon, ahankali Itama Aysha ta zauna Dan nesa dashi akasa, Kamar kullum ya shiga yimata bayani cikin nutsuwa da daukan hankali"

*Gyara adon mace, komai yanason gyara, idan kina dakyau kira da wanka, dan haka mata atashi agyara, akwai kayan gyara lada da kala sai wadda kika zaba domin gigita me gida, sabbabin amare ina da irin naku, yan mata masu shirin shiga daga ciki kuma akwai naku na musamman cikin rahusa mai sauki, ina aikawa kowanni gari, ina da tabbaci akan kayana, idan kika gwada saikin dawo insha Allahu, gamasu bukata su tuntubeni ta wannan no 07014197556*

Ummi dake gefe ma kallo tabi Aliyu dashi saboda yadda yake mata bayani daki daki dole nema mutum ya fahimta sannan daya fara yi mata bayani cikin harcen french yake baya taba sako kowwanni yare, har suka gama karatun Ummi na kallo Kuma tana saurare, murmushi tayi har cikin zuciyarta sanan ta sake dagowa ta kalleshi, tunda ya zauna agorin har yanzun idon sa nakan littafin ko sau daya beyi kuskuren dago idon sa ya kalli wani guri daban ba, gani tayi ya rufe littafin tare da mikewa yana kokarin shiga dakinsa yake fadin shikenan kije gida sai gobe kuma.

Itama Aysha littafinta ta dauka sannan ta mike ta kalli inda Ummi take tace, Ummi sai anjima"

Tsintan kanta tayi da amsa mata, bayan ta wuce ta bita da kallo, me kama da harara"⅝

*********

Ai saidai ki koma inda kika fito tun da ke kince kunnen Kashi gareki.

Mama karatu naje fah"

Wa kika gayawa wa da kika tashi fita??

Mamma kona tambaya ai ba barina kuke yi ba ke da Umma"

Cikin fada Umma tace shine ai aka ce miki ki koma inda kika fito, badai gidan Innawo ba?, ki

koma can ki zauna tunda kince ke sarakan yan naci ne ke"

Mama kiyi hakuri kinji?

Tsawa Umma ta buka mata, bace a gurin wuce kibamu guri marajij mgn kawai.......

Afakaice Aysha ta harari Umma tare da fadin, Umma ba ruwan ki"

Au Babu ruwana ma kike cewa, takalmin dake kamafarta tacire tafara dukan Aysha dashi duk da cewa bawani da karfi take bugawa ba amman sosai Aysha ta hade fuska tare da kallon fuskar mamanta, gani tayi mama ta dauke kanta daga kallon su yayin da Umma kecigaba da fadin, ko tsinken ki karki barmin ki koma gidan Innawo"

Afusace Aysha ta mike ta nufi dakin mama jakar makarantar ta ta goyo tazo ta wuce su ta fice daga gidan"

Hanyar gidan Innawo ta kamo, idonta bushe, saida tazo kofar gidan sannan ta tuna fuskar Ummi, cak ta tsaya, ahankali ta juya ta kalli gidan su, hawaye ne taji suna sakkowa kan idonta, yatsun hannunta ta zubawa ido yayin da take matsa yatsun nata da daya hannun ta tayi tana dagowa tana kallon gidajen guda biyu wadda tasa su a tsakiya.

Hawaye ta share afili tace, bazan iya shiga gidan Innawo ba, haka Kuma bazan koma gidan mu ba, wani shashine na zuciyarta ke tambayanta ina zakije toh?, Kara matsa hannunta tayi sannan tace"

Bansan ko inaba sai makaranta, hawaye ta share sannan ta nemi wani dan tudu ta zauna tare da fadin anan zan zamana gobe inje makaranta......

Fadeela Lamido ✍️

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

*Episode 5- 6*

Zama Aysha tayi agurin tsayon lokaci, wani irin haushi Umma ke bata domin tasan idan babu Umma Mama bazata koreta ba.

Yamma ce tayi sosai kasancewar yanayin damina, tuni hadari ya  hadu sama na shirin zubo da ruwa amman Aysha ko ajikinta, tana zaune jakar makarantar ta goye a bayan ta kananan kaya ne ajikin ta riga da siket, sai hular dake kanta wadda ya matse tarin tudun gashinta a tsakiyar kanta, kasancewar ta farar bafulata cikin bakaken kaya yai matukar fitar da kyanta, Babu abun da take sai raba idon ta tana kallon mutane da motocin dake ta rige rige wucewa dalilin iskan hadarin dake tasowa, bakajin komai sai Karan iska hadari da Karan motoci.

**********

Agoje yake Jan motar domin isa gida akan lokaci, bayan ya faka motar akofar gidan nasu ya sakkowa tare da waiwayowa bayan sa yana kallon yariyar dake zaune nesa dashi.

Cikin zafin nama ya fara takowa domin tabbatar da abun da yake tunani, gabanta ya tsaya tare da fadin, ke!!!

Azubure ta mike tsaye tare da tsallaka kwatar dake gurin batare data sani ba.

Cak ta tsaya, kanta akasa.

Cikin kausasassar murya yace me kike anan gurin??

Umma da Mama suka kore ni"😔

Idonsa akan hadarin dake shirin sakkowa yace me kika musu?

Wai dan nazo kamin karatu"

Lumshe ido yayi sannan yace tun yaushe?

Sai yanzun ta dago ta sata kallon sa tana fadin, tun da nadawo gida"

Kallonta yayi cikin ido yayin da tai saurin yin kasa da kanta, yawu ya hadiye sannan yace, kika kasa basu hakuri Kuma?

Na basu fa amman sun ki"

Hannun sa yasa daya cikin aljihu sannan yace sau nawa kika basu hakurin"

Uku ta fada tare da gyra siket dinta da iska hadarin ke kokarin yayewa"

Ke! Ya sake cewa karo na biyu bayan ta dago idonta ta kalleshi yace, " ki wuce ki koma gida ki basu hakuri"

Kwal kwal tayi da idonta cikin shirin yin kuka, tana nifa na basu hakuri basu hakura ba, ni nan zanyi zamana gobe innaje makaranta sai in zauna acan"

Lumshe idon sa yayin jin ta ambaci makaranta, zuwa can ya bude idon nasa tare da fadin, " ke wai ina wasa dake ne, ki wuce gida ki basu hakuri nagaya miki, kina nufin anan gurin zaki kwana??

Cikin sauri ta daga kanta"

Wani irin kallo yai mata sannan yace shikenan, juyawa yayi ya nufi gida, binsa da kallo Aysha tayi harya kule sannan sannan ta koma ta zauna"

Zuwa can ta hangosa ya Kuma fitowa cikin sauri ya nufa masallaci"

*Gyara adon mace, komai yanason gyara, idan kina dakyau kira da wanka, dan haka mata atashi agyara, akwai kayan gyara lada da kala sai wadda kika zaba domin gigita me gida, sabbabin amare ina da irin naku, yan mata masu shirin shiga daga ciki kuma akwai naku na musamman cikin rahusa mai sauki, ina aikawa kowanni gari, ina da tabbaci akan kayana, idan kika gwada saikin dawo insha Allahu, gamasu bukata su tuntubeni ta wannan no 07014197556*

Zamanta tayi tana kallon duk wani me wucewa, zuwa can aka fara fitowa masallaci dauke idonta tayi dan gudun kar karsu hada ido da Aliyu, muryar sa taji daga dan nesa da ita yana fadin, " kina da taurin kai ko"?

Mikewa tayi ta shiga wasa da hannunta Kamar yadda ta saba kanta akasa tace, " ni a'a fah kaine kace in zauna"

Ni Kuma?, ke baki san gatse ba?

Shiru tayi idonta akan yatsun hannun nata
Domin batama gane me yake nufi da gatsen ba, duk da cewa cikin fulatanci suke mgnr

Kara daure fuskan sa yayi sosai sannan yace, "  ke kin sanin kuwa?, maza kije ki basu

hakuri nasake fotowa naganki anan gurin saina baki kashi wlh, kinji Kuma na rantse"

Tafiya ta fara yayin dayai tsaye agurin yana kallon ta, itako tafe take tana waiwayen sa saida Aliyu ya tabbatar ta isa kofar gidan nasu sannan ya nufi gida, cikin ikon Allah yana shiga gidan ruwan saman daya dade yana hada hadari ya sakko, ruwa ne ya kece sosai.

*********

Dadin yanayin da ake cikin na ruwan sama yasa Aliyu zama cikin su Ummi yaci abinci, Koda ba mgn yake yi ba, Amman yana sauraron hiran Innawo da Ummi saidai in sunyi abun dariya yai murmushi har yagama cin abincin ya mike yana fadin, saida safe"

Amsa masa sukayi sannan suka cigaba da hirar su.

Aliyu kuwa bayan ya shiga daki wanka yayi
Sannan yai shirin bacci ya kwanta tare da rufa cikin bargonsa me shigen laushi, addu'ar bacci ya karanta sannan ya lumshe idonsa yana mejin saukan ruwan saman da aketa zugawa"

Sosai yakejin dadin yanayin idonsa alumshe yanajin saukan ruwan saman daketa kwaranya, hiran Ummi da Innawo ya tuna dan haka yadanyi murmushi tare da gyara kwanciyarsa"

Bacci ne ya dauki sa, yayin da can cikin baccin yakejin hayaniya sama sama, ahankali ya bude idonsa har yanzun ruwan ake zubawa sannan ga hayaniya yanaji wanda be sanin me ake cewa, tashi yayi ya zauna yana me Kara baza kunnen sa, yaye bargon yayi gaba daya ya sauko ya nufi window tare da yaye labulen, Kakar Aysha yagani tare da mahaifiyarta da wasu maza biyu manya sai masifa suke cikin tsakiyar ruwan sama duk sun jike, cikin sauri ya saki labulen tare da nufar kofa, karo sukaci da Innawo cikin yanayin rudu tace kai *Ali* kaga Aisha wai??

***********

JIGON LABARIN

*Aliyu* dane ga Alhaji Bello Kano, shahararren dan kasuwa Kuma masu fada aji, mahaifiyar Aliyu mutuniyar Cemaroon ce, bafulatana, yar asalin kasar Camaroon, sun hadu da Alhaji Bello ne a kasar Camaroon alokacin dayaje domin kasuwanci, Soyayya ta kullo tsakanin su har takaisu ga aure, saidai kafin aurenta da alhaji Bello ta taba aure har da yaranta biyu namiji da mace wadda alokacin ita macen me sunan Ruqayya an auren da ita tana zaune da mijinta a Kano Nigeria, dan haka da Alhaji Bello ya nuna ra'yin sa akanta tai farin ciki domin zata zauna kusa da 'yarta, shiko Alhaji Bello irin mazan nan ne wadda suka jima basuyi aure ba, sai akan Fatima, cikin farin ciki Fatima ta taho aure Nigeria tabaro Babban danta Fahat can CAMAROON gurin mahaifiyarta, Fahat shine yayan Ruqayya, sai dai shi yana da lalurar tabin hankali, sai dai

Allah be kaddara dogon zama tsakanin Fatima da Alhaji Bello ba, domin kuwa tana da cikin Aliyu wata daya suka rabo, dan haka ta tattaro ta dawo CAMAROON anan tayi rainon cikin ta, bayan wata 8 ta Haifi danta katon gaske saidai bashi da hasken Fata kamar na Fatima, mahaifin sa Alhaji Bello yazo ya ganshi, inda yai masa huduba da Aliyu, sannan yayi duk wani abu da yadace uba yayi alokacin da aka haifan masa da, sannan ya koma Nigeria"

Fatima tacigana da rainon Aliyu cikin so da kauna, hakama mahaifiyar ta Innawo tana nuna tsananin soyayyarta wa Aliyu, bayan Aliyu yafara girma suka sanyashi makaranta sosai yake maida hankalin sa kan karatun sa, bayan ya kara girma ne suka kula da wasu dabi'u nashi, yana da son yara kanana, sannan Koda yaushe fuskarsa sake take amman mgnr sa ya kanyita ne ciki ciki kuma bada kowa yake mgn ba sai yaga dama, ta wani bangaren ana iya kiransa miskili, shidin kaifi daya ne, yana sa gabansa ne kawai abun da yasa gaba sannan baya daukan raini, idan ransa yabaci kuwa be iya fushi ba, ahaka Aliyu ya taso cikin kulawan dagin mahaifiyarsa lokaci bayan lokaci mahaifin sa nazuwa ganin sa, sannan akowanni lokaci yana aiko masu da sako babu laifi"

Aliyu yana da kimanin shekara 10 yayar sa Ruqayya ta kawo masu ziyara CAMAROON lokacin data tashi komawa ta nemi da abata Yayanta Fahat ta tafi dashi Nigeria domin neman masa magani, komai sai an masa baya iya yiwa kansa komai, haka kuwa akayi Ruqayya ta tafi da Fahat, yayin da Innawo da Fatima suka maida hankalin su gaba daya akan Aliyu, a yanzun haka Aliyu yana daf da kammala karatun sa na gaba da secondary, Aliyu matashin saurayi ne meji da kansa, wadda bazai wuce shekaru 25 ba, yana da matukar kokari amakaranta yana da tsanin tafta wadda har take son ta wuce misali, Kuma har wannan lokacin Fahat yana gurin kanwarsa Ruqayya kullum cikin nema masa magani take amman har yanzun ba'a dace ba

Kasancewar Fatima Bafulatana ce ita da danginta yasa fullanci ya zauna bakin Aliyu sosai, dan yanzun haka duk wata magana da zasuyi cikin harcen fullaci sukeyi duk da cewa Fatima tanajin hausa kadan kadan hakama Innawo tana gane wasu abubuwan, haka Kuma abangaren makaranta boko anayin amfani ne da french dan haka ya kejin french sosai, saidai Aliyu mutum ne meson jin yaruka da yawa dan haka ya nemi ajin English tun yana secondary School yana hadawa dashi, ayanzun haka Aliyu yana jin yaruka 4 Hausa Fulatanci English French.

Wannan kenan.

Abangaren Aisha kuwa, iyayen Aisha gaba dayan su Mutanen CAMAROON ne uwa da uba, yayin da mahaifiyar Aisha ta kasance Fulani, maifinta Kuma kirista ne, kaddara ta hadasu aure wanda basu jima tare ba, Aisha nada shekara uku suka rabo, kasancewar sa ba musulmi bane tai zafin naman tattaro diyarta ta rike gunta, duk da cewa me kudine sosai Babban ma'akacin gwamnati, Bilkisu wato mahaifiyar Aisha kyakayawace sosai fara tas hakama Aysha ta dauko farin fatan da kyau gurin uwarta, Koda shima mahaifin Aisha fari ne tas, Kuma yana tsananin son Aisha tare da kawo mata ziyara duk lokacin da yaso ganin ta, bata nemi komai ta rasa ba, domin mahaifinta tsaye yake akan karatun ta bashi da wani buri daya wuce yaga Aisha cikin farin ciki"

Haka itama Aisha tana son Daddyn ta sosai da sosai har bata iya banbance wadda tafi so tsakanin sa da Maman ta, tun da ta taso yariya ce meson karatu sosai, fiye da tunanin me karatu, na boko dana bangaren addini, hakama Mamanta da kakarta Umma suna bata kulawa gurin karatun nata, Aisha yariya ce meson wasa da dariya Kuma me jajircewa akan abun da tasa gaba, yanzun haka tana aji daya na secondary School, Aisha yaruka biyu kawai take iyaji, fullanci sai Kuma french wada da dashi ake masu karatu amakarantar boko

*CIGABAN LABARIN*

Lumshe idonsa yayi sannan yace, "eh naganta dazon"

Ka ganta?,🤔 Ina take toh??

Kafin ya bude baki Umminsa ta karaso ta kure sa da ido, inda Innawo ta sake cewa ina jinka"

Innawo nace miki dazon naganta zaune a kofar gida nace mata ta Koma ta koma gida"

Wani irin kallo mahaifiyar tasa ta masa me cike da tuhuma sannan tace bayan Kun gama karatun ina ka kaita?

Ni?

Eh kai fah"

Ummi nifa tasowan hadarin nan da nadawo nasameta awaje ne kawai, Dana mata tambaya tace min Koranta akayi agida sabo da ta zo karatun daker nasata ta koma gida, Kuma banbar gurin ba har saida naga shiganta gida"

Cike da bacin rai Ummi tace zo ka fita kaje ka fito masu da yarsu"

Wani irin kallo Innawo tama Ummi ya nemota a ina?, kinaji yace saida yaga shiganta gida, suje can su nemeta  suna sonta ai basa koreta ba, yar karamar yariya kamar Aisha tun rana basu tashi nemanta ba sai yanzun?, wannan shiri ne kawai"

Innawo ai shima yanzun bashi da mafita fah, tunda an gansu tare"

Yana dashi da karfin ikon Allah"

Juyawa Aliyu yayi ya nufi dakinsa ba jimawa ya fito cikin sauri yana kokarin gyara wuyan rigarsa daya sanyata yanzunan yana me motsa labban sa, tare da nufan kofar da zata sadashi

da tsakargidan nasu"

Zo nan me kake cewa?, Ummi ta tambaya bayan ta tabbatar daya yayi mgn"

Lumshe idonsa yayi sannan yace cewa nayi saina zane ta"

Cikin yanayin dake nuna taji mamaki tace sabo da kaine ka haifeta?

A'a saboda ta fidda ni acikin ruwa Kuma saida nace ta koma gida, kenan kunnenta bamejin mgn bane.....

Toh waye ya aikeka fita cikin ruwan?, Innawo ta jefa masa tambayan bayan ta tsare sa da ido"

Kansa ya dan shafo kadan sannan yayi wuf yashige cikin ruwan saman dake sauka kamar da bakin kwarya"

Koda ya fito kofar gidan yan gidan su Aysha ne duk acikin ruwan saman sai haske haske suke yi tare da surutai wadda bayajin me suke fada saboda Karan ruwan saman da ake kwararawa"

Bebi ta kansu ba ya wuce abun sa, tafiya yake yana duba Aysha duk wani lungu da sako saida ya duba, gaba daya ya jike sharkaf yana tsiyayan ruwa, gaba daya unguwar ya gama zagawa babu Aysha babu alamarta
gashi dare nakara nisa, baban abun da yafi tayar masa da hankali kankantar shekarun ta, ko wani hali take ciki yanzun duk wannan ruwan da ake ina take?, ta fakewa ruwan ko bata fake ba?, jikinsa ya kallah yadda ya jike sharkaf gawani irin iska wanda yakejin tamkar zatai sama dashi, sosai hankalin sa ya kara tashi, ruwa yaki tsayawa tsayon lokaci, gashi  baya tunanin akwai inda be duba ba lungu da sako nacikin unguwar, dan haka yayi tunanin komawa gida watakila zuwa yanzun Aisha ta koma gida"

Zuwa wannan lokacin babu kowa alayin nasu dan haka yaji sanyi cikin ransa yana me tabbacin anganta, sai dai yana daf da shiga gidan ya hangi su Innawo da Ummin sa sunfito daga gidan su Aisha duk sun gama jikewa, kasa hakuri yayi ya karasa yana fadin, " an ganta"?

Inafah, suna nan sun kafe cewa ka fito masu da 'yarsu"

Lumshe ido yayi batare da yace komai ba ya juya ya shiga gida"

Koda Innawo ta shigo babu abun da take kira sai sunayen Allah "

Sosai hankalin Ummi dana Innawo ya tashi, baban burin su ayanzun be wuce ganin Aisha

ba, Innawo tagumi ta zuba lokaci bayan lokaci tana fadin, "munshiga uku"

Fitowan Aliyu cikin kananan kaya tare da katuwar rigar sanyi yasa duk suka dago suka kalleshi, ina zaka?, Ummi ta fada?

Zan dauki mota ne in kara bincikata"

A'a kazauna agida, tunda sun tura kanin Mamanta ya kira police"

Lumshe ido yayi tare da Kara tura hannunsa cikin aljihun rigarsa sanyin dake jikin sa sannan ya fara takowa ahankali, daf da Innawo ya zauna tare da daukan kafarsa daya ya daura kan daya, ahankali ya fito da hannun sa na dama daga cikin aljihun sweet ya shiga barewa sannan ya jefa abakin sa ya shiga tsotsa ahankali"

Ummi ce ta bishi da kallo yadda yake tauna cigam dinsa bakace wani abu na damun sa ba har wani dan girgiza kafarsa yake yi, kwayar idon sa fari karrr gawani farin ruwa kwance acikin sa, kwayar idon kawai kake gani suna juyawa, motsin da Ummi taji a tsakar gidan nasu yasata maida hankalin ta ga kofar falon, mamakin da taji yasata kallon agogo karfe 01:15am.....

Fadeela Lamido ✍️

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

*Episode 5- 6*

Zama Aysha tayi agurin tsayon lokaci, wani irin haushi Umma ke bata domin tasan idan babu Umma Mama bazata koreta ba.

Yamma ce tayi sosai kasancewar yanayin damina, tuni hadari ya hadu sama na shirin zubo da ruwa amman Aysha ko ajikinta, tana zaune jakar makarantar ta goye a bayan ta kananan kaya ne ajikin ta riga da siket, sai hular dake kanta wadda ya matse tarin tudun gashinta a tsakiyar kanta, kasancewar ta farar bafulata cikin bakaken kaya yai matukar fitar da kyanta, Babu abun da take sai raba idon ta tana kallon mutane da motocin dake ta rige rige wucewa dalilin iskan hadarin dake tasowa, bakajin komai sai Karan iska hadari da Karan motoci.

**********

Agoje yake Jan motar domin isa gida akan lokaci, bayan ya faka motar akofar gidan nasu ya sakkowa tare da waiwayowa bayan sa yana kallon yariyar dake zaune nesa dashi.

Cikin zafin nama ya fara takowa domin tabbatar da abun da yake tunani, gabanta ya tsaya tare da fadin, ke!!!

Azubure ta mike tsaye tare da tsallaka kwatar dake gurin batare data sani ba.

Cak ta tsaya, kanta akasa.

Cikin kausasassar murya yace me kike anan gurin??

Umma da Mama suka kore ni"😔

Idonsa akan hadarin dake shirin sakkowa yace me kika musu?

Wai dan nazo kamin karatu"

Lumshe ido yayi sannan yace tun yaushe?

Sai yanzun ta dago ta sata kallon sa tana fadin, tun da nadawo gida"

Kallonta yayi cikin ido yayin da tai saurin yin kasa da kanta, yawu ya hadiye sannan yace, kika kasa basu hakuri Kuma?

Na basu fa amman sun ki"

Hannun sa yasa daya cikin aljihu sannan yace sau nawa kika basu hakurin"

Uku ta fada tare da gyra siket dinta da iska hadarin ke kokarin yayewa"

Ke! Ya sake cewa karo na biyu bayan ta dago idonta ta kalleshi yace, " ki wuce ki koma gida ki basu hakuri"

Kwal kwal tayi da idonta cikin shirin yin kuka, tana nifa na basu hakuri basu hakura ba, ni nan zanyi zamana gobe innaje makaranta sai in zauna acan"

Lumshe idon sa yayin jin ta ambaci makaranta, zuwa can ya bude idon nasa tare da fadin, " ke wai ina wasa dake ne, ki wuce gida ki basu hakuri nagaya miki, kina nufin anan gurin zaki kwana??

Cikin sauri ta daga kanta"

Wani irin kallo yai mata sannan yace shikenan, juyawa yayi ya nufi gida, binsa da kallo Aysha tayi harya kule sannan sannan ta koma ta zauna"

Zuwa can ta hangosa ya Kuma fitowa cikin sauri ya nufa masallaci"

*Gyara adon mace, komai yanason gyara, idan kina dakyau kira da wanka, dan haka mata atashi agyara, akwai kayan gyara lada da kala sai wadda kika zaba domin gigita me gida, sabbabin amare ina da irin naku, yan mata masu shirin shiga daga ciki kuma akwai naku na musamman cikin rahusa mai sauki, ina aikawa kowanni gari, ina da tabbaci akan kayana, idan kika gwada saikin dawo insha Allahu, gamasu bukata su tuntubeni ta wannan no 07014197556*

Zamanta tayi tana kallon duk wani me wucewa, zuwa can aka fara fitowa masallaci dauke idonta tayi dan gudun kar karsu hada ido da Aliyu, muryar sa taji daga dan nesa da ita yana fadin, " kina da taurin kai ko"?

Mikewa tayi ta shiga wasa da hannunta Kamar yadda ta saba kanta akasa tace, " ni a'a fah kaine kace in zauna"

Ni Kuma?, ke baki san gatse ba?

Shiru tayi idonta akan yatsun hannun nata
Domin batama gane me yake nufi da gatsen ba, duk da cewa cikin fulatanci suke mgnr

Kara daure fuskan sa yayi sosai sannan yace, "  ke kin sanin kuwa?, maza kije ki basu hakuri nasake fotowa naganki anan gurin saina baki kashi wlh, kinji Kuma na rantse"

Tafiya ta fara yayin dayai tsaye agurin yana kallon ta, itako tafe take tana waiwayen sa saida Aliyu ya tabbatar ta isa kofar gidan nasu sannan ya nufi gida, cikin ikon Allah yana shiga gidan ruwan saman daya dade yana hada hadari ya sakko, ruwa ne ya kece sosai.

*********

Dadin yanayin da ake cikin na ruwan sama yasa Aliyu zama cikin su Ummi yaci abinci, Koda

ba mgn yake yi ba, Amman yana sauraron hiran Innawo da Ummi saidai in sunyi abun dariya yai murmushi har yagama cin abincin ya mike yana fadin, saida safe"

Amsa masa sukayi sannan suka cigaba da hirar su.

Aliyu kuwa bayan ya shiga daki wanka yayi
Sannan yai shirin bacci ya kwanta tare da rufa cikin bargonsa me shigen laushi, addu'ar bacci ya karanta sannan ya lumshe idonsa yana mejin saukan ruwan saman da aketa zugawa"

Sosai yakejin dadin yanayin idonsa alumshe yanajin saukan ruwan saman daketa kwaranya, hiran Ummi da Innawo ya tuna dan haka yadanyi murmushi tare da gyara kwanciyarsa"

Bacci ne ya dauki sa, yayin da can cikin baccin yakejin hayaniya sama sama, ahankali ya bude idonsa har yanzun ruwan ake zubawa sannan ga hayaniya yanaji wanda be sanin me ake cewa, tashi yayi ya zauna yana me Kara baza kunnen sa, yaye bargon yayi gaba daya ya sauko ya nufi window tare da yaye labulen, Kakar Aysha yagani tare da mahaifiyarta da wasu maza biyu manya sai masifa suke cikin tsakiyar ruwan sama duk sun jike, cikin sauri ya saki labulen tare da nufar kofa, karo sukaci da Innawo cikin yanayin rudu tace kai *Ali* kaga Aisha wai??

***********

JIGON LABARIN

*Aliyu* dane ga Alhaji Bello Kano, shahararren dan kasuwa Kuma masu fada aji, mahaifiyar Aliyu mutuniyar Cemaroon ce, bafulatana, yar asalin kasar Camaroon, sun hadu da Alhaji Bello ne a kasar Camaroon alokacin dayaje domin kasuwanci, Soyayya ta kullo tsakanin su har takaisu ga aure, saidai kafin aurenta da alhaji Bello ta taba aure har da yaranta biyu namiji da mace wadda alokacin ita macen me sunan Ruqayya an auren da ita tana zaune da mijinta a Kano Nigeria, dan haka da Alhaji Bello ya nuna ra'yin sa akanta tai farin ciki domin zata zauna kusa da 'yarta, shiko Alhaji Bello irin mazan nan ne wadda suka jima basuyi aure ba, sai akan Fatima, cikin farin ciki Fatima ta taho aure Nigeria tabaro Babban danta Fahat can CAMAROON gurin mahaifiyarta, Fahat shine yayan Ruqayya, sai dai shi yana da lalurar tabin hankali, sai dai Allah be kaddara dogon zama tsakanin Fatima da Alhaji Bello ba, domin kuwa tana da cikin Aliyu wata daya suka rabo, dan haka ta tattaro ta dawo CAMAROON anan tayi rainon cikin ta, bayan wata 8 ta Haifi danta katon gaske saidai bashi da hasken Fata kamar na Fatima, mahaifin sa Alhaji Bello yazo ya ganshi, inda yai masa huduba da Aliyu, sannan yayi duk wani abu da yadace uba yayi alokacin da aka haifan masa da, sannan ya koma Nigeria"

Fatima tacigana da rainon Aliyu cikin so da kauna, hakama mahaifiyar ta Innawo tana nuna tsananin soyayyarta wa Aliyu, bayan Aliyu yafara girma suka sanyashi makaranta sosai yake maida hankalin sa kan karatun sa, bayan ya kara girma ne suka kula da wasu dabi'u nashi,

yana da son yara kanana, sannan Koda yaushe fuskarsa sake take amman mgnr sa ya kanyita ne ciki ciki kuma bada kowa yake mgn ba sai yaga dama, ta wani bangaren ana iya kiransa miskili, shidin kaifi daya ne, yana sa gabansa ne kawai abun da yasa gaba sannan baya daukan raini, idan ransa yabaci kuwa be iya fushi ba, ahaka Aliyu ya taso cikin kulawan dagin mahaifiyarsa lokaci bayan lokaci mahaifin sa nazuwa ganin sa, sannan akowanni lokaci yana aiko masu da sako babu laifi"

Aliyu yana da kimanin shekara 10 yayar sa Ruqayya ta kawo masu ziyara CAMAROON lokacin data tashi komawa ta nemi da abata Yayanta Fahat ta tafi dashi Nigeria domin neman masa magani, komai sai an masa baya iya yiwa kansa komai, haka kuwa akayi Ruqayya ta tafi da Fahat, yayin da Innawo da Fatima suka maida hankalin su gaba daya akan Aliyu, a yanzun haka Aliyu yana daf da kammala karatun sa na gaba da secondary, Aliyu matashin saurayi ne meji da kansa, wadda bazai wuce shekaru 25 ba, yana da matukar kokari amakaranta yana da tsanin tafta wadda har take son ta wuce misali, Kuma har wannan lokacin Fahat yana gurin kanwarsa Ruqayya kullum cikin nema masa magani take amman har yanzun ba'a dace ba

Kasancewar Fatima Bafulatana ce ita da danginta yasa fullanci ya zauna bakin Aliyu sosai, dan yanzun haka duk wata magana da zasuyi cikin harcen fullaci sukeyi duk da cewa Fatima tanajin hausa kadan kadan hakama Innawo tana gane wasu abubuwan, haka Kuma abangaren makaranta boko anayin amfani ne da french dan haka ya kejin french sosai, saidai Aliyu mutum ne meson jin yaruka da yawa dan haka ya nemi ajin English tun yana secondary School yana hadawa dashi, ayanzun haka Aliyu yana jin yaruka 4 Hausa Fulatanci English French.

Wannan kenan.

Abangaren Aisha kuwa, iyayen Aisha gaba dayan su Mutanen CAMAROON ne uwa da uba, yayin da mahaifiyar Aisha ta kasance Fulani, maifinta Kuma kirista ne, kaddara ta hadasu aure wanda basu jima tare ba, Aisha nada shekara uku suka rabo, kasancewar sa ba musulmi bane tai zafin naman tattaro diyarta ta rike gunta, duk da cewa me kudine sosai Babban ma'akacin gwamnati, Bilkisu wato mahaifiyar Aisha kyakayawace sosai fara tas hakama Aysha ta dauko farin fatan da kyau gurin uwarta, Koda shima mahaifin Aisha fari ne tas, Kuma yana tsananin son Aisha tare da kawo mata ziyara duk lokacin da yaso ganin ta, bata nemi komai ta rasa ba, domin mahaifinta tsaye yake akan karatun ta bashi da wani buri daya wuce yaga Aisha cikin farin ciki"

Haka itama Aisha tana son Daddyn ta sosai da sosai har bata iya banbance wadda tafi so tsakanin sa da Maman ta, tun da ta taso yariya ce meson karatu sosai, fiye da tunanin me karatu, na boko dana bangaren addini, hakama Mamanta da kakarta Umma suna bata kulawa gurin karatun nata, Aisha yariya ce meson wasa da dariya Kuma me jajircewa akan abun da tasa gaba, yanzun haka tana aji daya na secondary School, Aisha yaruka biyu kawai take iyaji, fullanci sai Kuma french wada da dashi ake masu karatu amakarantar boko

*CIGABAN LABARIN*

Lumshe idonsa yayi sannan yace, "eh naganta dazon"

Ka ganta?,🤔 Ina take toh??

Kafin ya bude baki Umminsa ta karaso ta kure sa da ido, inda Innawo ta sake cewa ina jinka"

Innawo nace miki dazon naganta zaune a kofar gida nace mata ta Koma ta koma gida"

Wani irin kallo mahaifiyar tasa ta masa me cike da tuhuma sannan tace bayan Kun gama karatun ina ka kaita?

Ni?

Eh kai fah"

Ummi nifa tasowan hadarin nan da nadawo nasameta awaje ne kawai, Dana mata tambaya tace min Koranta akayi agida sabo da ta zo karatun daker nasata ta koma gida, Kuma banbar gurin ba har saida naga shiganta gida"

Cike da bacin rai Ummi tace zo ka fita kaje ka fito masu da yarsu"

Wani irin kallo Innawo tama Ummi ya nemota a ina?, kinaji yace saida yaga shiganta gida, suje can su nemeta suna sonta ai basa koreta ba, yar karamar yariya kamar Aisha tun rana basu tashi nemanta ba sai yanzun?, wannan shiri ne kawai"

Innawo ai shima yanzun bashi da mafita fah, tunda an gansu tare"

Yana dashi da karfin ikon Allah"

Juyawa Aliyu yayi ya nufi dakinsa ba jimawa ya fito cikin sauri yana kokarin gyara wuyan rigarsa daya sanyata yanzunan yana me motsa labban sa, tare da nufan kofar da zata sadashi da tsakargidan nasu"

Zo nan me kake cewa?, Ummi ta tambaya bayan ta tabbatar daya yayi mgn"

Lumshe idonsa yayi sannan yace cewa nayi saina zane ta"

Cikin yanayin dake nuna taji mamaki tace sabo da kaine ka haifeta?

A'a saboda ta fidda ni acikin ruwa Kuma saida nace ta koma gida, kenan kunnenta bamejin mgn bane.....

Toh waye ya aikeka fita cikin ruwan?, Innawo ta jefa masa tambayan bayan ta tsare sa da ido"

Kansa ya dan shafo kadan sannan yayi wuf yashige cikin ruwan saman dake sauka kamar da bakin kwarya"

Koda ya fito kofar gidan yan gidan su Aysha ne duk acikin ruwan saman sai haske haske suke yi tare da surutai wadda bayajin me suke fada saboda Karan ruwan saman da ake kwararawa"

Bebi ta kansu ba ya wuce abun sa, tafiya yake yana duba Aysha duk wani lungu da sako saida ya duba, gaba daya ya jike sharkaf yana tsiyayan ruwa, gaba daya unguwar ya gama zagawa babu Aysha babu alamarta
gashi dare nakara nisa, baban abun da yafi tayar masa da hankali kankantar shekarun ta, ko wani hali take ciki yanzun duk wannan ruwan da ake ina take?, ta fakewa ruwan ko bata fake ba?, jikinsa ya kallah yadda ya jike sharkaf gawani irin iska wanda yakejin tamkar zatai sama dashi, sosai hankalin sa ya kara tashi, ruwa yaki tsayawa tsayon lokaci, gashi baya tunanin akwai inda be duba ba lungu da sako nacikin unguwar, dan haka yayi tunanin komawa gida watakila zuwa yanzun Aisha ta koma gida"

Zuwa wannan lokacin babu kowa alayin nasu dan haka yaji sanyi cikin ransa yana me tabbacin anganta, sai dai yana daf da shiga gidan ya hangi su Innawo da Ummin sa sunfito daga gidan su Aisha duk sun gama jikewa, kasa hakuri yayi ya karasa yana fadin, " an ganta"?

Inafah, suna nan sun kafe cewa ka fito masu da 'yarsu"

Lumshe ido yayi batare da yace komai ba ya juya ya shiga gida"

Koda Innawo ta shigo babu abun da take kira sai sunayen Allah "

Sosai hankalin Ummi dana Innawo ya tashi, baban burin su ayanzun be wuce ganin Aisha ba, Innawo tagumi ta zuba lokaci bayan lokaci tana fadin, "munshiga uku"

Fitowan Aliyu cikin kananan kaya tare da katuwar rigar sanyi yasa duk suka dago suka kalleshi, ina zaka?, Ummi ta fada?

Zan dauki mota ne in kara bincikata"

A'a kazauna agida, tunda sun tura kanin Mamanta ya kira police"

Lumshe ido yayi tare da Kara tura hannunsa cikin aljihun rigarsa sanyin dake jikin sa sannan ya fara takowa ahankali, daf da Innawo ya zauna tare da daukan kafarsa daya ya daura kan daya, ahankali ya fito da hannun sa na dama daga cikin aljihun sweet ya shiga barewa sannan ya jefa abakin sa ya shiga tsotsa ahankali"

Ummi ce ta bishi da kallo yadda yake tauna cigam dinsa bakace wani abu na damun sa ba har wani dan girgiza kafarsa yake yi, kwayar idon sa fari karrr gawani farin ruwa kwance acikin sa, kwayar idon kawai kake gani suna juyawa, motsin da Ummi taji a tsakar gidan nasu yasata maida hankalin ta ga kofar falon, mamakin da taji yasata kallon agogo karfe 01:15am.....

Fadeela Lamido ✍ it

*⚫BA'KAR FURA⚫*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍

*Episode 7- 8*

Sosai ta maida hankalin ta ga kofar, domin motsin da takeji ya tsananta, gaba dayan su kofar suka maida hankalin su, daga can suka farajin Muryan Umma tana fadin, " innawo!!

Na'am Innawo ta amsa dashi tare da yunkura ta mike cikin azama ta bude kofar"

Kallon kallo sukayi Innawo da Umma bayan tsayon lokaci Umma tace, " ina jikan naki?, ya leko daga waje"

Jinjina kai kawai Innawo tayi sannan ta juya ta kalli inda Aliyu da Ummin sa ke zaune adaidai lokacin da Aliyun ya mike tsaye tare da tahowa, ganin da Innawo tayi yana shirin wuceta ya fice tai saurin rike hannun sa tare da fadin, " babu inda zakaje Aliko"

Hannunta ya zame da sauri yai waje kamar iska yayin da Ummi da Innawo suka rufa masa

baya"

Ahannun police biyu suka sameshi yayin da suke kukarin dannashi motar yana fadin, " ku sakeni basai kun rikeni ba"

Ganin har sunsashi cikin motar Innawo ta fara kuka tare da bawa police din hakuri, motar suka tada batare da sun saurareta ba, motar Innawo ta riki cikin kokarin karsu tafi dashi figar motar da sukayi yayi sanadin faduwan innawo, cikin azama Ummi ta dagata yayin da Innawo ke matsanancin kuka tana Kiran sunan Aliyu.

Kokarin shiga da ita gida Ummi keyi daker tasamu ta Marya da ita gida, dare ya riga da ya tsala bakajin motsin kowa sai kukan karnuka da shishekar kukan Innawo awannan dare wadda bame dadi ba agare su"

Ko ita kanta Ummi karfin hali kawai takeyi amman tana cikin matsanancin damuwa domin tafara tunanin ko ruwan jiya ya tafi da Aisha, idan ko har hakane Lallai Aliyu yana cikin matsala babba"

Wannan tunanin ya haifar da damuwa me tsanani azuciyar Ummin Aliyu, saidai bata son Innawo ta fahimci haka, dan haka ta shiga kwantarwa da Innawo da hankali"

Wannan daren yadda suka rana hakama daren ya zame masu domin cikin su babu wadda ya runtsa, sunayin sallah asuba Innawo tafara Kiran waya tana sanarwa yaranta abun dake faruwa"

Misalin karfe 7 yaran Innawo duk sun hallara yayin da kowa ka ganshi zakaga damuwa kwance aka fuskarsa, tare da tunanin yadda zasu bullowa lamarin"

**********

Kamar yadda gidan su Aliyu suka kwana babu bacci hakama Mama da Umma wannan dare basu iya runtsawa ba, nadama ne cike da zuciyar su tare da dana sani, tun dare yayyen Mama suka iso gidan Kuma har safen suna nan suna neman duk wata hanya da za'abi Aliyu yafitu masu da 'yar Yar su.

Zazaune suke afalon gidan kowa da irin shawaran da yake badawa, adaidai wannan lokacin wayar Mama tafara kara, wayar ta dauka yayin dataji gabanta yayi masifan faduwa ganin sunan Daddyn Aysha akan wayar.

Juyawa tayi ta kalli Yan uwanta tare da fadin, " Daddy Aysha ke kira"

Subuhanallahi Innawo tafada, tare da kara cewa, "ko yaji Ibr ne?"

Nima tunanin da nake kenan.

Umarni Umma ta bata dan haka ta dauki wayar tasa a kunnenta, kasa cewa komai tayi itadai kawai saurare take"

Na sauke Aisha amakaranta yanzun, saidai bata da lafiya, kafin ta iso gida jiya ruwa ya sameta ahanya, nakaita asibiti, magani na gurin ta, dan Allah ki kula sosai ki tabbatar tashanye maganinta, sannan kuma duk lokacin da ta nemi zuwa gidana, akirani awaya zanzo na dauke ta.

Cikin tsananin farin ciki tace insha Allahu bazata sake zuwa ita daya ba"

Tunkan ta sauke waya suka fara godewa Allah, saidai sosai sukayi mamakin yadda Aisha ta iya kwasan jiki ta tafi har inda ubanta yake domin tafiyar ba karama bace"

Hira suka cigaba dayi yayin da wasu ke zagin Aisha tare da kiranta Munafuka, wannan hirar ta dauke su tsayon lokaci wadda basu farga ba saida daya daga cikin police din ya Kira Umma yana sanar da ita zuwan iyayen Aliyu nan take sanar dasu ai sunga Aisha

*********

Allah ya isa tashin hankalin da Umma ta sakamu ciki daren jiya, insha Allahu saitaga sakayya"

Ummi ke fadin haka lokacin da yayyen ta maza suke shigowa tare da Aliyu.

Ai Fatima bama sai kin fada ba, Allah baya bacci ko gyangyadima bayayi, wannan matar bansan me take nema damu ba.

Aliyu Innawo ta kalla wadda taga duk hannun sa ciwo da alama kare duka yayi dasu cikin tsananin tausayin shi tace, " Sannu Aliko, Allah yai maka sakayya"

Kawar dakai yayi tare da cizon lebensa na kasa, kwayar idon sa ta sake kallo sunyi wani irin jah wadda tun haihuwar sa bata taba ganin sunyi ja haka ba ahankali tace, " Allah ya huci zuciyar ka Ali"

Alhaji Umar ne yace, " ai yace baxai yadda ba sai yasa an kamata"

Wa din zaisa akama?🤔

Innawo ta tambaya"

Ita kakar yariya, alhaji Umar ya bata amsa"

A'a Sam bazai yuwu ba Aliko, hakuri dai zakayi, akamata tsofai tsofai da ita, mudai mu kiyaye abun da zai hadomu da su kawai, afusace Aliyu ya mike ya shige dakin sa, yayin da Alhaji Umar yai saurin binsa abaya.

BAYAN SATI 1

Ummi ina son muyi mgn ne.

Toh inajin ka, sosai ta maida hankalin ta kansa"

Ummi akan wannan alkarin da kika min"

Ni?, wanni alkawari kenan?

Kansa yashafa, Ummi har kin manta kinga ni dake inaso ai ban mance ba"

Nan danan Ummi ta kirne fuska, ina jinka?

Ummi kinsa na gaya miki burina har yanzun ina son nazama *SOJA*

Lumshe ido tayi, Aliyu kenan ai ko yanzun kai soja ne, jarumtar ka tana tabbatar min da eh lallai na haifi SOJA , Sojana kanin Fahat da Ruqayya Kuma dan auta na, karake mgnr tayi tana shafa suman kansa.

Cikin sauri yasa hannun sa ya ruko nata dake kansa yana fadin, " Ummi banso, ni ba irin wannan SOJA nake nufi ba  fah, Sojan gaske"

Yadda yake shagwargwabe mata yasata murmushi batare data shirya ba sannan tace, " wato yau ka bude baki kana mgn ko?, Kai har yanzun bazakai hankali bane?

Ni nayi hankali fa Ummi, Ummi lokaci sai tafiya yake yi fah"

Jimmm tayi zuwa can tace toh ka bari zamuyi mgn

Amman Ummi Koda yaushe nayi mgn haka kike cewa fah.

Wannan kalamin nasa yasa ta kalleshi sosai sannan tace, " Aliyu ka cire hankalin ka gurin nan, kayi karatun ka kawai, ni bani da sha'awan wannan aikin, baya bani sha'awa Sam.

Jimmmm yayi kamar ruwa yacishi yana me zubawa Mahaifiyar sa ido, ya gaza furta komai tsayon lokaci sannan ya mike ya koma dakin sa, zuwa yanzun kam ko Ummi bata fada ba

nasan bata so, wannan dalilin yasa koda yaushe take min kauce kauce, duk da cewa beji dadi ba amman beson Ummin sa ta fahimci hakan dole ya riga daurewa tare da masifar son yai mgn da mahaifin sa, gashi ya dade be aiko masa sako ba bare yaba da wasika akai masa, wannan damuwan da yake ciki yau yasa shi tunawa da Aisha, tunda abun nan ya faru be sake sakata a idon sa ba, cikin ransa ya fara tunanin yadda zaiyi domin ya hadu da ita din.

Bayan yadanji dadin zuciyarsa sakkowa yayi yayi wanka sannan ya fito da nufin zuwa kasuwa kamar yadda ya saba, ganin fitowan shi yasa Ummi jin dadi domin ta dauka yana can yana fushi, misalin 6 na yamma ya dawo gida, wanka ya sake sannan ya nufi masallaci, bayan an Kida sallama zaman sa yayi amasallacin har akayi isha'i sannan ya fito.

Ahankali yake tafiya yana tafe yana kallon kofar gidan su Aisha tare dajan carbin dake hannun sa, sai dai har ya iso kofar gidan nasu ko gilmawan mutum be gani ba, dan haka yahau saman motar sa dake kofar gidan su ya zauna.

Tsayon lokaci ya dauka yana mesa ran zaiga ta fito amman shiru, ganin kafa nadaukewa yasa ya nufi gida, washegari ma haka ya kare zaman shi bata fito ba harya koma gida, saida ya kwashe sati yana zaman jiran tsan mani sannan ya hakura, sai dai yasama ransa duk daren dadewa ya hadu da ita saiya hukunta ta akan rashin jin mgn irin nata.

Wata daya me kyau aka share bekoji Ibrn Aisha ba, dan haka yayi tunanin kota koma gidan Babanta gaba daya🤔

Yauma kamar kullum Aliyu ne cikin yar karamar motar daya saba hawa, wadda take mallakin Alhaji Umar, Wanda ya danka masa ita domin samun saukin zirga zirgan makaranta da kuma zuwa rufar sa akasuwa da yake zama kullum bayan ya dawo daga makarantar, kamar kullum kasuwar ya taso misalin 06:00pm, cikin nutsuwa yake Jan motar yana me saurin ya isa gida kan lokaci"

Wacece waccen?, Aliyu ya fada yana me kallon yariyar dake daga masa hannu cikin kokarin tsaida shi"

Alhamdulilahi ya fada lokacin daya tabbatar Aisha ce ahankali ya tsaida motar yayin data karaso jikin motar fuskarta cike da murmushi yayin data ajiye robar dake hannunta ta shiga wasa da hannun nata, fuskanta akan hannun ta yayin da har yanzun take matsanancin murmushi.

Kofar motar ya bude ahankali yayin data dan kauce tana fadin, " ina wuni?

Ahankali yace Yaya?

Kara tsanta wasa da hannunta tayi ga murmushin da yaki barin fuskanta tace, " kullum saina leko ko zanga wucewan ka amman ban taba ganin kaba sai yau"

Ko?

Dagowa tayi ta sata kallon shi sannan tace wlh"

Hakane,  Aliyu ya fada ahankali sannan yace to matso mana"

Motsawa tayi kamar yadda yace, sai dai wannan lokacin gani tayi ya hada rai sosai dan haka ta fara raba ido.

Kina nema na kimin me??

Ni?, ba komai, Aisha tafada tana kwalkwal da ido"

Ina tambayan ki nace kina nemana kimin me?

Babu fah, kaiwai dai"

Ni sa'anki ne?, ni kike tarewa ahanya?

Kaita girgiza da saurinta.

Kinyi na farko kinyi na karshe karki kara"

Ahankali tace tam, juyawa tayi ta dauki dan bukitin tana kokarin wucewa yace zonan"

Ahankali ta sake aje bokitin ta dan taka kadan, gani tayi ya fito daga motar bata wani ankaraba taji ya yarfa mata mari, wanda yasata saurin kallon sa tare da dafe kuncinta, muryansa ce tafara sauka cikin kunnenta kafin radadin marin daya zuba mata"

Ranar danace ki koma gida meyasa baki koma ba??

Ai nace maka korata suka yi fah😭😭

Nikuma me nace miki da kika fadi hakan?

Kace in koma in basu hakuri😭😭😭

Meyasa bakiyi hakan ba??

Kasa mana Aisha tayi illa hawaye dake zubo mata kawai.

Wani marin ya sake kaimata yana fadin mgn nake miki?

Fashewa tayi da kuka sosai tana fadin aina basu tun kafin nafito gidan suka ki"

Ok taurin kaiko?, shine kika kama hanya kikabar unguwan nan, ina kikaje toh?

Ni gidan Daddy na naje"

Yayi kau, ni Kuma kika barni ina yawo acikin ruwan sama??, kinsan a inda nakwana ranar?, Hannun ya mika ya zuzzuba mata rankwashi masu kyau sannan yace wuce kibani waje, ni baruwana dake, karki sake tareni ahanya.

Afusace ta juya tana matsanancin kuka, koda takai gaban bokitinta kafa tasa ta Shure, nan take markadaden kayan miyan ya kware akasa yayin da ta kwasa aguje tai gida"

Kayan miyan ya kalla jawur akasa sannan ya daga kafada dake nuna ko ajikina ya tada motar yabar wajen"

Da matsancin kuka Aisha ta shiga gida tare da kokarin shigewa kurya.

Yau naga abun daya isheni Umma ta fada tare da bin bayan Aisha, ina kayan miyan nawa?

Kuka kawai Aisha takeyi ba bakin mgn dan haka Innawo ta kare mata kallo sama da kasa nan ta kula da kayan miyar daya shafi kafarta, komawa tayi ta zauna saman kujera tana fadin, " Bilkisu saiki fito ta marar da kayan miyan.

Da matsancin mamaki Mama ta fito tana kallon Aisha tana fadin, " ta zubar"?, ganin inda Aisha ke kuka ta matsa gabanta tare da dafa kanta tana duba fuskarta tare da fadin, " Innawo zoki gani ai banda barin kayan miyar harda mari Tasha, wa ya mare ki?

Karasowa Umma tayi wa ya mareki?

Duk bata kulasu ba illah kukan dayaki karewa, tsaye suke akanta, yin duniya taki mgn dan haka duk suka kauce suka bata.

Mama daga gefen Aisha ta zauna tane me binta da ido, cikin ranta take fadin yariyar nan bakaramin maruwa tayi ba.

Kwana biyu Aisha na jinyan fuskanta ko makaranta bata iya zuwa, aran kwana na biyun ne tai shirin zuwa makaranta tsaf sannan ta tsaya gaban Mama Mama nagama zan tafi"

Batare da Mama ta kalletaba tace, " waye ya mareki"?

Wata mata ce bansani ba na bigeta.

Dagowa Mama tayi ta kalli Aisha shine ta taf tafka miki mari haka?, Kinsan har yanzun fuskarki bagama warkewa tayi ba.

Kasa kawai tayi da kanta ganin haka Umma tace tunda tana jin zata iya zuwa makarantar kibar ta taje.

******

Aban garen Aliyu kuwa tunda ya daki Aisha yaji ya huce beko sake tunataba har aka dauki tsayon lokaci, hakama gidan su shiru ya zauna lafiya.

Aliyu ne ya fito daga gida cikin shirin tafiya kasuwa kamar yadda ya saba, motar ya shiga ya zauna tare da sauke ajiyan zuciya, kokarin tada motar yake wani yaro ya taho gaban motar cikin sauri yake fadin gashi inji wata tace in baka"

Wata?, Ya fada sannan ya kalli farar takardan dake hannun sa, ahankali ya karfa yaron ne ya nufi juyawa yayin da Aliyu ya dakatar dashi.

Ahankali ya shiga ware takardan tare da daura idon sa akan rubutun dake kai wadda aka rubutashi da french...

*_Ya Aliyu kai hakuri kaji_*

_Aysha✍️_

Daure fuska yayi lokaci daya kujeran dake gefen sa ya warga takardan ya ja motar sa batare dayacewa yaron komai ba.

******

Haka ce ta sake kasancewa da yamma bayan ya dawo, wannan yaron ne ya sake miko masa takarda, amsa yayi saidai wannan lokacin aljihu ya sanyata dan yasan Aisha ce.

Saidai Koda ya shiga gida bekarabi takan takardan ba har washegari ya shirya ya kuma fita.

Misalin karfe 6 na yamma ya dawo gida wannan karon ma wata takardan yaron ya sake miko masa, sai wannan lokacin ya tuna be bude najiya ba, dan haka ya shiga dakin sa ya duba kayansa najiya, daukowa yayi ya ware takardan.

*_Baxan sake ba, inzo kamin karatu?, ga kudin ka natara maka harma dana ranar da bakamin karatum bama na tara maka, ina son na kawo maka tsoron naka nakeji_*

_*Aysha*_✍

Murmushi ne ya subuce masa batare daya shirya ba, kokarin tuno fuskantama yake ya kasa, sai dai baya manta suffanta, yariya ce yar madaidaiciya fara siririya me fararen yatsu hannun da kafa, kasa tunu ainihin fuskanta yayi dan be fiye kallonta ba, murmushi ya sakeyi bayan ya tuno shekarunta, afili yace, " kina da basira Aysha"

Daya takardan ya bude, itama ga abin da yagani.

_*Ya Aliyu, kai hakuri dan Allah, inzo?*_

_*Aysha_*✍

Murmushi ya sakeyi, sosai yaji yariyar tabashi tausayi, yawacin yara masu irin shekarunta ba sosai suke son karatun har hakaba.

Washegari musamman yaje makarantar su adaidai lokacin da suka tashi, tsaye yayi yana raba ido daker ya iya ganosu ita da Husna, saida ya kira Husna sannan suka ganshi, saidai Husna ce kadai ta taho Aysha ko cak ta tsaya"

Bayan Husna ta karaso ta gaidashi yace kiramin kawarki.

Da hannu ta kira Aysha yayin da Aysha ta fara takowa cikin yanayin sanyin jiki"

Ki karaso mana, Koda kince tsorona kije.

Kasa tayi dakai yayin data shiga wasa da hannunta.

Kifara jin tsoron kakarki kafin kiji tsorona, ni ba abun tsoro bane, saidai bana shakkar matashi bare tsofaffi, ni namiji ne ba mace ba bare kukan jaririyar kyanwa ya firgita ne, nafahimci kina son karatu, ni ashirye nake dana baki gudunmawata aduk lokacin da kike bukata kofa abude take, saidai akwai wani sharadi da zan gaya miki daya tak.

Fadeela Lamido ✍

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

*Gyra page din baya, akwai wani dan kuskure da nayi, akwai guri biyu danasa cewa anyi kiran waya, toh ankara sanar dani cewa ba waya bane, dan sako ne aka aiko musamman domin isar da sakon, toh kowa ya gyara acikin kansa🙏 🥰*

episode 9- 10

Kin yarta?

Kanta kawai ta daga domin duk acikin magarsa nakarshen nan kawai ta fahim ta.

Murmushi yayi kadan sannan yace, idan zakizo karatun ya kasance 03:15 karki zo kafin haka, bayan haka kuma zan kara miki minti biyar ne kawai, dazaran 03:20 ta cika kizauna a ida.

Tam tace kanta akasa, tana wasa da hannun ta"

Kallo ya bita dashi sannan ya juya ya kalli Husna yace, "kinga kawarki nason ai mata karatu amman Kuma tana jin tsorona"

Ya ba tsoron ka take ba.

Haba?, Kina nufin kema haka take lankwasa miki hannu, idonta akasa, jikinta na rawa?

Cikin dariya da kallon yadda Aysha ta nutsu sosai Husna tace a'a kam, ni batamin haka.

Kallon Aysha yayi yace, " ke matso nan"

Ahankali ta matso kamar yadda yace.

Kallo yabita dashi tsayon lokaci, yariya ce kyakyawa sosai, dogon hanci karamin baki ga idanuwa masha Allahu, uwa uba ga farar fata, juyawa yayi ya kalli Husna itama babu laifi tana da kalan nata, amman Aisha ta zarta ta, sai da ya tabbatar da nangaba ne ainihin surarsu zata bayyana dan yanzun kam yara ne kanana ko nono baya tunanin suna dashi.

Murmushi yayi sannan ya mika hannun sa ya riko na Husna, juya yayi ya kalli Aysha yana fadin, kema daura naki.

Cikin idonsa ta kalla sannan ta daura hannunta kanna Husna kamar yadda yace, sannan ya hade ya rike tare da fadin, "ki saki jikin ki kinji ko?, Kema kanwata ce kamar Husna, yadda Husna zatayi mgn dani kema kina da wannan damar, niba wani hallita bane daban, Kuma bantaba jin tsanarki ba har cikin raina, ko ranar da kikaga na dake ki namiki hukunci ne irin wadda zanwa Husna idan tayi ba daidai ba, ahankali ya kejin hannunta na rage rawan da yake zubawa ada, dan haka yacigaba da cewa, " idan Kuna da wata damuwa zaku iya gaya min in baku shawara, ni yayan ku ne kuma Aminin sirrin ku"

Cikin jin dadi tare da gamsuwa suka amsa gaba daya.

Ahankali ya saki hannun su suna murmushi kamar yadda shima yakeyi, yana binsu da kallo yace, " amman fa ina duka idan mutum yayi ba daidai ba, ko ku baku son duka?

Dariyq Husna tayi, ya Aliyu ai kowa yayan shi namai fada, amman kasan me?

A'a

Aysha na tsoron tsawarka sosai, tace har hantan cikinta kadawa yake yi"

Murmushi yayi cikin sauri ya bude motarsa ya shiga ya zauna yana fadin, "bana sanin lokacin da nake yin ta, yanzun dai ke Aysha bani kudina in wuce"

Sauko da Jakarta tayi ta bude wani kefe ta kwaso kudi cike da hannunta ta mikawa Aliyu

Hannu biyu yasa ya karba, yana lumshe ido tare da fadin, " lallai na bude kasuwanci, anya kuwa bazan daina zuwa kasuwa ba?

Sunkuyar da kanta tayi itako Husna cikin rashin fahimta tace, " ya Aliko kudin meyene wannan?

Ba ruwanki, yanzun dai kuje gida saina dawo.

Haka Husnah ta tsuke bakinta bayan Aliyu ya wuce Husna ta kalli Aysha tace, " aina gaya miki yayanmu yana da kirki sosai, baya da matsala , amman dai yanzun kinbarjin tsoron sa ko?

Naji sauki sosai Husna akan yadda nakejin tsoron sa, amman fa kina ganin kuwa wata rana bazai sake dukana ba?

Idan kinyi laifi ko anjima ne dukan ki zaiyi mana, toh ke laifin zaki kara?, nifa sau daya ya taba marina tundaga lokacin ban Kara bari ya dakan ba.

*****

Aliyu zaune saman motarsa harabar makarantar su, Sweet ne abakin sa kamar yadda ya saba Kuma ya zamar masa jiki, maza ne guda biyu suka tunkaro shi yayin da suketa dariya cikin yanayin dake nuna suna cikin nishadi.

Koda suka karaso tsalle sukayi suka hau saman motar yayin da Aliyu yace daga ina haka tun dazon nake raba ido.

Munje shakatawa, kaiko kana nan kana fama da sweet, malam kaje kasha sweet din da kwanyarka zatasan kasha, jikin ka da jijiyoyin jikin ka zasu shaida, hankalin ka ya kwanta, nutsuwa da shigeka, amman ka tsaya nan kana wahalar da harcen ka.

Wanni irin sweet ne wannan?, Aliyu ya fada yana kallon su.

Hmmm kanayi Kamar bakasan komai ba, kawai wasu yara mukaje muka lallatse, yanzun haka jina nake kamar sabon haihuwa, na taba, nasha, na runguma, sannan na tsotsi breast iya son raina, ina kaucewa ana turo min.

Dayan ne yace, " shige kawai, sai najika kawai kana gurnani.

Kaka laifina?, bakaga yadda yariyar ke Kara makale min bane, juyawa yayi ya kalli Aliyu abokina ya kamata ace ka shiga wannan yanayin, wlh wata sabowar duniya zaka jika cikinta, ina tabbatar maka daka lokacin bazaka sake sanya ba.............

It's haram, Aliyu ya fada, duk juyowa sukayi suna kallon shi, yayin da yaci gaba da cewa, " Annabin Allah cewa yayi, daka taba jikin matar daba takaba, gara ama dinki akanka da kusa a duniya daka hadu da Allah akan wannan laifin.

Yayi alaramma, amman dai kasan ba aure muke dashi ba ko?, wannan karatun naka bashi akan mu"

Hmmmm, Sani Allah ba'a mishi dibara, ka sani kabar take sani.

Kana nufin haka zaka zauna har kayi sure?, Ko sweet bazakasha ba?

Indai irin nakune baxan shaba insha Allahu, asalima ba wannan tunanin akaina.

Sani ne ya kalli daya abokin nasu yace Suraj kanajin shi"

Rabi dashi dadin abun dai munsan dalilin tsotsan sweet din.

Tsaki Aliyu yaja sanna ya sauko daga saman motar ya shiga, ganin yana shirin figar motar suka sauka aguje suna dariya tare da daga mishi hannu.

****

Ummi Baffah har yanzun be min aike ba, Allah yasa lafiya betaba jimawa haka ba.

Aliyu, meyasa ne kake damun kanka, akwai abun da kamema karasa ne?

A'a Ummi, ina son ne kawai nabada sako akai mai.

Jimmm Ummi tayi  cikin zurfin tunani zuwa can tace, " to ko intanazar maka kudine kaje kuyi mgn baki da baki, kafadaa mishi abun da kake so idan ya amince saikai zaman ka gurin shi"

Dariya yayi har ya fitar da sauti, sannan ya fada kan cinyarta ya kwanta yana fadin, Ummi ni ina kusa dake, ai bazan iya zama kasar da banbu ke acikin sa ba.

Hmmmm, ai kafi son Baban ka.

A'a Ummi, Sam ba haka bane ina sonku gaba daya sannan kuma dake nasaba, waccen karon danaje har zazzbi naitayi fa sati biyu kawai sabo da babu ke.

Murmushi tayi har cikin ranta taji sanyi, dan haka ta shiga shafa sumar kansa tare da leka fuskarsa tana fadin, " toh yanzun sati biyu kayi masassara Yaya kenan idan kayi aure?, karfa daga aure yariya taga kahau massasra intace yayane kace Ummi na.

Dariya yayi sosai irin wadda ya jima biyita ba, Ummi ma dariya tayi yayin da Aliyu ya tashi ya zauma tare da sunbatan Ummin sa yace, " kinsan ko Bantabayin tunanin nan ba, Ummi"

To gara ka fara, don wata rana dole zakayi aure, kar yar mutane taga tabara, Koda yake ai itama tasan Auta ta aura,

Cikin murmushi yace hakane Ummi, amman idan kuma ya kasan ce itama auta ce fah?🤔

Fashewa da dariya Ummi tayi da shikenan tabara ta auko.

Cikin dariya Aliyu ya mike ai bawata damuwa Ummi sai mu zauna anan kawai anan kicigaba da kula damu.

Hirar me ake?, Innawo take fadi lokacin data daga labulen dakin.

A'a wai Inna tunanin kara aure ne"

Murmushi Innawo tayi ai ya kamata Aliko, yara kamarka ma indai da lafiyan su auren su suke ai"

Fita yake kokarin yi, yau fuskanr sa cike take da fara'a Innawo tace zo mana muyi mgn ka samu yariyar ne?

Dawowa yayi yasa bakin sa a Kunnen Innawo, mgn ya mata sannan ya juya da sauri.

Kallon mamaki Innawo tabi Aliyu dashi tare da sakin baki sannan tace, Ashe ko zaka tsofe, Allah ya taimakeka ya baka nasara, ni ina farin ciki da hakan, amman sai inda matar.

Ficewa yayi yana dariya, Ummi ma binsa da kallo tayi bayan ya fice tace, " Innawo me yace miki"?

A'a Babu ruwanki wannan mgnr mu ce, inace yanzun kuka gama naku?

Dole Ummi tai shiru saidai har cikin ranta take son jin abun da yagawa Innawo.

******

Ummi da Innawo zaune afalon su, yayin Aliyu ke zaune gafen su, abinci ya gamaci sannan ya tashi ya nufi dakin sa, kai tsaye wata kofa ya nufa wadda zata sadashi da tsakar gida, tajima rufe, bude kofar yayi ahankali ya billa tsakar gidan tare da kallon agogo, 03:17 ya gani, dago kansa yayi da nufin dakon jiran ta, ido biyu sukayi tana sako kafarta cikin gidan, cak ya tsaya ta shigo sannan da hannu yai mata nuni da kofar dakin.

Kofar ta nufa da tarin mamaki akan fuskarta, domin bata taba sanin da kofa agurin ba, wani irin kamshi ne ya daki hancinta bayan ta shiga cikin dakin, komai tsaf agyara babu alamar kazanta.

Katuwar katifa ce akasa daga gefenta akwai kujerar zaman mutum daya.

Sosai takebin dakin da kallon komai burgeta yake yi, rasa inda zata zauna tayi dan haka ta nemi kasa ta zauna.

Zamanta yayi daidai da shigowan Aliyu ahankali ya maida kofar ya rufe sannan ya taka ahankali ya isa bakin katifar ya zauna tare da nuna mata kujerar yana fadin tashi ki koma can"

Nan ma yayi Ya Aliyu"

Jimmmm yayi tsayon lokaci zuwa can ya matsa daf da kujerar sannan ya sake cewa dawo nan Aysha.

Babu musu ta mike wannan lokacin, zama tayi yayin daya amsan littafin ya bude ya duba sannan ya daura akan cinyar kafarta ya shiga yi mata bayani"

Sunyi nisa sosai da karatun sannan taji yace, " ina kikace masu zaki agida?"

Islamiyya.

Lumshe ido yayi da wanni lokacin kika  zuwa islamiyyar?

Karfe uku da rabi nake zuwa"

Agogon hannun sa ya kallah hudu saura ya gani, kallonta yayi yanzun 4 saura fah"

Ahankali tace idan 4 din yayi sainaje ko?

Tsintan kansa yayi da daga mata kai sannan yace, " idan kika fita wannan kakar taki ta ganki fah?

Duk da cewa ta tsorata a zuciyarta amman sai tace, sai in labe harsai ta wuce in fita.

Dariya yayi kadan, sannan yace, " ashe kina da wayau, toh yanzun ki tashi kije makaranta nima sallah zanyi inje kasuwa"

Tam tace tare da mikewa har takai bakin kofar yaga tana waigowa dan haka yace zonan.

Dawowa tayi ta tsaya yayin data kurawa wani hoto dake bangon dakin ido.

Me kike kallo?

Dawo da hankalinta tayi garei tare da nuna hoton wannan naga kunyi kama dashi sosai.........

Babanane, mahaifina kenan.

Kunyi kama sosai, to wadannan fah?

Waigawa Alitu yayi ya kalli inda ta numa, pic din Fahat ne da Ruqayya dan haka ya juyo yana fadin, wannan yayyai nane

Dama kana da yayyai?

Eh Amman basa akasarnan, Aunty Ruqayya tana aure a Nigeria ya Fahat ma yana can.

Ya Allah, jibesu farare, kaiko baki.

Runtse ido yayi domin har cikin ransa yaji kalamin ta, saida zuciyarsa ta motsa, cikin son basarwa karta Kara firgicewa dashi yace, " eh naji ni ubana dauko, ba yanzun kika gama cewa muyi kama ba?

Itama cikin son gyara zancenta tace, ai fari kawai suka fika shima farin kadan ne.

Kawar dakai yayi acikin zuciyarta yace wai itana nan me wayau, afili kuwa cewa yayi, " ai nasani kon ke da kadan kika darani haske.

Tun kan ya rufe baki dariya ya subuce mata cikin sauri tasa hannun ta ta toshe bakinta, sai dai duk da haka dariya neman kwace mata take yi.

Ganin haka ya dauke kanshi can gefe kokarin fita take tana dafe da bakinta yace ke dawo.

Dawowa tayi yayin data bar dariyar nan danan ganin inda ya daure fuskan sa.

Ahankali ya mike ya isa gabanta madubi, tsaye yayi yana kallon kansa tsayon lokaci sannan ya dauki kum ya fara taje sajen sa duk suka mike tsaye sannan ya mufi kansa nan ma tajewa yayi daga bisani ya maida Kum din tare da zuba hannun sa duk biyun cikin aljihun wandon ta tare da fadin matso kusa.

Tahowa tayi ahankali ta jero dashi, su biyu ya hanga cikin madubin dan haka yai saurin lumshi idon sa, ya jima be bude ba tsayon lokaci ya bude idon sa ransa a hade, Aysha kuwa banda kallon madubin babu abun da take, sosai dariya keson balle mata sai dai tana tare ta domin bastaan wani irin hukunci zai mataba idan tayi dariyar bakin sa.

Aliyu kuwa kallon su yake cikin ransa yana fadin, bantaba ganin bakina ba sai yau, ai wannan kwatan kwacin duhune da haske🕳️⚪, kallonta yayi can kasa dashi take, saboda kankantar ta, cikin kin yadda da abun da idon sa ke gane masa tare da tsare gida sosai yace, " ina jin ki akwai abun da zaki nuna mun ne?

Dariyar da take boyewace ta subuce mata, dariya tayi sosai har hakoranta suka bayyana, kallo yabita dashi yayin da ta dake take fadin, " Babu Ya Aliyu da kadan nafika fari.

Lumshe ido yayi da dariyar wayon ta, yake kan lefen sa.

Aisha ko zuwa wannan lokacin dariya ce ta kwace mata wadda ta rasa ta yadda zata tsaidata"

Dariyarta yasashi bude ido, murmushi ne ya subuce masa domin kuwa yasan karfin halin sa takewa dariya, duk da cewa ta rufe bakinta da hijjabinta be hanashi gane dariya take ba, sosai ya tsareta da ido tsayon lokaci, Sallan mangariban da ake kwalawa ne ya fargan dasu azabure Aliyu ya kalli agogo sannan ya dago kansa ya kalleta adaidai lokacin da Aysha ke kallon kofar tana fadin"

Zan wuce ya Aliyu"

Ahankali ya taka ya isa bakin kofar ya leka sannan ya dawo yana fadin, " Kash,😬 Ummi tana tsakar gida fah.

*⚫BA'KAR FURA⚫*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

*episode 11- 12*

Zare ido Aysha tayi yayin data koma da baya ta zauna, hawaye ya gani shar yana zobo mata dan haka ya isa bakin gado ya zauna yana binta  da kallo, yayin da kunnen sa suke tsakar gida.

Sosai hawaye ke zubo mata, dan haka abun ya shiga bawa Aliyu mamaki, kasa yayi da murya yace matsoraciya kawai, kinsan kinajin tsoro meya kawoki?

Ahankali tai mgn dan haka ya ce mene?

Akaine kace min bakajin tsoro, yanzun Kuma kace Ummi na tsakar gida"

Kawar da kansa yayi yai murmushi sannan ya juya ya kalleta, kenan nine matsoracin sabo da ban fitar dake ba?

Tana Satan kallon idon shi tace a'a.

Toni kibar min kuka.

An fara kiran Sallah, nasan Mama zane ni zata yi.

Kawar dakai yayi sannan yace, "kiyi hakuri Ummi ta shiga daki, kinsan yanzun idan ta ganki fada zatayi, zaki zama baki da damar nan wadda kika sameta ayau, idan kin amince kinbar zuwa daga yau to kizo ki wuce, nayi hakane sabo da tsaro badan tsoro ba.

Ahankali ta fara share hawayen ta saidai duk da haka fuskanta akwai tarin damuwa.

Mikewa yayi ya sake lekawa har yanzun Ummi na nan zaune bamata da niyar tashi Dan haka ya dawo cikin dakin yana kallon Aysha tare da fadin, " inje inyi sallah in dawo?"

Cikin sauri ta girgiza kanta alamar a'a

Kallon ta yayi sannan yace lallai kuwa, kenan yau bazan samu jam'i ba?, sabo dake?, tsaki yaja kadan sannan ya nufa toilet din dake cikin dakin, alwala yayi ya fito yana ware hannun rigarsa, abakin kofar ya hangeta, dan zaro ido yayi sannan ya tsaya yana tunanin hanyar da zai billowa al'amarin.

Window dake dakin ta baya ya kalla sannan ya fara takawa ahankali ya isa window, labulen ya yaye sannan ya leka, juyowa yayi ya kalleta sosai sannan yace, kwaso takalmin ki mugani ko zaki iya fita tanan.

Cikin sauri ta kwasa takalmin ta ta isa gareshi, daukanta yayi cak ya tura ta, cikin ikon Allah ta dire tsaf tare da sauke ajiyan zuciya, aguje ta fice agidan, shiko Aliyu murmushi.

Juyowa yayi ya nufi masallaci yayin da ya wuce Ummi tana sallah a tsakar gidan.

*****

Daga ina kike?, Ina kika tsaya har aka Kira sallah?

Jakar makarantarta ta aje tare da yaye rigar jikinta tana nunawa Mama bayanta, Mama yau duka mukaci, da cewa ma akayi amakaranta zamu kwana, bayana duk ya kunbura.

Yar dariya Mama tayi, radadine ya rudaki Amman bayanki be kunbura ba, saki rigarki.

Muryan Umma sukaji tana fadin, ta dawo ne ne gantalallar?

Eh Umma gata ta dawo.

Gidan ubanwa ta tsaya?

Mamace ta sanar da ita duk yadda akayi yayin da Umma tace yayi kyau ai, yanzun haka surutu sukai, gara da aka zane kun ai.

Mikewa Aysha tayi tana fadin, " su Umma anji gulma"

Wanni itin kallo Mama taiwa Aysha yayin da Aysha taki kallon ta, Muryan Umma sukaji tace ga magulmaciya nan agaban ki"

Jimmmm Aysha tayi tsayon lokaci yayin da Mama tace tashi kije kiyi sallah ki dauki abincin ki.

Mikewa Aisha tayi bayan tayo alwala tana kokarin maida dan kwalin ta taga wucewan Umma kitchen bayan ta tabi da kallo sannan tace, " Umma dazon naga me kama dake a hanya"

Tukunyan miyar Umma ta dauko sannan ta fito tana fadin, " haba"?

Allah kuwan, Aysha ta fada sannan ta dauki hijjabinta ta zura tare da sake cewa, " Umma baki tambayen me kama dake din ba"

Toh inajin ki gaya min waye ne me kama dani din?

Birii.

Cikin sauri Umma ta sauke tukunyan miyan tare da kallon Ayaha data kambara sallah, Mama ma kallon Ayaha tayi tare da fadin, lallai baki da mutunci.

A'a barni da Ita, ai nima ba kanwar lasa bace, kallon Ayaha tayi wanda zuwa yanzun tayi ruku'u tace, mancewa kikai ai biri namiji ne, wannan mutumin na wancen garin shine katon biri, dashi sukafi kama, ficewa tayi adakin ta nufi tsakar gida, inda mama keta dariya tana fadin Aikuwa Umma kinyi maganin rashin kunya.

Ai kibarni da ita.

Zuwa can Aysha ta fito hannunta dauke da kofin da fura me sanyi aciki, Mamace ta kalleta sannan tace kizo kidauki abincin ki.

Banaci, furar nan ta ishe ni.

Mama batabi ta kanta ba ta jawo abincin dake gabanta, yayin da Aysha ta koma daki, Umma ce ta zauna kusa da Mama domin cin abincin amman sai ganin Mama tayi tana ya mutsa fuska.

Yaya akayi?, Umma ta tambaya

Umma miyan nan gishiri yayi yawa.

Hannu Umma tasa cikin miyar ta dandana tare da kallon mama tace, " wlh miyata lafiya kalau take, Indo ce ta takara min shi.

Batanan akayi miyan ai Umma, kila dai hannun ki ne ya subuce.

Saifa kiyi, Aysha ce ta kara shi, aina zagi ubanta, ta zuba min gishirin ne dan karnaci, toh sainaci ko inaci ina rufe ido ne.

Aikuwa indai hakane sai mata duka wl....

Kashhh, karkice mata komai, barta kawai, muci abincin mu bamuma san tayi ba kawai.

******

Yau tunda ya tashi dariyar Aysha ta jiya ce ke fado masa, wadda aduk lokacin daya tuno saiya murmusa, sannan yana yawan tuno yadda hasken ta ya dannen dan hasken da yake dashi nesa ba kusa ba, afili yayi dari tare da fadin dole kiyi dariya Aysha kinga dan baki me karfin hali, kallon fatarsa yayi sannan yace kai ina, niba baki bane, kawai dai hasken tane yai yawa har yana kashe ido.

Irin wannan tunanin baya awa daya batare daya fado masa ba, dan hakan yake yawan murmushi musamman idan ya tuno irin amsan da take bashi wadda yafi kama da aje ahaka din.

Aliko yau murmushin me kake ne?

Innawo wanine yabani dariya.

A lallai kuwa yana da abin dariya, yau bazaka kasuwar bane?

Zani amman sai 4 yanzun zuwa zanyi in kwanta.

Mikewa tayi ta nufi daki yayin da Aliyu ma ya mike ya nufi nasa dakin, cikin ransa yake fadin kila yau bazatazo ba, dan naga jiya ta tsorata.

Kwanciya yayi yana jiran lokacin daya gindaya mata na zuwan, yayi yaji ana kwankwasa window sa ahankali.

Mikewa yayi ya isa window ahankali ya bude, Aysha ce tsaye cikin kayan islamiyyarta riga da wando da hijjabinta daidai guiwa, jakar makarantar ta rataye agefenta yayin data bude madaidaicin bakinta tace, " ina yini"

Lumshe ido yayi batare daya amsa ba, juyawa yayi ya bude kofar data shigo jiya ganin haka tai saurin zagayawa ta shigo"

Rufe kofar yayi sannan ya dawo ya rufo window tare da dawowa wajen zaman shi ya zauna, itama Aysha kujeran jiya ta zauna tana kokarin fito da littafin ta.

Aliyu kuwa kur yamata da ido yana me kare mata kallo tsayon lokaci.

Kallon da yake mata yasa duk taji ta tsargu, rasa inda zatayi tayi tayi, tun tana kawar dakai harta fara buga kafarta akasa, tana dan sheshshekar kuka?

Lumshe idon sa yayi tare da fadin, "Menene"?

Kai ne.

Idon shi lumshe yace me ya faru?

Ya Aliyu kallo na fa kake?

Neman ki nake, hasken ki ke kashe min ido na.

Kyalkyalewa tayi da dariya, tare da fadin gani nan fah.

Daidai ina?

Dariya ta sake sawa, yayin da hakan ke kara sashi nishadi.

Hannunta ta daga tana yawo dashi saitin fuskarta tana fadin, gani nan fa👐

Kara ware idon sa yayi nadaiga wasu TAURARI guda 10 suna yawo, tare da wani haske wal wal.

Dariya ta Kara sawa wadda har shima saida yadan murmusa.

Sosai yakejin wani nishadi na shigarsa hakama Aysha mantawa tayi da komai zuwa wannan

lokacin data kalli fuskar Aliyu take yin dariya domin ba karamin dariya yake sata ba.

Muryan sa taji yace nidai tunda ba ganin ki nake ba bani littafi kawai karki hanani zuwa kasuwa kamar jiya.

Littafin tabashi, har suka gama acewarsa be ganinta, haka ya bude bata kofar ta fita shima ya fita.

Hakace ta cigaba da kansancewa har tsayon wata Uku, aduk ranakun islamiyya saita fara shiga gidan su Innawo sannan ta wuce makaranta, wata rana ta fita ta kofa wata wata rana kuwa saidai ya sakata ta window, tsayon wannan lokacin Babu wadda ya taba sani.

Zuwa wannan lokacin shakuwa me karfi ta shiga tsanin Aysha da Aliyu har yakai ranar da Babu makarantar suna kewan juna tare da kosawa suka junan su.

Ayanzun Aysha tasan wasu daga cikin halayen Aliyu, sosai take ganin kirkin sa, haka shima Aliyu ya fahimci Aysha dakyau, akoda yaushe yana yaba kwazonta tare da son karatu nutsuwa da kunya.

****

Yauma kamar kullum Aysha ce zaune ita da Aliyu, littafin ta kan cinyar sa, kokarin fahimtar da ita yake, duk da cewa zuwa yanzun idan an bata aiki amakarantar tana jaraba yi da kanta, Koda za'ayi mata gyara yana zamuwa bame yawa banr, sosai take dauke duk wani abu da zai koya mata, rufe littafin yayi bayan sun gama ya mika mata sannan yace toh bani kudina.

Wani littafi ta bude cikin Jakarta ta dauko masa kudin ta mika masa.

Amsawa yayi sannan ya daga katifarsa ya tura, juyo yayi adaidai lokacin da Aysha ke mika masa sweet"

Murmushi yayi sannan yace, " au har da kari?, to bare min"

Bare masa tayi ta mika masa, yayin daya tura mata fuskarsa yana fadin saka min.

Saka masa tayi kamar yadda yace, idon sa lumhe yace, Kai, bantaba shan sweet me dadin wannan ba.

Cikin yar dariya tace , "Kai, Ya Aliyu duk sweet din da kake Sha?"

Ummm wannan yafi dadi.

Yauwa Ya Aliyu wai meyasa kake saka kudin ka kasan katifa?

Dauke idonsa yayi daga kallonta ina ruwan ki?

Dan Allah"

Toh tarawa nake in sunyi yawa inje makka"

Kaiii!! dariya tayi, ya Aliyu har makka ma?🤔, bama katafi Nigeria ba gurin Baffah?

*Kar me karatu ya manta, duk mgnr da Aliyu yake yi da Aysha sunayin ta ne cikin harcen fullaci, idan karatu ne kuwa da harcen french domin Aysha batajin hausa, yare nan biyu kawai take iyaji, hakama iyayen Aysha, gidan Innawo ne kawai sukejin hausa kadan kadan.*

Nace meki kudin zuwa Nigeria nake nema?, wannan kudin aiki nawa zasu baki mamaki, inason nayi wani abu me daraja dashi sabo da sun fito daga hannun 'kanwata, kawata Kuma aminayar sirri na.

Murmushi Aysha tayi me sanyi har cikin ranta take kallon fuskan Aliyu dake kawace da murmushi, cikin yanayin jin kunya take kallon shi dazaran taga kamar baya kallon inda take"

Shikuwa Aliyu daya kulla tana kallon sa yake fara wasa da girarsa tare da gashin idon sa, wadda hakan kesa Aysha murmushi, shima Aliyu dayaga tana murmushi yake jin zuciyarsa wasai, suna cikin wannan yanayin suka tsinkayi bugun kofar dakin ta cikin falon, azabure suka kalli kofar gaba dayan su"

Kai Aliko!!!!

Muryan Innawo yaji dan haka dan haka ya nunawa Aysha bayan kofar da Innawo ke bugawa.

Kusan atare suka isa gurin, yayin da Aliyu ke amsawa tare da bude kofar sukayi ido biyu da Innawo"

Kallon sa tayi sama da kasa sannan tace, " Kai dawa a ciki ?

Lumshe idon sa yayi, nidawa kuwa Innawo?, ni daya, lafiya?

A'a daman yariyar nan Indo ce ake nema.

Wacece haka?

A'a jeka abun ka, juyawa Innawo tayi batare da ta jira me zaice ba.

Rufe kofar Aliyu yayi sannan ya dawo dakin yana rike da kugun sa da hannun sa duk biyun

yake kallon Ayaha tare da fadin, " wani yaga shigowan ki nan ne?"

Cikin samyin jiki tace a'a.

Bakin gadon ya dawo ya zauna yana me tuna irin kallon da Innawo tamai, be dawo daga wannan tunanin ba yaji ana buga kofar dakin ta tsakar gida.

Da tsananin mamaki ya juya ya kalli kofar, domin babu wadda yasan cewa yana bude kofar a yanzun sai Aysha Kuma gata aciki suna tare.......

Fadeela Lamido ✍️

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

*Episode 13to 14*

Mikewa Aliyu yayi, mamaki cike da fuskar shi, sai dai ya kasa zuwa gun kofar, yayin da yayi da yai tsaye hannun sa cikin aljihun sa.

Aysha kuwa tuni ta kara gigicewa tana shirin fara kuka.

Kofar kuwa kara tsananta bugunta ake yi, dan haka yace waye?

Nice, muryan Innawo yaji cikin daga murya
Dan haka ya saki ajiyan zuciya sannan ya nufi kofar dakin cikin falon ya fice zuwa tsakar gida da innawo ke tsaye.

Gaban kofar ya sameta cike da kallon tuhuma ta kalle shi ina Indon?

Kawar dakai yayi can gefe sannan yace wai wace miki tashigo nan din?

Runtse Ido Innawo tayi, Aliko wannan ba halin ka bane ka bude min kofar nan.

Ai kinsan ba'a bude wannan kofar muje ta ciki ki duba ki gani.

Ban zuwa, alamu ya nuna kana amfani da kofar nan Aliko, dan ada ba haka rufuwarta yake ba. sannan yariyar nan sau uku ana shigowa nimanta ni jikina ya bani indo na dakin ka.

Zuwa yanzun kam bashi da mafita dan haka ya kawar da kanshi tare da fadin karatu tazo.

Raratu?, toh daman har yanzun ba'abar wannan karatun ba?, Maza ka bude mata kofa ta fita tun kafin uwarka ta dawo.

Lumshe ido yayi, sannan ya koma ta inda ya fito, Aysha ce ke zaune ta fara hawaye ya cemawa tashi muje"

Mikewa tayi tana raba ido, yayin data rike wani daga cikin littafin ta ahannu, jakar makarantar ta Aliyu ya dauka sannan suka fito Ayaha na gaba Aliyu na binta abaya, a tsakar gida suka hadu da innawo, kallo kawai ta bisu dashi yayin da Ayaha ta wuce sumi sumi, ganin da Innawo tayi Aliyu nashirin fita har kofar gidan tare da Ayaha tace dawo Aliko.

Lumshe ido yayi sannan ya mika mata littafinta ya dawo ciki.

Wanni irin kallo innawo tabishi dashi sannan  ta dawo takoma ta zauna tare dasa tagumi.

Kusa da innawo ya zauna domin ya kula hankalin Innawo ya tashi sosai, dan tafadata yayi, Innawo menene wai?, Naga duk kin damu ne.

Ba dole in damu ba Aliyu, bamu ankara ba har ka canza hali Aliyu, me zai kaika ka dauki yariya mace budurwa kasata cikin dakin ka ka rufe kofa ka rufe window babu me ganin ku sai Allah.

Wani irin kallo yai mata, Innawo wannan ce budurwa?, Aysha ai karama ce.

Himmmm Aliyu ka gyara tunanin ka, mace mace ce, ba iyayenta ba harni bazan amince da haka ba, hakika nashiga tashin hankali, ga manya manyan 'yan mata can awaje me zakayi da Ayaha dahar za'a ce maka ka rabu da ita ka kasa rabuwa da ita.

Innawo ki fahimceni, ni kina bani dariya idan kina nuna wai son ta nake, haba Innawo kallini fa, babban yaro ne fa, Aysha fa ko nono bata dashi, me zanso a ita?, wlh karatu take so kuma nasan bazaku bari ta dinga zuwa ba sabo da kakarta, niko ban tsoron kakarta.

Baka tsoron kakarta?, amman kasan duk wanda yaga wannan al'amarin zai kawo wani tunani daban ko?

Innawo dan Allah kibar wannan mgnr, toh waini ce miki akayi dan iskane ni?, alkawari na dauka zanbawa Aysha gudunmawata dari bisa dari akan karatun ta, kuma kome wani zaice bazan janye ba daga abun da nai niya, Innawo ai daman mutum baka iya mishi, dan haka kawai mutum yayi abun da yake ganin ya dace karya kula da me mutane zasu ce.

Zuwa wannan likacin innawo ta kasa mgn damin ta lura lamarin nashirin girmama, daker ta iya fadin, " kenan Aysha zata cigaba da shigowa gidan nan, Kuma acikin dakin ka batare da kowa ya sani ba??

Zanso ki ki rufe min wannan sirrin Innawo, ki yadda dani, wallahi daidai da rana daya banta bataba ji cikin raina wai zanyi wani abu da ita ba, ina mata kallon kankanuwar yariya ce yayayyiya, ina jinta acikin zuciyata kwatan kwacin yadda nakejin Husna, sai dai nashaku da ita sosai fiye da Husna, ni kaina ina son yi mata karatun innawo.

Wani irin yawo Innawo ta hadiye sannan tace, Mahaifiyar ka bazata yadda da wannan tsarin ba?

Karki gaya mata dan Allah"

Waigowa Innawo tayi ta kalle shi sannan tace shikenan.

****

Karfe 6 Aysha ta taso islamiya tun daga nesa ta hango motar Aliyu akofar gida, dan haka ta labe wani zaure tare da kiran wani yaro, dan Allah kaje can gidan kace ana kiran Aliyu.

Juyawa yayi yayi Ayaha ta sake kiran sa idan an tambaye ka inji waye kace inji wani ne.

Tafiya yaron yayi ba jimawa sai gashi sun fito tare da Aliyu, lekawa tayi ta hango su dan haka ta fito"

Tun daga nesa Aliyu ke murmushi, Aysha ma cikin jin kunyarsa take murmushin.

Karasowa yayi gabanta lallai ma yariyar nan kin rainani,towai kece har zaki tsaya kice akira miki ni?

Dana sani nashigo???

Kishigo kimin me? ba dazon maka rabu ba?

Lumshe ido tayi sannan tace na dame ka ko?

Ni bance ba, amman dai kinsan yanzun gida ya dace ki isa ko?, ogogo ya kalla yazun za'a kira mangariba kije gida.

Jikinta babu wani karfi ta wuce dan haka yace, nagode da kika leko na ganki.

Gani yayi ta juyo tayi mgn, tana kifkifta ido tare da jujuya bakinta, sai dai tayi nisa dashi bayajin me take cewa dan haka ya zuba hannun sa cikin aljihu ya bi bayanta, tana gaba yana binta abaya yake fadin.

Ni kike murgudawa baki?

Tana gaban sa da tazara tsakanin su sosai tace, ni ban murguda maka baki ba.

Takawa take cigaba dayi yayin da shima yake cigaba da takawa, yadda suke da tazara ko mutum kusa dasu yake baya iya gane magana suke yace, " nagani ai, kenan kema kin iya murguda baki.

Ya nifa ban murguda maka baki ba, ka koma kar wani ya ganmu.

A'a aike kika aika har gidan mu a kirani dan haka duk inda kika shiga saina biki"

Dariya tasa tare da dan juyowa ta kalleshi, yaya wallahi ka shiko gidan mu zaka hadu da Umma.

Toh bake bace daga nace yanzun muka rabo kin hau fushi, da bakiyi dariya ba har ciki zan biki.

Ton naiyi ai kaje kaji.

Korata kikeyi?

A'a tsoro nake kar wani ya gan mu.

Ko an gamu ai baza'a gane tare muke ba.

Eh amman nakusan shigewa gida in barka awaje.

Ba komai, ana aiken kine da daddare?

Wata rana dai ana aike na gurin idi sawu maganin sauro ko wanni abun.

Zaki fito anjima injira ki a wajen ?

Eh amman  kuma ni idan ba'a aikoni ba fah?

Sai in koma gida inta kuka.

Dariya ta kuma yi tare da dan juyowa ta kalleshi toh ai bana wajen bare inyi dariya.

Lallai ma yariyar nan, wato har kukana ma idan inayi dariya zaki min?

Toh daman babba kamar ka yana kuka ne?

Yanayi mana, amman ni bazakiga kukana ba insha Allahu, danni bana kuka, amman anjima idan  baki fito ba zan kasa bacci.

Zanzo tafada adaidai lokacin data dafa kofar gidan su dare da fakan idon mutane ta daga masa hannu cikin fara'a.

Da kansa ya amsa, tare da daga mata gira, tana shigewa gida shiko cigaba da tafiya yayi saida yai nisa da gidan nasu sannan ya dawo ya nufi masallaci.

******

Da daddare kamar yadda Aliyu yace ya Isa gurin idi me shago Ana fitowa sallan Isha,'i saidai har ya karaci zaman sa Aysha bata fito ba, dan haka ya nufi gida, tashi yayi ya nufi gida cikin sanyin jiki sosai domin ba haka ransa yaso ba, Koda ya kwanta gadon sa yata tuna Aysha yana dariya daga can bacci me nauyi ya dauke shi.

Misalin karfe 03:15pm, Aliyu ne kwance bakin katifar sa, runtse idon sa yayi da karfi ayanzun jiran zuwanta kawai yake yi, zuwa can yaji ana kwankwasa kofar ahankali.

Sakowa yayi ya Isa ya leka window Aisha ce dawowa yayi ya bude kofar ya leka ya mata nuni da tashigo sannan suka shiga dakin tare da maida kofar ya rufe.

Ina wuni Yaya Aliyu?

Lafiya Lau, ya fada tare da mika masa hannu ta bashi litrafinta.

Littafin ta fito dashi sannan ta mika masa  cikin daure fuska ya amasa.

Satan kallon idon sa take yadda yake daure fuska saita tunashi acan da kafin ya fara

sakar mata fuska.

Karutun yake mata, Amman kwata kwata hankalinta baya gun karatun tunanin ta kawai be wuce tasan me yake damun sa ba dan haka ahankali tace, ' yau baka da lafiya ne?

Lafiya ta Lau, bacci ne kawai ban samu ba jiya, kaina ciwo yake min.

Littafin ta mika hannunta ta dauka ta maida cikin jaka adaidai lokacin da yake cewa kawo Mana.

A'a baka da lafiya gobe sai muyi,

Ki kawo nace.

Yaya ka bari gobe sai muyi.

Idan gobema na tashi da rashin lafiyar fa, ni haka nake idan banyi bacci ba saina kwana biyu Banda lafiya.

Lumshe ido tayi sannan tace, jiya bakayi bacin bane?

Banyi ba ya bata amsa yana me kawar da kansa.

Yi hakuri, naso fitowa ba'a barni bane, amman yau insha Allahu zan fito.

Sakin ransa yayi kadan dan kaha Aysha ta sake cewa kayi hakuri kaji?

Naji, kawo littafin to.

Kabarshi sai gobe.

Komawa yayi ya kwanta saman katifar, yayin da Aysha take zaune kujerar dake gefen gadon tana me karewa sumar kansa ido ahankali ta kira sunan sa, Yaya Aliyu?

Na'am indo.

Bakayin aski ne??

Dago kansa yayi yana kallonta tare da fadin, me kika gani?

Naga gashin ka yayi tsayo kamar na mace.

Murmushi yayi, macen da bata da gashi ko?, Inayi kawai yana saurin taruwa ne.

Sumar ta Kara kallo sannan tace, Yaya Aliyu?

Na'am indo, ya sake fada akaro na biyu.

Inma kitso?

Kitso kuma Ayaha?, Kin iya kitson ne?

Eh na iya.

Murmushi yayi bayan ya kalli fuskarta ya tabbatar da gaske take sannan yace yi min to.

Hannunta ta daura kansa tare da diban gashin kamar yadda makitsa keyi ta fara kitsawa.

Duk abun da take Sadiq najinta, aciki zuciyar sa yasan babu wani kitson da zata iya dan haka ya barta ta masa din, yanajin yadda take ta cikuikuye masa gashi, ita ko Aysha yi take tana cigaba da surutu yayin da yake amsa mata, saidai zuwa can taita magana tajishi shiru dan haka ta leka fuskarsa, baccin sa yake merai da lafiya dan haka ta fashe da dariya wadda dariyar ta tadashi.

Ke baki wuce ba.

Nagama maka kana bacci.

Tashi yayi zaune, tashi ki wuce gida, saukowa yayi ya leka tsakar gidan yana fadin, yi maza insaki ta window Innawo da Ummi suna kitchen.

Takalmanta ta diba yayin da Aliyu ya dauketa cak ya zurata batare daya lekaba kamar yadda yasaba kowacce rana.

Gaban sa ya yaji ya fadin adaidai lokacin da yaji muryar wata na fadin, Innalillahi wa inna ilaihir raju'un, toh kuzo ku gani.

Jin wannan kalamin yayi matukar daga hankalin Aliyu, dan haka ya taho da sauri ya leka.

Wata mata ce take tafa hannuwa cikin tsabar mamaki da tashin hankali akan fuskar ta, yayin da Ayaha ke rungume da jakar makarantar ta tare da takalmanta a kirjinta.

Innawo da Ummi ne suka karaso gurin yayin da matar ke fadin kunce bata shigo ba?, Gata adaki. Katon namiji balagagge.

Ummi ce ta kalli Aliyu dake tsaye ta window, cikin tsananin mamaki ta juya ta kalli matar

tana fadin, " Murja daga Ina kikaga Ayaha ta fito?

Gashi kina gani kuwa ga wadda ya daukata nan cak daga cikin dakin ya dareta anan, akan idona ba wani ne ya gaya min ba, nifa daman jiya da idona naga shigowan Ayaha gidan nan Amman kukace bata shigoba sabo da da hadin bakin ku ake sata adaki.

Wani irin kallo Ummi taiwa Aliyu na tuhuma sannan tace, Aliyu kaika sako Aysha ta window?

Fuskarsa daure sosai yace eh.

Eh?, Aliyu eh fa kace min?

Lumshe idon sa yayi cikin yanayin dake nuna beji dadi ba, yace Ummi karatu tazo"

Karatu?, Hannunta ta daga cikin zafin rai ta rafka masa mari wadda har saida yasa hannunsa ya dafe.

Murja kuwa juyawa tayi ta fice agidan tabar Aysha tsaye agurin"

Innawo kuwa bata da bakin mgn, rasa abun yi yasa Ummi fashewa da kuka, cikin kukan take zagin Aliyu mgn ta ciki bacin rai babu irin wadda bata fada masa ba.

Idon sa ne ya kada yai jawur, tare da fadin, Ummi tsaya kiji, amman Ina ta inda take shiga batanan take fita ba, cikin wannan yanayin Umma da Murja suka samu Ummi, nan umma ta shiga surfawa Aliyu zagi tare da fadin, ya lalata mata jika"

Idan hankalin Ummi da Innawo yakai dubu toh yau duk sun baci, cin mutunci sosai Umma kewa Aliyu yayin da yake kallonta ido cikin ido tana me nuna shi da yatsa, wannan lokacin Innawo hakuri ta shiga bawa Umma yayi da Umma ke ture Innawo tana zagin Aliyu.

Cikin wata irin murya me cike da karadi da hargowa yake kadawa Umma Hannu tare da fadin karki Kara zagina ya isheki haka

Eh lallai, ke Murja kiga min dan iska mara mutunci, wadda besan darajan manya ba.

Juyowa Aliyu yayi afusace ya fito daga dakin, ganin barin sa dakin Innawo da Ummi sukayi cikin gida aguje, ganin sa sukayi da masifar gudu ya fito daga kitchen dauke da bakin wuta ya nufusu, tara tara suka masa daker suka samu suka rike shi yayin da Umma ke fadin, kubarshi ya kawo dan uban shi.

Zafgegen itace ne ahannun sa, yayi da Ummi da Innawo suke kokarin kwacewa, duk yadda suke son hakan ya gagara  kokarin nufar Umma yake yayin da Umma ke tsalle tana surfa masa

zagi,

Daker Ummi da innawu suka tura Aliyu cikin daki suka maida kofar suka rufe.

Zuwa wannan lokacin jama'ar unguwa sun fara cika gidan, mutane ne tun daga ciki har kofar gida, ganin yadda aketa gutsura mgnr ya dagawa Ummi hankali yasata daukan gyale bashiri tabar gidan.

Innawo ko da mutanen unguwa daker suka fitar da Umma da iyalenta, har gida Innawo ta bita tana me bata hakuri, hakama kwakota hakurin suke bawa Umma domin dai babu wadda ya taba ganin abokin fadan Aliyu Kuma ba'a sanshi da wani mugun hali ba, asali ma be cika sakin fuska ba, sai dai kowa yasan shi mutum ne meson yara, daker Umma ta lafa sannan suka baro gidan, ganin yadda hankalin Innawo yake atashe mutane sukaita kokarin kwantar mata da hankali, har cikin gida wata makociyarta ta rakata yayin da har wannan lokacin Aliyu na rufe adaki.

Innawo ce atsakar gida tare da inna talatu makociyar su, inna talatu ce tace toh abudeshi Mana.

Kofar falon Innawo ta kalla, a'a rabu dashi aciki, fadan karfin hali yake yi, mutumin da bashi da gaskiya wai shi ke tada jijiyoyin wuya.

Ummi ce ta dawo ita da Alhaji Umar da wani yayanta Alhaji sani, ganin su Inna talatu ta tashi ta fita.

A tsakar gidan suka tsaya suna maida mgnr Ummi kuwa gefe ta koma tasa tagumi, bayan Innawo ta gama musu bayani Alhaji Umar yace, " yanzun Ina Aliyu?"

Rufeshi mukayi tunda yaki sauraron kowa.

Mikewa mazan guda biyu sukayi suka bude kofar suna kallon yadda Aliyu ke huci"

Alhaji Umar ne yace sannu da karfin hali.

Sunkuyar da kanshi yayi kasa tare da gyara wuyan rigar sa.

Alhaji Sani ne yace wai toni abun dake daure min kai, karattun dole ne?, itama yariyar yar iskace bata da tarbiya.

Ummi ce tace ai ni yanzun ma Aliyu shi babba me laifi, kwata kwata indo bata wuce shekara 14 , Ina za'a hada shi"

Alhaji Sani ne yace, au 14 aini na dauka ma ko budurwa ce.

Ina fa sa'ar Husna ce fah, nan suka shiga masa fada tare da Haddad masa bashi ba Aysha, sosai suka masa fada tare da daura duk laifin akanshi, sannan suka wuce gidan su Aysha suka Kara bada hakuri, yayin da Innawo da amsa da sharadi. Baruwan Aliyu da Ayaha.

Koda suka dawo gida, Sun Kara zaunar da Aliyu tare da gargadin sa sosai akan Aysha, Ummi ko sabo da nuna tsananin bacin ran da tayi aka sashi ya bata hakuri.

Tuni unguwa ta dauka ko Ina labarin ake yayin da hakan ke Kara tada hankalin Ummi.

***

Har akayi kwana biyu da faruwan abun fuskar Aliyu bata dawo daidai ba hama fuskar Aysha da kannen uwar ta suka taro suka zane, yau ta fara zuwa isalamiya, koda tazo wuce gidan su Aliyu rage sauri tayi tana me kallon kofar gida.

Misalin karfe 6 Aliyu ne zaune saman motar sa akofar gidan su, tun daga nesa ya hangota dan haka ya maida hankalin sa gareta, lokacin da tazo saitin shi murmumai daga nesa yayin daya mayar mata, sannan yace.

An bigeki ranar?

Batare data tsaya ba tace, eh

Wace ta bigeki?

Sakkowa yayi yafara takawa abayanta"

Gaba dayan su saida suka dakeni.

Allah ya isa ya fada, sannan ya sake cewa, kwa biyu ban gankiba banajin dadi.

Nima haka.

Zaki fito anjima gun idi?

Kila, ta fada tare da hawa gadan gidan su.

Zan jira ki awajen ya fada tare da wuce gidan nasu.

08:00pm

Umma sauro sun hanani bacci baki da maganin sauro ne.

Buda cikin kwanon nan ki dauka.

Bude kwanon Aysha tayi bakomai aciki Umma.

Babu?, miko min ingani.

Mika mata tayi, ganin babu ta dauko kudi ta mikawa Aysha amsa maza kije ki sawo................

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

Episode 15- 16

Agogon dake daure a hannun sa yake kalla tare da waigawa ya kalli kofar gidan su Aysha.

Har cikin ransa yake son ganin ta, yayi da ya kafe gidan nasu da ido yana daga karkashin wata katuwar fishiya gefen shagon idi cikin duhu.

Akan idon sa ta fito daga cikin gida, murmushi yayi wadda yasa zuciyarsa yin fari Kar sannan ya zuba mata ido harta karaso gaban shagon idi"

Hasken fitulun unguwar ne ya haske fuskar Ayaha, itako har ta Isa shagon idi raba idon take yayin da yaita murmushi.

Ganin harta amsa maganin sauro din tana ta waigen bayanta yasashi tausasa murya tare da mata dan Kira, Indo!!!

Cikin sauri ta kalli cikin duhun tare da dan karasawa gurin ta dan tsaya nesa dashi,yaya Kaine anan?

Eh shigo mana Indo"

Nidai gaskiya ka fito sarari.

Murmushi yayi kadan, kina nufin nan asako nake?

A'a kam Yaya, amman duk fadin layin nan mu rasa inda zamu zauna sai a mattarar aljanu"

Dariya yayi har ya fitar da sauti sannan yace, kice tsoro gareki kenan?

Nidai banson bishiya.

Waigawa ya fara yi to Ina zamu tsaya  nan yafi sirri ai"

Nidai ka fito nan gurin.

Takowa ya farayi hannun sa cikin aljihun sa  yana me binta da kallo, Yaya akayi kika fito?

Wayau nama Umma, cemata nayi sauro ya hanani bacci.

Ke!!! nine sauro?

Cikin matsancin murmushi tace, " Kai!! Yaya ta yaya zance maka sauro?

To danwa kika fito?

Dan kai.

Kinga kenan nine sauro.

A'a Yaya kafi karfin sauro, ni kawai wayau nayi dan in fito.

Toh naji me wayau, yanzun Ina kudina kodan ban miki karatu kwana biyu ba shikenan bazaki bani ba wannan karon?

Cikin dariya sosai tace wlh yaya kacika son kudi.

Kinga laifina?

Tana dariya tace a'a.

To gaya min Ina kudina, suna jakata Ina Tara maka ai.

Toh kin kauta, yanzun ki koma gida sai gobe ko?

Kaita daga alamar eh.

Hannunsa dake cikin aljihun ya murza sannan ya fito da kudi ya mika mata.

Yaya daman kana da kudi ne?

Au kin dauka kasuwan da nake zuwa gantali ne kawai?

A'a Yaya ni bance ba, amman ni ka barso, yanzun fa ka gama tambayana kudi.

Eh naki nafiso.

Toh zan baka nawan wannan ma ka barshi.

A'a ya fada yana waigen layin tare da fadin kona sawo miki nama ne?

Itama?, waigawa tayi ta kalli me naman tare da fadin, ni banson Naman mutumin nan dama dai me kuli ne.

Me kuli?, Hanyar ya kallah Ina zuwa to barin nemo miki me kulin.

Mikewa yayi yabi saman layin yayin da Aysha ta fara raba idon kar wani ya ganta, Aliyu be wani jima ba ya dawo ya mika mata ledan sannan ta nufi gida.

Shima fitowa yayi yana me bin bayan ta bayan tahau gadan gidan su ya daga mata Hannu itama ta daga masa.

Maida hankalin sa yayi kofar gidan su, yayin da ya hangi Innawo zaune kan takalin dake kofar gidan.

Kallonta yayi sosai sannan ya karasa
Yana fadin Innawo me kike nan?

Karaso ta fada ahankali.

Karasawa yayi tare da zama gefenta, sai dai ya kula akwai damuwa akan fuskarta dan haka yace Innawo meke damun ki ne.

Kallon shi tayi sosai sannan tace, Aliyu Kaine, Aliyu me kake nema ne gurin Aysha, yanzun ranar nan yadda aka tara maka jama'a bakaji kunya ba? Abun da ya faro ranar ko yaro na goye

da yana da baki saiyace wani abu domin ko yagaji da Jin sunanka bakin uwarshi da ubanshi wajen maida mgnr, kuma duk wadda yaji wannan Ibrn dole saiya zarke ka, yanzun wannan besa kai hankali ka rabu da Aysha ba, to yanzun daga Ina kuke??🤔🤔.

Zancen kauce kauce be taso ba, Aliyu ya fada azuciyar sa, afili kuwa cewa yayi, ni naje wajen idine kawai muka hadu.

Kuka hadu Aliyyu?, Yanzun Aliyu bazaka guji wani abu ya sake faruwa ba?, karka bari a buga maka tanbari fah.

Innawo nifa, abun da wasu zasuce baya damuna fah, tunda nina San ba wani mugun abu neke ba, Allah ma yasani, toh Innawo idan duk duniya zata dauka bani da kirki ni dan iskane suje suyi tayi, ai zargi haramun ne, Kuma ni ba dan iska bane, ko Ina iskanci bazan tsaya a jaririyar yariya kamar Aysha ba, taimakonta kawai nake ni.

Wanni irin kallo Innawo ta masa na tuhuma sannan tace Amman kuwa idan har haka kake da kafiyan tsiya baka dauko abun arziki ba, Kuma matsawar baka rabu da itaba toni nabar bin bayan ka, kuma zan gayawa uwarka domin baxan bari abun yai nisa ba, mikewa tayi ta shige gida yayin daya bita da kallo.

****

Ganin duk suna bacci ta lallaba ta wuce bayan Umma ta kwanta, kusan minti 20 da kwanciyarta sannan ta fara laluban namanta tana turawa abaki, tas ta cinye sannan ta saka agadon tasha ruwa tare da fita tasa ledan abola tare da wanko hannunta ta koma dakin.

Washegari da Safe Umma ta fito ta nufin shara, gidan tashare tsaf sannan ta kwashe ta nufi bola, ledan datagani saman bolan ne ranta be kwanta dashi ba dan haka ta dauko ta bude.

Nama me kuli ta hanga aciki guda biyu tare da yankan albasa, cike da mamaki ta juya ta kalli dakin tare da kwalawa mamakira.

Fitowa mama tayi yayin da Umma tace, waye ne yaci nama da tsohon dare dan munafunci.

Nama?, Umma.

Nama kuwa gashi nan dan keta har zubarwa akayi, idan bake bace to yarki ce.

Jimmmm Mama tayi sannan ta fito tana leka takardan sannan ta kwalawa Aysha Kira"

Ganin takardan Naman jiya hannun mama gaban Aysha yai mugun faduwa.

Ina kika samu wannan Mama ta tambayeta.

Tsintan kanta tayi da fadin, idi me shago ne yabani.

Ke kiji masharraciyar yariya, ni Zaki rainawa hankali, shi idin me yaci bare yaba wani, duk yadda akayi kin hadu da wannan dan iskan yaron, shine kawai duk nan duniya yake da wannan karfin halin, dauka yake kamar shidin babu wadda yake shayi, kana masa mgn yana wani rurrufe idon sa na rashin d'a'a.

Kallon tuhuma Mama tabi Aysha dashi sannan tace, fita kikayi da daddare??

Sunkuyar da kanta tayi Umma ce tace na sawo mata maganin sauro.

Zaro ido Umma tayi, nace ki sawo min maganin sauro koko ke kikace min sauro ya hanaki bacci?🤔

Ke kika aikeni, Aysha tafada batare data kalli inda Umma take ba.

Cikin tsabar mamaki Umma tace, eh lallai Aysha baki da kirki, zuciyarki bata dakyau Sam, Kuma idan ba da gaske aka miki ba mgn Zaki dauko mana akwai alamun hakan.

Mama dakin ta dawo yayin da Aysha ta zauna abakin gado cikin tagumi.

Itama mama cikin damuwa tace, " Jiya kinje gurin Aliyun ne?"

Nifa Idi ne fa ya rage daidai naje Sayan maganin sauron ya miko min.

Shikenan Mama ta fada sannan ta juya ta fita tsakar gida, yanajin tashin hirarsu sai dai bayajin me suke cewa.

*****

Indai nice uwarka dana tsuguna na haifeka toh nagaya maka ka rabo da Aysha, wai wanni irin masifane haka, me kake nema wajenta Aliyu?, aita mgn daya ko kunya bakaji, wlh bantaba maka shedan rashinji ba, Kuma bantaba tunanin haka daga gareka ba, nasanka dai da fushi kamar kuturo amman baka da rashin ji sai wannan karon, ni daga gau bazan sake maka mgn akan Aysha ba, Amman kasani, nafada Kuma zan Kara fada maka ayau, tunda nake a duniya bantabajin natsana wani mutum ba kamar yadda na tsana Aysha, Aysha karamar yariya ce amman tanada naci, tun tana zuwa karatu  yanzun gashi wai har Kai kebinta kofar gidan su, duk da irin kashedin da aka maka. Ninayi  Innawo tayi, su Yaya ba irin mgnr da basu makaba rana duk akan ka rabu da ita amman  Ina, to yau nace maka indai nice uwarka ban amince  ko sake kallon Aysha ba bare har kayi mgn da ita.

Jikin sa amatukar sanyaye yace shikenan naji, kiyi hakuri.

Dauke idonta tayi yayin daya mike yana ma Innawo wani irin kallo.

*****

Misalin 8:30pm Aliyu ne ke juyi kan gadon sa, duk cikin son hana kansa fita, fuskar Aysha yake tunanawa tana wannan dariyar tata dake sashi nishadi.

Tashi yayi ya zauna, har ga Allah yana son bin umarmin Ummi sai dai wani abun da yakeji yanai masa yawo balakin son ganin Aysha yake yake dan haka ya Mike kawai ya fito hannun sa cikin aljihun sa.

Yana dafda fita falon Innawo ta fito tana fadin, " Ina zuwa?,

Gadina kike ne?, Wucewa yayi batare daya jira amsanta ba.

Kallo ta bishi dashi har ya kule ko tantama batayi gurin Aysha zashi dan ada daya dawo sallah baya sake fita.

Wani irin yanayi ta shiga na damuwa ko Yaya karshen abun zai kasance oho, tunda Aliyu ya fita har kusan minti 15 da fitansa Innawo ta kasa sukuni tashin hankali ne da damuwa me tsanani cikin zuciyar Innawo.

Innawo!!!

Na'am Fatima.

Ina Aliyu, Ummi tafada alokacin data fito daga dakin Aliyun.

Cikin tsananin damuwa tare da takaici tace ya fita.

Jimmmm Ummi tayi zuwa can ta koma ta zauna tare da fadin, Innawo mun shiga uku, wani irin al'amari ne wannan.

Waigowa Innawo tayi tana fadin, wlh kuwa tunanin da nake kenan, zance duk ya wade unguwa amman shiko ajikin shi, Kuma ni abun dake daure min Kai ita yariyar ba aure ta Isa ba bare ace sonta yake.

Innawo kibar wannan mgnr, ni yanzun mafita kawai nake nema, yanzun fa Kila gurinta yaje, ko Ina suke haduwa ma oho🤔

Innawo ce ta mike tana fadin, Ina zuwa barin leko shi.

******

Ya akayi kika fito daga gidan?

Duk bacci suke.

Lumshe ido yayi tare da fadin, ban zaci zaki fitoba ai, kawai fitowa nayi in kalli kofar gidan ko in koma in kwanta .

Dariya Aisha tayi irin Wanda kesa Aliyu nishadi cikin ransa sannan tace, " Yaya ka kalli kofar gidan fa kace?

Eh Mana, da babu ai gara ba dadi ko? Yanzun bani Ibrn makarantar Yaya karatun kwana biyu.

Yau banje makarantar ba gidan kitso naje har sai yamma nadawo.

Shine baki aiko aka kirani ba?

Banga motar ka ba ai"

Ban dawo ba kenan lokacin, kice yau kitso kikasha?

Eh cewa nayi amin irin wadda namaka ranar nan.

Cikin sauri ya shafa kansa tare da fadin, aini babu wani kitso akaina kindai har batsamin gashi kawai.

Wlh na maka kitso ranar. Matsawa tayi daf dashi tana daka tsalle domin ta samu ta taba kansa tace daya yabi tanan dayan Kuma tacen yabi.

Dariya yayi sannan yace ni banga komai ba akwai dai alamun an cuccure min gashi.

Toh sai in warewa yayi daman kanka ya cika santsi

Kedai kice baki iya ba kawai.

Yaya kasan me?

Sai kin fada.

Gashin kanka fari ne shima.

Fari Kuma Aysha??

Eh sabo da farin shima da kadan fuskarka tafishi haske.

Dariya ne ya kamasa yana me kallon fuskanta tare da yanayin girmanta so da yawa idan tayi wani abun mamaki take bashi, tunda tai mgn ta koma can gefe tana rufe bakinta.

Shikowa Aliyu murmushi yake tare da fadin kizo nan ni ba abun da zan miki, d'anawa kika yi.

Motar da Aysha ta hango ta faka kofar gidan su yasa Aysha ta saurin waigawa.

Umma ta iya shaidawa tare da wan mahaifiyarta sai wasu maza guda biyu, cikin tsananin firgici da tashin hankali ta koma bayan Aliyu tana fadin nashiga Uku yaushe Umma ta fita?🙄

Aliyu kuwa hannunsa duk biyun ya zuba cikin aljihun tare da tsayawa tsaye babu alamar fargaba cikin fuskarsa.

Gadan gadan suka nifo garin yayin da Umma ke fadin, " gashi nan katon ballagagge yana neman hurewa yariya kunne domin ta bujirewa mgnr iyayenta.

Shikuwa yayan Mama fadi yake ku tafi dashi, Ina Aishan?

Police ne guda biyu suka rike Aliyu yayin da Aysha tai saurin ta rike rigar Aliyun ta baya tare da share hawayenta jikin sa.

Duk yadda suke jansa yaki jawuwa fadi yake ku sakeni intafi da kafata.

Baza asake kaba, kuja shi Dan iska ne mara mutunci, me kokarin raba yara da iyayen su muje can ofishin su amana iyaka dakai

Cikin sauri Aliyu ya fixge kadarsa daga hannun Dan sandan dake rike dashi yafara takowa gaban Umma yana fadin, adai rika Jin tsoron Allah, Kuma na tabbata rana tana nan zuwa.

Cikin kufula Umma tace haka kaima taka ranar tana nan zuwa, kada ka jinkirta tuba wai dankai saurayi ne, ah'ah, dan amakabarta babu inda aka rubuta tsofi kadai.

Tafe yake Aysha na rike dashi har yanzu yayin da Aliyu ke sake fadin, inda kika nufa kenan ke?, to kisa azuciyar ki jiya ta wuce bazata taba dawowa ba.

Oho maka Mara mutunci, kokarin tura Aliyu suke yayin da adaidai wannan lokacin Innawo ta karaso cikin rasa abun yi tasa koka tare da fadin, kagani ko, fadi yake Innawo ki koma gida.

Sosai gurin ya ciga duk da cewa darene, wani abun da ya daurewa mutane Kai gadai Aliyu

acikin motar police Amman Aysha taki sakin rikarsa duk da irin dukan da Innawo ke dirka mata"

Jawota ake tana sake komawa cikin matsancin kuka yayin da kukan nata ke Kara jawo hankulan mutane.

Mamaki jama'ar gurin suka fara yayin da wasu ke dariya wasu ko cewa suke wannan lamari. Ko na lafiya ne?🤔🤔

Ganin an dauke lokaci bacin rai yasa mahaifiyar Aysha Mama cewa itama atafi da ita aci ubanta, tunda bata da mutunci.

Da yawan mutane agurin wannan shawaran suka bada yayin da wasu ke fadin gara atafi dasu a horasu a samu saukin abun, dan haka aka barta Tashaga motar,
yayin da aka wuce dasu gaba daya.

Duk abun da ake Ummi taji, bacin rai ya sata fadin, aje dashi duk abun da za'a mishi amishi tunda shine ya sayawa kanshi.

Innawo kuwa hawaye yaki tsaya cikin idonta ita kadai tasan me take ji.

Hakama ma mahaifiyar Aysha tsananin bakin ciki yasa take addu'ar Allah yasa suma Aysha dukan dasai ta kasa tashi ta hakane kawai za'a samu saukin abun........

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

episode 17-19

Wannan daren duk gidaje biyun basu runtsaba, innwo ko addu'a taitayi cikin wannan daren Allah ya daidaita wannan lamarin.

Itako Ummi tsabar haushin Aliyu ne cikin ranta, fushi tayi dashi me tsanani irin wadda ta

jima batai ba dan kaha ta dauna kawai tare da zubawa waje daya ido.

Hakama gidan su Aisha Umma Banda juyi ba abun da take, yayin da mama ke share hawayen takaici"

Umma ce ta tashi zaune tana fadin, wai kuka kike ne?, nikaina banso ace har Aisha aka tafi ba, amman ki duba yadda akejan Aysha tana tana Kara rike yaron, ni babban abun dake daga min hankali yaushe har sukayi sabo da yaron nan har haka, duk taka tantandin da mukeyi da yariyar nan Amman bata gani🤔

Hmmmm, Umma inajin takaici sosai, amman gara azane Aysha ta yadda ko kofar gidan su yaron bazata sake kallo ba, inason amata dukan dasai ta kasa gane yaron, amata dukan dasai tayi wata da wattanni zana iya taka kamarta, tunda ita tace bata da mutunci muzuba"

Cike da karfin guiwa Umma tace, da ammata haka zamu samu sauki insha Allahu. Shima Mara kunyan yaron idan jikinsa ya gaya masa ya fita hanyar yariyar.

******

Washegari Innawo taso suje domin duba halin da Aliyu ya kwana ciki amman Ummi tace kartaje, sannan ta hana agayawa kowa daga cikin 'yan uwanta, acewarta abarshi can saboda idan yaji wuya ya kiyaye gaba, badan ran innawo yaso ba take hakuri domin kuwa itama tana son Aliyu ya fita hanyar Aisha.

Har aka kwashe tsayon kwana uku babu wadda yaje gurin Aliyu, da yammacin ranar da suka cika kwana uku ne Innawo tace, Fatima horon nan ya Isa haka, yakamata aduba yaron nan fah.

Innawo abarshi dan Allah.

A'a Sam bazai yiwu ba, Kuma kema nasan karfin hali kikeyi azuciyar ki kinajin zafin abun.

Innawo kina kallon dajin yadda naita masa mgn aranar Kuma yacigaba da abun da yaga dama.

Fatima hannun ka baya rufewa ka yanke ka yar.

Toh Innawo ita Aisha da suka bari acen fa, macece itafa ba namiji ba, amman tunda sunga abun nasu bana lafiya bane sai suka barta acen ai kaza tana taka danta badan bataso bane.

A'a, ai ita Aysha tun washegari akace sun tafi su dawo da ita.

Innawo ai tabawa tace min basu dawo da itaba har yau tana can itama.

Innalillahi wa inna ilaihir raju'un 🤔🤔 to wanna wacce irin masifa ce, cikin sauri Innawo ta saki aikin da take tana fadin banga ta zama ba kuwa, wlh duk daukata sun karbo yariyar nan🤔

Mayafi Innawo ta dauka ta nufi gidan Umma, cike ta samu gidan duk iyalan Umma sun hallara, Koda sukaga Innawo ce daker suke amsa mata gaisuwar da take masu, kin kallon duk wani daure daure da suke mata tayi tare da fadin, ashe Aisha har yanzun tana can, wlh ji nake tun washegari kun dawo da ita, shiko dama Aliyu mahaifiyarsa tayi fushi tace abarshi can tunda bayyajin mgn.

Daya daga cikin kannin Mama ce tace, tana can, ai yariga ya gama hure mata kunne, yariya yar karama an canza mata tunani gaba daya ta zama wata iri.

Muryar wata can taji tana fadin, waya Sani ma ko tofi yaimata aruwa tasha, yariya kamar Aysha ace ta guji danginta sai wani katon banza baki mummuna dashi me BAKAR zuciya.

Ummace tace ai wlh inaga mgnr nan saitaje kofar sarki, dan idan yana ganin ya iya sammako toni atafe nakwana.

Insha Allahu mgnr bazata kaimu kofar sarki ba, yanzun zanje in sabo kawun nan shi gobe muje can akashe mgn,, da yadda Allah Aliyu yabar Aisha, kuyi hakuri mu masu laifine, haka Innawo taita basu hakuri sannan ta baro gidan bayan sun amince gobe zasu hadu a police station.

******

Misalin 10:00am duk gidajen guda biyu sun hallara, bayan tattaunawa da mazan sukayi tare da police din aka yanke shawaran zane su gaba daya.

Fito dasu akayi yayin da Innawo naganin Aliyu ta fara hawaye, shike dauke idonsa yake, haka yaki yadda ya hada ido da kowa cikin dangin mahaifiyarsa duk iya kokarin su na su hada ido dashi yaki barin hakan ta faru.

Itako Aysha lokacin da aka fito da ita share hawaye take, yayin da duk ta fada tai zuru zuru da ita.

Yan uwan mahaifiyarta kuwa zaginta suka fara tun daga nesa suke fadin, duba idon shigeya wannan yariyar kuwa jinin mu ce?

Dayar ce tace kika Sani ko jinin ubanta yafi yawa ajikinta?

Da alama kuwa wlh natsana yariyar nan, iri irin wannan mgnr sukaita yi, yayin da police din suka shiga daure hannun Aysha da kafarta kamar yadda suka gama daure na Sadiq.

Mutum biyu ne akansu kowanne da zafgegiyar bulala a hannun sa kusan atare aka fara zuba masu bulalar yayin da tun ana farko Aysha ta fara ihu, shikuwa Sadiq runtse idonsa kawai yake tare da cije leben sa.

Kafarsu da hannun su kawai ake duka, saboda azaba tumi Aysha ta fara burgima tana fadin tabari ayafe mata bazata Kara ba, daga bisani ta shiga Kiran Yan, uwana mahaifiyarta saita suka tabbatar da tayi lilis suka barta.

Aliyu kuwa tuni kafarsa da hannun sa suka kunbura sai dai har yanzun bece kala ba har aka gama aka barshi.

Tuni su Umma suka wuce da Aysha dan haka bayan ankama na Aliyu su Alhaji Umar suka kamoshi.

Koda suka shiga cikin motar bece kalama illa kansa daya hada ga guiwa duk yadda su Alhaji Umar ke kara fadan duk wani abu da zai nisantashi da yariyar, har suka iso gida fada ake Kara masa sai dai har wannan lokacin bece komai ba Kuma be kalli kowa ba.

Duk da cewa kafarsa tayi tsame be kulataba su nafara fita shima ya fita abun sa, Innawo agaba yayin da su Alhaji Umar ke bayanta Aliyu akarshe suka shigo gidan alokacin da Ummi ke alwalan la'asar.

Da kallo Ummi tabishi har ya karaso saitin ta, kallon sa tayi sama da kasa, kafarsa kunbure take sutum hakama hannunsa duk biyun, akan fuskarta ta sauke idonta, idonsa jawur tagani.

Sai wannan lokacin Aliyu ya dago ya kalli fuskar Ummin sa tare da fadin, sannu Ummi.

Kasa kasa yai mgnr dan haka ta tabe baki tare da dauke idonta daga gareshi tana fadin, ka nemi Ummi tun wuri.

Duk juyowa sukayi suna mata nasiha nan suka Kara yiwa Aliyu fada tare da Kara jadda masa ya rabo da yariyar nan, daga karshe Kuma suka bashi umarnin yabawa Ummin sa hakuri.

****

Kwana biyu yayi agida yana fama da zazzabi kafarsa kuwa daker yake iya takata, haka ma hannun sa.

Cikin wannan kwana bitun Ummi sama sama take amsa gaisuwar sa, Innawo ce kadi ke matsa masa yaci abinci amman baya iya yin hakan.

Ranar kwana na ukun ne ya farajin dadin jikin sa, har ya shirya zuwa makaranta, fitowa

yayi yaiwa Ummi sallama daker ta amsa sannan yaje har kofar Innawo yana mata sallama.

Adawo lafiya me gidan, kadai karya ko?

Zan karya idan nafita Innawo.

Toh adawo lafiya Allah ya bata sa'a.

Kofar gidan ya fito, tsaye yayi yana kallon gidan su Aysha yana tuna sanda ta rike rigarsa tana me nuna batason a tafidashi cikin matsancin kuka, duk yadda yaso daya banbare hannunta Kara rikeshi take, wani irin yanayi ya shiga game da Aysha cikin zuciyarsa wadda yake tunanin ada babu shi, bagar yayi daga dogon tunanin da ya tafi sannan ya kama hanya cikin tsabar tunanin Aysha.

*****

Tunda suka dawo da Aysha bataiwa kowa mgn ciki harda mahaifiyarta, koda yaushe fuskarta cikin fushi take, bakomai ke sata wannan bacin ranba sai irin zagin da kannai mahaifiyarta tare da yayyen mahaifiyar tata sukaita mata, ta yadda suka fadin wannan halin nata saidai idan can dangin ubanta ta kwaso su ba a dangin su ba, babvan abun da yafi bata haushi mama ma biye masu take babu wani ko mutum daya dake bayanta koya tausasa harshen sa akan kalamin da suke gaya mata, kwana biyar ta kwashe kwance sannan ta nufi makaranta.

Misalin karfe 2 Aysha ta fito daga makaranta, abin hawa take nema ta hangi mutun daga nesa kamar Aliyu yana kiranta, azabure ta fara takawa harta Isa gare shi, murmushi ne ya bayyana akan fuskarta haka shima Aliyu.

Karasowa tayi ta tsaya tana wasa da hannunta yayin data kasa kallon sa.

Ahankali yace, " Aysha ya jikin ki"

Ni lafiyata lau, tafada kanta akasa.

Murmushi yayi sannan yace ai da kika nace saikin bini nadauka jaruma ce ashe raguwa ce duka daya kika birkice.

Kamar jira take ta fashe da kuka da karfita.

Dan zare ido yayi sannan ya karasa ya dafa kanta yana fadin, yi shiru ni ai wasa nake miki daga wasa saiki kama kuka?, Kiyi hakuri nabari kawata, hannun yasa yana share mata hawayen sannan yace, Ina ta tunanin wani hali kike ciki agida ne shine nace barin zo in ganki.

Dagowa tayi ta kalleshi tace, ni Mama bata min mgn kowa ma bemin sai dai suyita

zagina ku......

Katseta yayi da fadin, kin masu mgn ne basu amsa ki ba??

Cikin kawar dakai tace a'a

Toh ke kimasu mgn kinji ko?

Kaita daga ahankali.

Yauwa ko kefa, muje in sauke ki.

Zagayawa tayi ta shiga, ko cikin motar hira suka dan taba duk da ya kula Aysha cikin fushi take, nesa da gidan ya dauketa sannan ya koma da baya yabar unguwar.

Misalin karfe uku ya dawo gida, cikin dakin sa ya zauna tare da bude kwanon abin cin daya samu adakin , tun da ya dawo yaune yai sha'awar ya cin wani abu, sai dai alokacin da yake shirin Kai loma bakin sa yaji ana fadin, Sako daga kofar sarki cikin minti 15 ana bukatar Aliyu Akofar.

Gaba daya gidan saida gabansu ya fadin, domin idan zance yakai kofar sarki to lallai lamarin ya girmama, aje abincin Aliyu yayi tare da rasa ta yadda zaiyi ya hada ido da mahaifiyar sa.

Innawo ce tace Kai Aliyu maza ka fito, fitowa yayi yana me Satan kallon dukar Ummin sa, itako Ummi wannan karon suman zaune tayi domin ko tantama batayi an Kuma ganin Aliyu da Ayaha ne.

Inawo ce ta dauki mayafi yayin da Ummi ke fadin, Innawo karkije kibarshi yaje shi daya.

Innawo bata saurareta ba tabi bayansa, yana gaba har suka Isa, yayin da suka samu Umma da Aysha agurin.

Batare da bata lokaci ba aka karanto laifin Aliyu wadda tun kafin suzo gurin Innawo tasan koma meye dai kan Aysha ne, gashedi tare da Jan kunne akamawa Aliyu da Aisha fahimta nacin su tare da kinjin mgn sarki ya bada Umarnin amasu bulala, haka akayi bulala goma goma aka masu a gadon bayan su sannan aka sallame su.

Ko ahanya Innawo batacewa Aliyun komai ba, kurmar karfi da yaji ta zama, hakama Ummi Koda taga sun dawo da kallo kawai ta bisu tare da nemarwa kanta mafita acikin zuciyarta

Zaune take ta kasa tashi ta saka wancen ta kwance wancen har taga Aliyu yazo ya

wuce ta ya fice agidan.

Innawo ce ta fito tana fadin, Aliyu fita yayi ne?

Fita yayi Innawo.

Zama Innawo tayi kusa da Ummi tana fadin, wannan al'amari ya wuce azauna ana masa fada fa, tunda dagashi har yariyar kamar ma Kara tunkudasu ake yi, yanzun karki tantamar gurinta zashi tunda yana kallo kakarta ta saita mata hanya, nifa Ina ganin addu'a ce mafita, dan wannan lamarin nema yake yafi karfin mu.

Innawo nifa bazan iya ba, gaba daya Aliyu ya sire min, nifa Innawo kudin mota kawai zan hada mishi ya koma gurin mahaifin shi, karake mgr tayi cikin fashewa da kuka yayin da Ummi tai saurin dafa bayanta tana fadin, karki mai haka Fatima, ai be saba da mahaifin sa ba, idan kikai masa haka Zaki cutar dashi.

Cikin matsancin kuka Ummi tace, Nima cutar dani yake anan Innawo, Banda cutar da zuciyata da yake Kuma yana watsar da mutuncin danginmu a idon duniya, Innawo yaranki basu jawo miki abun magana ba har kika auren dasu lafiya wani baitaba jawo miki rigimar da aka kaiki kofar sarki ba sai akan Aliyu, baki taba zuwa police station ba sai akan shi, Kuma ai bashi kadai bane jikanki.

Cikin son kwantar wa Ummi da hankali tace au to saime?, duk wannan ba wani abu bane rayuwar kenan ai, karki fara kokarin turashi inda be saba ba kinjin ko kiyi hakuri zai bari.

Sai bayan sallah isha'i Aliyu ya shigo gida, washe gari ta kama asabar ne Aliyu yana gida, misalin karfe 11:15am takardan sammaci ta samesu wadda Umma ke Karan Aliyu.

Babu wadda yaji mamakin takardan cikin su, domin kuwa sunsan hakan na iya faruwa, Aliyu ne ma ya Dan nuna ya shiga damuwa badan kowa ba sai gudun Kar mahaifiyarsa tace yakijin mgnr ta dan haka ya tsuna gabanta yana fadin, Ummi kiyi hakuri, bada gang......

Katseshi tayi da fadin bakomai jeka kawai, duk yadda yaso yai mgn Ummi taki sauraron sa dan haka ya mike ya koma dakinsa cikin tashin hankali, daker ya iya kaiwa Monday kafim ranar harya fada saboda yasan shirun dasu Ummi suka masa shima mgn ce

KOTU

BAyan an gama karanto karar Aysha da Aliyu, babban Alkalin ne ya kalli Aysha sannan ya juya ya kalli Aliyu, juyawa ya sakeyi ga Aisha yace shekarki nawa?

Cikin harcen fullacin tace , shekarata 14.

Alkalin ne ya ya bukaci datayi mgn cikin harcen French dan haka tai saurin juya harce ta sake maimaitawa.

Juyawa yayi ya kalli Aliyu tare da fadin, Aliyu kaji laifukan ka da ake tuhumarka dasu?

Eh naji ranka ya dade.

Hakane koko zaka kare kanka?

A'a

Kallonsa Alkalin yayi sosai sannan yayi rubutu a takardan dake gabansa tsayon lokaci sanan ya dago tare da fadin.

Ina bawa iyayen Aliyu da iyayen Aisha shawara da ku nutsu kusa hankalin ku waje daya ku masu aure, inaga wannan kadai shine mafita, idan hakan be muku ba kuna iya zaban wani kotun domin in juyaku zuwa can, eh mafita amasu aure.

Babu halin mgn acikin kotun dan haka Innawo na fitowa wajen kotun tace, Wlh wlh da Aysha ta aure wannan abun Kara ta mutu yau.

Ummi ma dake gefe cewa tayi, ki kwantar da hankali ki Umma badai Aliyu bane, daga rana me kamar tayau ki rubuta ki ajiye yabar Aysha har abada, nima bana kaunar Aisha kwatan kwacin yadda kike kin Aliyu.

Cikin fara'a Umma tace Alhamdulillah, nayi farin ciki dakin Aisha da kikeyi.

Haka suka dawo gida kowa zuciya babu dadi, suna shiga gida Ummi dakin Aliyu ta nufa, akwatin sa babba ta dauko ta shiga hada kayansa Innawo na tayata, shigowa yayi ya yana kallon su, Ummi ce tace duk wani abuka dakasan yana da mahimmanci ka tattarashi domin komai dare yau zakabar kasar nan.

Ina zani Ummi???

Gurin mahaifin ka zaka koma bazan iya ba.

Ummi karki min haka"

Karka sake min mgn Aliyu wannan tafiyar taka babu fashi.

Runtse ido yayi yayin da hawaye sukai saurin sakkowa kan fuskar sa......

*Yanzun ne zamu shiga cikin LAMARIN*

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

episode 20-21

Innawo da Ummi basubi takan Aliyu ba haka saida suka gama tattara masa kayan sa tsaf, Mayan akwati biyu suka masa sannan Ummi ta kallesa kazo ka duba idan akwai wani abu me mahimmanci naka.

Ficewa Sukayi, yayin da Aliyu yabi bayan su da kallo, share fuskarsa yayi sannan yabi bayan su.

Afalo ya samesu harda Alhaji Umar ahankali ya Isa gurin kafar Ummin sa ya zauna, Ummi dan girman Allah kiyi hakuri, Ummi ki yafe min badan halina ba, wlh Ummi zan shiga cikin wani yanayi.

Cikin daga murya tace, Kai Aliyu?

Na'am Ummi na.

Wlh wlh babu wata kalma dazakai amfani da ita da zaisa najenyi gudurina, matsawar kana son kwanciyar hankalina katashi ka tattara ka wuce tukan dare ya maka. Magiya bazata amfanar dakai komai ba.

Juyawa yayi ya kalli Alhaji Umar, saidai tukan ya bude baki aljaji Umar din yace' " kayi sauri Aliyu zanje na dawo yanzun na sauke ka atasha.

Zuwa yanzun kam ya fahimci bashi da mafita, dan haka ya koma dakin ya dauki duk wani abo nasa me mahimmanci, daga karshe ya daga katifar sa, kudin da Aysha ke bashi ne suka bayyana agurin ahankali yasa hannun sa ya kwasa sannan ya shiga shirya su cikin wata

karamar jaka yana zubawa wadda takardun sa ke ciki sannan ya goyata abayan shi ya zauna bakin katifar tare da daura kansa kan kafar sa.

Aysha ce ta fado masa, ko Yaya zataji idan tasan baya nan?, wani hali Aysha zata shiga idan ta waiga ta kula ayau Nabar garin nan batare Dana mata sallama ba, tana iya yin fushi dani, zata shiga wani hali sosai, da wannan tunanin ya bude kofar nan wadda zata sadashi da tsakar gida ya fice agidan.

Bekobi takan motarsa ba, gani yayi gaba daya yanayin garin ya canza masa, zuciyar sa babu dadi komai na jikin sa zazzabi yake masa, bakin shagon idi ya Isa cikin sanyin jiki ya mika masa hannu suka gaisa yayin da idi yace Allah ya kauta fah.

Ameen Aliyu ya amsa masa dashi sannan yace ai komai ya kare daga yau Nigeria zan koma.

Sosai idi yaji faduwan gaba Nigeria gurin wa?

Ai mahaifina dan Nigeria ne.

Allah sarki, yanzun can zaka koma kwata kwata"

Eh kawai ya iya cewa.

Shiru idi yayi zuwa can yace Amman ko yariyar nan Indo zata shiga wani hali.

Shine nake tunani idi, gashi yanzun nan zan wuce gashi Kuma inason nai sallama da ita.

Shiru idi yayi tsayon lokaci sannan yace zo muje"

Ahankali suke takawa har suka Isa gidan idi yayin daya mishi shinfidan tabarma a tsakar gida tare da fadin, Ina zuwa.

Idi na fita matarsa ta aje ruwa gaban Aliyu ahakali ya mika hannun sa ya dauka, kurba yayi yayin da yaji wani dan sanyi cikin zuciyar sa.

Muyar Ayaha yaji tana sallama cikin sauri ya juya ya kalleta, itama kallon sa tayi yayin da ta danyi murshi sosai tare da aje ledan hannunta kofar dakin tana fadin, mmn Ahmed ga cefanan nan.

Amsa mata tayi daga daki sannan ta karasa kan tabar tana fadin, Yaya me kakeyi anan gidan?

Kawar dakai yayi cikin dakiya irinta maza nazo miki sallama ne Aysha Ummina ta kore ni.

Kallo tabishi dashi yayin da hawaye ya shiga tsiraro mata layi bibbiyu, yanzun Ina zaka Yaya?

Nigeria.

🙄🙄🙄 Nigeria fa kace🙊😭😭

Eh Aysha, Ummi ta koreni, Yaya zanyi?

Yanzun tafiya zakayi ka barni?😭

Yaya zanyi Aysha?, nasan wata rana zandawo kodan sabo da Ummi na.

Kanta ta hada da giuwa ta shiga raira kuka.

Ahankali yace Aysha?, kuka zaki min?, Bakison mu rabu lafiya ne?

Banason katafi ne ya Aliyu.

Nima ba'a son raina bane Ayaha, ni abun da nake so dake dan Allah ki nutsu kiyi karatun ki, Allah ne ya hadamu ba mutum ba, Kuma shine ya kaddari rabuwa adaidai wannan lokacin.

Kuka Aysha take yi hawaye wani na korar wani, ahankali ya mika hannun sa yafara share mata tare da fadin, Aysha kiyi hakuri idan kin tashi aure dazaran ansa miki rana ki rubuta ki aiko min zanzo insha Allahu.

Dagowa tayi da sauri ta kalleshi, hawaye ta share sannan tace ta Yaya zan aiko maka da Sako toh?

Dagowa yayi yasa hannun sa cikin jakar dake bayan sa ya ciro wata takardan ya mikawa Aysha, " Idan kin samu me tafiya Kano Nigeria kirubuta sako sannan kibashi wanna takardan ya duba, wannan shine adireshin gidan mahaifina.

Cikin sauri ta amsa takardan tare da kuresa da ido, yanzun tafiya zakayi?

Zan tafi Aysha, Hannu ta mika ta rike hannun sa daya dafa kanta dashi tace.

Yaya kabani wannan zoben kodan in diga tunawa dakai.

Angama Aysha, sai dai ai yayi miki yawa.

Ina so haka.

Daya hannun sa ya mika yana cire zoben dake dan karamin yatsan sa ya nufi hannun Aysha, gwadawa yaitayi ko a babban yatsanta kinyi yayi dan haka ya mika mata tare da fadin ki adana, mikewa yayi yana fadin sai mun sake haduwa kenan??

Hmmm, a ina zamu hadu Yaya, kace min kawai sai mun hadu a kiyama.😭😭😭🤩

Gabansa ne yaji ya fadi, juyar da kansa yayi can gefe ya cire kwallar idonsa sannan ya juyo yace kisa azuciyarki Allah ne ke kaddara komai ba mutum ba, idan ko har hakane muna iya sake haduwa, shinekenan Ayaha ni zan wuce Ina miki fata alheri.

Shiru Aysha tayi tana wasa da yatsunta yayin da hawayenta ke sauka kan sandar hannunta.

Ganin haka yace bakice komai ba?, nima kimin fatan alheri"

Cikin matsancin kuka tare da share majina tace toni me zance?😭

Kawar dakansa yayi sannan ya juyo yace cewa zakiyi inai maka fatan alheri"

Cikin fashewa da kuka tace inai maka fatan alheri😭😭😭😭

Fashewa tayi da kuka dan haka ya matso ya rungumeta akaron Fargo yana cire kwallar gefen ido, tsayon lakaci tana kwance ajikin sa zuwa can ya dagata tare da fadin yi hakuri, cikin sauri ya juya yabar gidan batare daya waiwayeta ba.

Harya Isa kofar gida yana jiyo ihon ta sosai hankalin sa take atashe runtse idonsa yayi sannan yacigaba da tafiya.

Tuni aka gama zuba kayansa amotar Alhaji Umar duk suna titi jira suke suga ta Ina zai billo.

Ganin sa yasa ahaji Umar ya zaga ya zauna amzaunin sa, yayin da Innawo tace toh Aliko Allah ya tsare, wani irin kallo yaimata me kama da harara sannan ya kalli Ummin da dake kofar gida tsaye yace Ummi zantafi , dan Allah ki yafe min.

Cikin kawar dakai tace ni burina kazauna gurin babanka kawai.

Kad'a Kai yayi ya shige motar yayin da Innawo ke daga masa hannu saidai yaki mayar mata saima dauke kansa da yayi.

Ta kofar gidansu Aysha suka wuce kallo yabi gidan dashi bayan sun wuce gidan ya maida hankalin sa kan titi.

Abangaren Ummi kuwa tunda Aliyu ya wuce take share hawaye, badan tana ganin hakan shine kadai mafita ba bazata iya rabowa dashi ba takaishi inda be saba ba, amman hakan shine kadai mafita dan haka ta shiga damuwa sosai.

Koda Ayaha ta koma gida kuryan gado ta haye yayin da zazzabi me zafi ya rufeta, acikin gidan su babu wadda yasan da tafiyan Aliyu dan haka babu wadda ya zargi komai.

*******

Aliyu acikin motar, Banda tafarfasa babu abun da zuciyarsa ke masa, adaidai wannan lakacin yafi tuna Ummin sa fiye da kowa, acikin zuciyarsa yake fadin, yanxun shikenan nabaro inda Ummi na take, yanzun shikenan a Nigeria zanyi rayuwa, kwalla ya cire tare da kallon hanyar da suke ketawa.

Har dare ya raba suna sharar hanya yadda yaga rana haka yaga dare idonsa ko gezau ba yayin da zuciyar sa ke tafarfasa.

Misalin karfe 10 :12am suka iso Kano Nigeria, fitowa yayi cikin tsananin gajiya da zaman motar, wata motar ya sake dauka wadda zata dauke shi da kayan sa har kofar gidan mahaifin sa, tafe suke yana kallon garin me cike da ababen hawa, kota Ina motocine tare da mutane kota ina.

Sannu ahankali suka shigo cikin unguwar gidagene kake gani wannan na wane waccen masu Dan Karen kau yayin da yake ganin wani gidan tamkar zanashi akayi.

Akofar wani tankasheshen gida yace yayi, tsayawa yayi kamar yadda Aliyu ya dakatar dashi sannan ya sakko ya biyashi ya taya shi sauke kayan sa ya juya ya wuce.

Aliyu ne ya nufu babban gate din gidan ahankali ya shiga kwankwasawa, bugu biyu wani dattijo ya taho ya bude masa.

Kurawa juna ido sukayi, tsayon lokaci sannan ya kauce ya bawa Aliyu hanya.

Wucewa Aliyu yayi ciki tare da barin kayansa waje ganin haka mutumin na ya Kira wasu maza suka shigo da kayan harabar gidan sannan ya kalli Aliyu yace, toh bawan Allah Koda ban sanka ba Naga kamarka da mai gidan, babu laifi asanarwa hajiya xuwan ka?

Daure fuska Aliyu yayi sosai sannan yasa hannun sa duk biyun cikin aljihu yana fadin, " gaya mata"

Toh wa za'a ce mata?

Cikin kawar dakai yace Aliyu daga Cameroon.

Cikin sauri tsohon ya wuce ciki yayin da Aliyu ya kalli harabar gidan, filine sosai da aka kawata shi da shuke shuke na zamani gwanin burgewa, daga can gefe ka wajen adana motoci inda ya hange zafafan motocin guda 6 jere reras, dattijon ne ya maido da hankalin sa gareshi da fadin.

Bismillah.

Akwatunan sa yaga anyi gaba dasu zuwa cikin gidan dan haka yabi bayan su.

'yan mata ne guda biyu suka nufusa aguje cikin fara'a.

Kara tamke fuskarsa yayi dan haka duk sukaje burki daga kokarin fadawa jikin sa suna fadin, " Yaya Haydar sannu da zuwa"

Ahankali ya amsa da yauwa sannan ya karasa kujerar da ke kallon ta wata tattijowa dake zaune yana gaidata cikin daure fuska.

Fuskarta asake babu laifi ta amsa tare da fadin ya Anya?, ya mamanka?

Alhamdulillah lillahi ya fada.

Kallon Yan matan tayi tace, Islam kiraka shi dakinsa ke Kuma Meenat ki Kai masa abinci.

Aliyu agaba Islam nabin sa abaya suna daf da Isa kofar dazata sadashi da dakin yace ke koma.

Momy tace in rakaka dak......

Cikin tsawa yace banso.

Jikintane ya kama rawa daker ta iya mika masa key din tana fadin toh ga key din.

Amsa yayi sannan ya nufa kofar ya bude ya shiga, dakinsa ne dai wadda yasaba sauka saidai yasha gyara fiye da baya da yake zuwa komai an canza ga manya manyan hotunan sa kowanne kusurwa wadda alokacin be wuce shekara 18 ba.

Jakar bayan sa ya sauke kan gado sannan ya nufi toilet, yajima sannan ya fito yana tsane gashin kansa sannun ahankali ya shiga gyara jikinsa, BAyan yasa kaya ya nufi wawakeken gadon sa ya kwanta tare da lumshe ido.

Bude idon yayi yayin da hawaye suka gangaro masa yana me kewan Ummin sa tare da tausayin Aisha. Su biyu ne tsaye cikin ransa  Ummi sai Aysha.

Turo kofar Meent tayi da sallama abakinta tare da kayan abinci, tana kokarin mayar ta kofar ta rufe yace, " ke koma"

Abinci ne Momy tace na kawo ma.....

Banci, fita maza kibani guri.

Juyawa tayi da matukar sauri, jikinta na zuba bari saboda tsawarsa me rugugi.

Juyawa Meenat tayi tanaita abincin kitchen sannan ta fito falon tana cewa, " Aunty Islam abincin ma yace beci"

Momy ce tace, " ku rabu dashi, idan ubanshi ya dawo sa karata, ai kunsan halinsa jarababben yaro ne, sai kubi ahankali idan ba hakaba duk saiyaji muku ciwo kafin ya tafi.

Meenat ce tace, niko da har murna nayi da zuwan shi amman yanzun du guiwata tai sanyi.

****

Misalin 5 na yamma Alhaji Bello ya dawo gida, Jin dirin motar sa Islam da Meenat suka shiga rige rike fita ji kake ridiiii sabo da yadda suke tika gudu"

Cikin sauri Aliyu dake kwance ya sauko ya nufi window yana son ganin dalilin guje gujen nasu tare da iface iface"

Mahaifin sa ya gani tsaye yayin da Meenta tace Baffah albishin ka.

Bude baki yayi da nufin cewa goro Islam tai saurin cewa yayan mu Haydar yazo.

Cikin dan zaro ido Baffah yace SOJA?

Eh Islam ta fada yayin da Meenat tace wlh na rigaki fadi"

Yana matsancin murmushi yace toh ku kwantar da hankalin ku, yanzun dai tukuna SAJO ya iso lafiya?

Lafiya Lau suka hada baki"

Yauwa to duk ku sakeni, yanzun barrin je inga SOJA sai kuzo kowacce ta fada abun da take so.

Aliyu kuwa tunda yaga Baffah ne sukeyiwa wannan tsallen yaja tsaki sannan ya koma

ya kwanta rigingine tare da daukan sandan hannun sa ya kare idon sa dashi.

Cike da fara'a Baffah ya shigo dakin, tare da sallama abakin sa.

Kasa kasa Aliyu ya amsa yayin da Baffah ya iso dafdashi ya zauna.

Kallon yanayin sa kawai yayi ya gane kamar yana cikin damuwa.

Hankali yace, SOJA?

Batare daya bude idon sa ba yace sannu Baffah.

Hannu Baffah ya mika ya cire hannun Aliyu afuskarsa yayin da hawayen dayake tarewa suka zobo.

Subuhanallahi, SOJA mene ke faruwa?

Wani hawayen ne ya sake zubo masa kamar an bude famfo daker yace, " Baffah Ummi ce ta koro ni.

Lumshe ido Alhaji Bello yayi tare da fadin, " yayi kau, Ummin ka ta kauta min, dama kyawun d'a gidan ubanshi.

Ganin har yanzun Aliyu na zubar da hawaye yace, " meka mata"?

Kasa mgn Aliyu yayi hawaye ne kawai kebi masa fuska wani na korar wani.

Hannu Baffah ya tura acikin gashin kan Aliyu, cikin sigan lallashi yace, kamin mgn Mana, ko kana son in kira su Islam da Meenat suzo suga katon yayansu SOJA yana kuka?

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

episode 22- 24

Cikin sauri ya girgiza kansa tare dasa hannun sa ya share hawayen sa

Inajin ka.

Bakomai Baffah

A'a, akwai SOJA.

Babu Baffah kawai tagaji da ganina ne.

Ba gaskiya bane Soja, duk yadda akayi Kaine baka da gaskiya.

Hawaye ne suka sake zubo masa yayin da mahaifin nasa yabishi da kallo tare da fadin, " shikenan, koma dai menene bakomai, kai nawa ne, Ina tsananin farin ciki da zuwan ka, na dade Ina jiran irin wannan ranar gashi ayau tazo min, tuni naso ka dawo nan amman amman aka nuna min fin karfi, saigashi yau da taku ta hado ku ta koro min Kai, duk da haka naji dadi, Kaine dan da nafara haifa dan haka nake alfari da kai. Hajiya ma kullum cikin mgnr ka take, kareke mgnr yayi yana share ragowan kwalar dake idon Aliyu yana me cigaba da fadin kayi wanka?

Nayi.

Abinci fah?, Kaci?

Ni Baffah banjin yinwu.

Jimmm, Baffah yayi sannan yace zo muju to masallaci.

Mikewa Aliyu yayi ya nufi toilet, ya wanko fuskarsa tare da dauro alwala, shima Abba nan ya shiga yayi alwala sannan suka fito.

Kusa da juna sukayi sallah yayin da Baffah yakejin tsananin farin ciki, a yau gashi ga Haydar. bayan sunyi sallah isha'i gidan Hajiya suka wuce wato mahaifiyar Alhaji Bello, ganin Aliyu sosai gidan ya dauki farin ciki musamnan da sukaji cewa gaba daya ya dawo, sosai Hajiya

ta shiga farin ciki, sai anan gidan Aliyu yasa wani abu acikin sa.

Sai misalin 10 na dare suka dawo gida afalon yabar Baffah ya nufi ciki.

Ahaji sai yanzun nake ganin ka?

Murmushi yayi kadan tare da fadin, kinsan dai inada bako yau, munje wajen Hajiya ta ganshi takuma San da zuwan shi.

Amman Alhaji harka shigo gidan nan ka Kuma juya ka fita abinka, toh bakomai Nima nayi farin ciki da zuwan shi, kannen sama sunata murna, amman na kula shi da d'aci yazo, kareke mgnr tayi tana yatsuna fuska.

Sauke ajiyan zuciya yayi sanan yace, babu wani daci da yaxo dashi, kawai dai Ina tunanin anbata mishi raine dan yace ma bazai koma ba.

Bazai koma ba?, anan zai zauna?

Eh, alhajin ya fada yana kawar dakai yayin da Momy tace ai shikenan, to karatun sa fah"?

Anan zaiyi insha Allahu, kinsa nagaya miki yana da burin yazama Soja tun yana yaro uwar ce bata so, insha Allahu yanzun zancika mishi burin sa, zan nuna masa kulawata wadda be sameshi ba abaya ba.

Yayi kau Momy ta fada tare da Kara fadin yamaki cin abinci.

Eh, yaci gidan Hajiya.

Yayi kyau ta sake fadi tare da nufar dakinta cikin tarin takaici.

********

Tun washegari ranar Baffah ya fara nemawa Aliyu makaranta, domin yana ganin Aliyu yariga daya girma, lokaci dada kurewa yake, sosai yai bakin cikin barin sa tun farko a Cameroon domin danan yake tun farko da yanzun karatun sa yayi nisa. Yanzun Kashi kusan an bata lokaci ne kawai. dan haka dole ya mike, cikin ikon Allah cikin sati biyu yasamu masa gurbin a babban makarantar horaswa dake Kaduna, yayin da aka shiga shirye shiyen tafiya, watan Aliyu daya da sati biyu ya wuce Kaduna, cikin rakiyar Baffah da kannen sa Meenat da Islam, wadda har yau be saba dasu ba yaki sakin jikin sa dasu, Kuma har ya wuce makarantar baya baccin kirki kullum tunanin Ummin da da Aysha shine makale cikin zuciyar sa.

******

Cameroon

Aysha ce zaune adakin Umma, zoben Aliyu ta dauko ta zura a babban ya tsarta ganin yana shirin fadowa ta yamutsa fuska tare da fadin yaushe zan girma?, yau kwana ya Aliyu dari biyu da sittin da bakwai amman har yau zoben nan bemin daidai ba😬 mikewa tayi ta nufi wata jakar Umma, wani bakin zare ta dauko ta dawo ta zauna, warware zaren tafara tare da nadawa zoben cikin kokarin yiwa zoben ciko, yi take tana gwadawa a babban yatsanta hartaga ya zauna sosai sannan ta maida zaren.

Mikewa tayi ta fito ta hada wanke wanke, Umma dake zaune agefe ta kalli Mama tace, kinga Aysha tunda Ali yabar kasar nan muka samu kanta, duk nukufarcin ta gama shi da wani zazzabi zazzabi da wani zama shiru duk angamashi.

Mamace tace ai lokacin nan nafirgita sosai da lamarin su, ance ya koma can kenan bazai dawo ba.

Kallon Ayaha Umma tayi tana fadin, aini iyayen sa sun biyani, dangin su sun burgeni da suka korashi, su o'i Kuma dole asaki jiki.

Cike da haushi Aysha ta kalli Umma tace, ai yace idan zanyi aure hardai yasani zaizo😏😏

Dariya Umma tayi sosai tana fadin, aifa sai zaizo din, Ashe ya janye soyayar tasa da yake dake?

Cike da tsiwa Aysha tace to daman yace miki sona yake ne, ni betaba min irin wannan mgnr ba, karatu kawai muke in dawo gida.

Karya kike muna fuka Umma tafada tana nuna Aysha da yatsarta.

Ji  Ummar nan, wlh ni harma kinban haushi, yaya Aliyun ne zaice yana Sona? babba ne fah, nikuma karama.

Mamace tace ke maza kiyi kitashi banson surutun banza, dake ake mgnr ne?

Cikin zunbura baki ta karasa ta tashi tana me fakar idon mama tana hararan Umma.

Gidan Innawo kuwa tunda Aliyu ya tafi hankali ya kwanta, ayanzun Umma da Innawo suna gaisawa cikin mutunci, idan sun hadu cikin layin kamar basu taba wani rigima ba, gidan juna ne dai basu shiga saida wani dalili na rashin lafiya ko jaje, sabanin sauran makota da suke iya shi domin zumuncin mukotaka.

Ahankali kwanaki suke juyawa zuwa watanni watanni najuyawa shekaru Aysha na Kara tsayo, amman tunanin Aliyu akoda yaushe yana makale cikin zuciyarta, shekaran Aliyu biyu da tafiya ta ware zaren data nadawa zoben ta, saboda natsarta da yayi, zama yayi dass a babban Dan yatsan ta, murmushi tayi tana zubawa zoben azufan kallo har ranta takejin sanyi idan ta kalli zoben.

Ayanzun shekarun Aysha 16 dan haka alamomin girma duk sun bayyana ajikinta, kasancewarta yar gayu yar kwalisa tuni samari suka fara kawo mata hari, sai dai koda wasa Aysha vata kula kuwa, karatunta kawai take yayin da har yanzun Aliyu na nan karkashin zuciyar ta, duk wani wadda zaice yana sonta yanzun balakin haushi yake bata, sannan duk wani lokacin da zatai tunanin irin zabinta daya take son aura suffan Aliyu kawai take gani.

Haka shima Aliyu anasa bangaren ya kasa goge Aysha cikin ransa, yayin da yakeji abun nason canza salo daga kanwa ko kawa yana son komawa soyayya, domin dayayi tunanin macen da ya keson aura Aysha ce ke zuwar masa inda yake kimanta matakin girmanta ayanzun.

Sosai ya Kara girma da cika, yayin da fatarsa ta Kara murjewa, bashi da matsalan kudi akoda yaushe Baffah cikin turo masa da kudi yake, sosai girma ya kama shi horon da suke karfa yasashi ya Kara budewa  yana sheki ga wani gasumba daya tara wadda akoda yaushe cikin gyara shi yake.

Sosai 'yan mata ke kokarin shige masa saidai ko kallo yariya bata isheshi ba bare har yayi mgn da ita, duk da cewa yana kallon yadda sauran abokan karatun sa  suke tara mata suna sauke bukatarsu akan su amman hakan beta sa yaji wai shima bari ya nema ba, duk kuwa dacewa jikinsa yana tabbatar masa da cewa yana bukatar abokiyar raguwa, shi kansa yasan ya girma.

Bayan shekara Uku

Duk iya inda ake son cikar budurwa Aysha takai, sosai wani farin ciki ke lillube Umma idan ta kalli yadda Aysha take da cikar halitta kirjinta cike yake tab da dukiya, yayin data kasance yariyar yar kwalisa wadda ta hada ilimin addini Dana boko, sosai uwa da uba ke alfari da Aysha domin ta hadu iya haduwa, Aysha irin matan nan ne wadda duk inda suka gifta sai an waiga bama ga namijiba har mace saboda wani irin kyawu da Allah ya bata.

Tuni manyan mutane suka fara kawo mata hari, yaran manyan mutane masuji da kansu ne ke zuwa nemanta amma da sunzo sau daya basu Kara dawowa koma mutum ya dawo ba kulashi take ba.

Awannan lokacin Aysha tana da shekara 19 wadda hakan yayi daidai da shekara 5 da tafiyan Aliyu, Kuma awannan lokacin ne ta kare makarantar secondary, ranarce kuma ta cire

zoben Aliyu daga babban yatsar ta maidashi kusa da dan karamin ya tsanta.

Har yanzun zanen fuskar Aliyu nanan acikin idonta, Kuma yanzun ne ta fahimci tana son Aliyu.

Itako Umma ayanzun ko tuna Aliyu batai hakama mamah ayanzun burin su be wuce Aysha tai aure ba.

Abangaren Aliyu kuwa shekaran sa daya da gama karatun sa wadda yayi shi na tsayon shekara 4 ya fito a matsayin BSc Security and Intelligence Science, Aliyu kenan banban yaro meji da takama wadda akafi sani da *(BS) Aliyu Moh'd Bello* saboda jajircewan sa kan aikin sa yayi suna sosai, kwarewarsa dabawa aikin sa mahimmanci. Be fiye zama agida ba Koda yaushe yana kan aikin sa dan haka be cika samun lokacin kansa ba.

Shekaransa daya kenan da fara aiki, saidai wani babban al'amari kulum Aysha Kara shiga ransa take, acikin idon sa yake kimanta girmanta ayanzun yayin da duk inda yaji an Kira Aysha saiya waiga.

******

Baffah?

Na'am Islam

Wai ya sunan Ummi na gaskiya?

Wacce Ummin? Baffah ya tambaya bayan ya tsare Islam da ido.

Ummin Cameroon.

Murmushi Baffah yayi sannan yace sunanta Fatima.

Toh Baffah wace Aysha?

Meenat ce tace, " Eh Baffah dan Allah wacece Aysha?

Aisha kuma?, bansanta ba meyasa kuke tambaya?

Islam ce tace Baffah kasan dai Yaya Haydar baya dariya ko?, Baffah mgn ma bayi yake ba, Amman sau biyu Ina shiga motar sa zamu gidan Hajiya wlh har muje mu dawo bin wakar Aysha yake yi"

Jimmm Baffah yayi zuwa can yace Sojan ne ke waka?, Karake mgnr yayi cikin fashewa da

dariya.

Meenat ce tace wlh Baffah, toh yana son sunan Aysha Idan yanabi har mantawa yake damu amotar kaji yana bi kasa kasa nina dauka ma sunan Ummi ne

Dariya Baffah ya sakeyi yayin da Momy tadan yi murmusa tare da fadin Kila budurwar sa ce.

Baffa ne yace Anya kuwa wannan son girman shi zai barshi ya nemi budurwa?, Inaga fa saidai a nemo wata amanna masa.

*****

Ayanzun Aliyu ya gama tabatar da cewa Aysha yake so, kullum ya zauna bashi da wani tunani daya wuce nata, fuskarta yake tunuwa tana wasa da yatsunta kamar yadda ta saba, murmushi yayi ko yanzun Yaya take? Allah sarki Aysha🥰 yariya me hankali, yariya me nutsuwa ga kunya ba irin yanmatan nan ba, Aysha me sanyin hali, yariya me ilimi da son nemansa Koda yaushe, afili yace yazama lallai inje inga Aysha, Ina tsananin son ganin ki.

Cameroon

Mama kinsan dai na dade banji ba, dan haka wallahi idan naje sai kun ganni.

A'a Aysha karki zauna, tunda kinki sauraron kowa toh kawai kice masa ya nema miki makaranta kafin Allah ya kawo mijin, duk kin ki da aure idan mijin ki yazo dole zakiyi, Umma ke fadin haka tana kallon Ayaha.

Ke Umma badamar afarq mgn saikice aure, komai aure, wlh natsana inji ance auren ma.

Baki Umma takama tare da fadin waike Aysha kanki kalau kuwa?, to ko lafiya ce bata ishe ki ba?, Dan ubanki aure ne ya samar dake idan baki sani ba.

Cikin tsiwa Aysha tace to waike Umma idan auren dadi garai me ya hanaki yi?

Mamace ta kawo ma Aysha duka, yayin da Ayahar tai saurin kaucewa.

Umma kuwa fadi take rabo da ita babu ruwanki, juyawa tayi gurin Aysha tana fadin, dan kasararki kifarawa uwarki fada dan tafini yarinta.

Dariya Aysha tayi sannan ta faki idon mama taiwa Umma gwalo.

Mikewa Ayaha tayi yayin data gyara mayafin dake ganta zuwa wuyanta kadai ta suka nufi baya hadon bayanta, riga da siket ne ajikinta na yadi me taushi, sosai suka matse ta gyaleta kuwa daidai wuyanta kawai ya tsaya, tsugunawa tayi ta dauki akwatin ta tace toh natafi.

Adawo lafiya mama tace tana binta da kallo tare da fadin ki gaidashi.

Cikin dan sanyin jiki kadan tace zaiji, Umma kema natafi.

Toh ki gaida Uban naki.

Jimmm ta tsaya tare da fadin, Umma wannan ai zagi ne, Nifa tafiya zanyi kimin addu'a

Matsoraciya, tafiya da intayi yawa awa daya kike kira tafiya, toh shikenan Allah ya tsare hanya.

Akwatinta ta fara jah harta fito kofar gida tana waiwayen gidan , ta kofar gidan su Aliyu ta wuce kallon gidan taitayi hartai nisa, tana Isa bakin titi ta tare mota tahau cikin harcen fullacin tace Tasha zaka kaini.

Cikin kankanin lokaci suka iso, motocine birjik ga matafiya kowa na azama,  wasu ta tambaya dan Allah Ina motar Kano Nigeria. Batare da bata lokaci ba aka nuna mata, yayin da ta taras mutun daya suke jira, shiga tayi tare da sauke ajiyan zuciya, kudin motar ta kirga tabada kamar yadda aka gaya mata sannan motar ta tashi batare da wani bata lokaci ba........

Toh ga Aysha ta shiga motar Kano Nigeria, Kar me karatu ya manta, Aysha ba bahaushiya bace, batajin hausa kwata kwata kozo in kasheka bata sani ba, daga fulatanci sai French take ita ji, wannan shine mafarin komai

*🕳BA'KAR FURA🕳*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

episode 25- 26

Tafe suke cikin motar tana kallon hanya, tunda take bata taba biyo irin wannan hanyar ba, iya tafiyanta me nisa gidan Daddy yau gata tana keta dajuka.

Tun tana ganin tafiyar me sauki ce harta fara tunanin kodai duniyar za'a bari, duk kokarinta na kada tai bacci cikin motar saida tai bacci me tsayo ta tashi, wani mutmi dake kusa da ita ta tambaya har yanzun ba'a kawo ba??

Ke yariya ai ba'ama soma tafiya ba, baki taba zuwa bane halan?

Eh kam wannan ne zuwana nafarko.

Toh ki shirya zama, akwai zama agaban mu.

Ya mutsa fuska tayi sannan tace da driver inajin fitsari.

Muryan wata mata daga bayanta taji tana fadin ke yariya daure mu Isa masallaci.

Waigawa tayi ta kalli matar tare da fadin ankusa ne?

Eh yanzun zamu Isa.

Bayan kusan tafiyan minti 27 suka Isa masallacin, yayin da Aysha tafice da sauri daman abakin kofar take domin itace takarshen shiga motar.

Masallaci ne Babba, wadda yake awajen gari, da alama masallacin kusam Dan matafiya akayi shi, waddan aharabar masallaci akwai masu abubuwan siyarwa nama tsire lemo ta sauran abubuwan motsa baki.

Cikin toilet din da aka samar domin mata ta shiga zuwa can tafito taga wasu har sun fara al'wala, itama wata butar ta dauka tayi alwala sannan ta shiga cikin masallacin, sai yanzun ta

tuna bata dauko hijjabin sallanta ba, gyalene kawai ajikinta wadda ya kasance karami ne sosai wadda be wuce adaurasa akai ba, kuma ko cikin kayanta duk irin sune. Dan haka dole tajira wannan matar ta idar da sallar sannan tace , " mama dan Allah aramim hijab inyi sallah.

Cirewa tayi ta mika mata, sannan ta zauna agefe, Bayan Aysha tayi sallah ta bawa matar hijjabin tare da gyara mayafinta.

Atare suka fito da matar wadda ya kasance su kadai ne mata acikin motar, hannunta matar ta rike suna tafe take matsa hannun Aysha tana fadin Yaya sunan ki?, Cikin harcen filatanci take mata wannan tambayar.

Sunana Aysha.

Ina zakije?, Ina nufin wajenwa zakije Nigeria?

Jimmm, Aysha tayi zuwa can tace wajen Babana zanje.

Babanki, Ina mahaifiyar ki fa?

Mahaifiya ta muna tare da ita anan Cameroon Babana Kuma dan Nigeria ne"

Cikin gamsuwa matar tace nafahimta, Amman meyasa ba'a hadoki da wani babba ba akabarki ke daya.

Ni kadaice agidan, kakata Kuma tsohowace mamanace take kula da ita.

Allah sarki, nagane, amman duk da haka naga gangancin su, kasancewarki yariya budurwa yakamata da wani babba atare dake, Amman insha Allahu Allah zai tsareki.

Insha Allahu Mama.

Kallon ta Mama ta sakeyi tare da fadin gaki kyakyawa dake, son kowa kin wadda ya rasa, ko in inyiwa dana kamo ne?

Murmushi Aysha tayi tare da sunkuyar da kanta kasa tana wasa da yatsun ta.

Matar ce ta sake cewa, ko kina da wadda kike so ne?, Ina da yaro na Babba in Zaki soshi?

Murmushi Aysha ta kumayiwa Mama kanta akasa.

Mama ma dariya tayi tare da cewa, Ina baki kunya ko?, Da haka suka Isa gurin motar yayin da matar ta roki mutumin dake kusa da ita ya dawo gurin Aysha domin Aysha ta dawo kusa da

ita.

Be musa masu ba ya basu guri suka dawo kusa da juna.

Hanya aka sake dauka tsayon lokaci suna keta hanya yayin da Aysha ta gaji da zama sosai.

Tun tana ganin abun kamar wasa har taga dare ya raba, sosai hankalinta ya Kara tashi, tun gurin 9:00am tafito, cikin firgice ta kalli Mama tare da fadin Mama ahanya zamu kwana ne?

Eh Mana Aysha Idan Allah ya taimake mu gobe da rana zamu Isa idan Kuma mun samu tsaiko har jibi muna iya kawai.

Wayyo Allah na mama kafata duk ta sake.

Daure diyata. Insha Allahu gobe war haka kina gidan mahaifinki kina hutawa.

Daren nan Ayaha bata iya runtsawa ba yadda taga rana haka taga dare, washegari Misalin 3:30pm Aysha ta sauka a garin Kano, sosai gabanta ya shiga faduwa yayin da wani shashin nazuciyarta ke mata fada anya kuwa hakan ya dace, sosai jikinta yai sanyi hankalin ta ya tashi har mama take tattare kayanta ta kula da hakan kallonta tayi tace, " Aysha ya dai?"

Bakomai mama.

Jimm tayi sannan mama tace motar Ina Zaki hau?

Akwatinta ta nufa ta bude sannan ta ciro wata farar takarda tace sunan unguwa yana rubuce anan.

Wani irin kallo Mama taiwa Aysha sannan tace amman dai iyayen ki suna da ganganci. mika Hannu tayi ta amsa takardan ta bude. dagowa tayi ta sake kallon Ayaha cikin yamutsa fuska tace, Inazuwa, driver daya sauke su ta nufa ta nuna masa takardan, sakkowa yayi ya yana rike da takardan yace ta dauko kayanta ga mota can asata.

Daukan Akwatin Aysha tayi yayin da mama tabita abaya har suka Isa cikin motar, shiga Aysha tayi ta zauna yayin da driver yake ke gaya masa sunan unguwar wannan lokacin bata sanin me mutumin yace dan bata san wani yare bane.

Takardan ta karba sannan Mama ta juya taiwa Aysha sallama tare da Kara gargadinta cewa takula da kanta.

Kwallah Aysha ta share domin Jin mama take tamkar mahaifiyarta sabo da yadda ta nuna kulawanta agareta, hawaye ne ya shiga ziraro mata yayin da can kasan zuciyarta takejin

kamar batawa iyayenta adalci ba, saidai data tuna yadda take balakin son ganin Aliyu saitaji zuciyarta na dada dakewa.

Nan ma tafiya akayi da ita sosai sannan mutumin ya juyo yace, "har yanzun ba'a kawo ba?"

Kai Aysha ta daga masa domin ta fahimci tambaya yayi amman bata iya sanin me yace mata.

Tafiya yayi me nisa sannan ya tsaya ya bude motar yana fadin sakko Hajiya, nan gurin shine karshe.

Cikin rashin fahimta ta yamutsa fuska cikin kokarin sakkowa tana me kallon garin tare dayin kwal kwal da idonta, hawaye ke shirin zubo mata.

Motar ya mayar ya rufe sannan ya zagaya ya shiga motar yana fadin, da Alama yariyar nan batajin Hausa.

Tausayi tabashi dan haka ya kirata da hannun sa yace Ina Zaki ne?

Cikin fullacin tai mgnr dan haka ya yamutsa fuska tare da fadin toh fah, sakkowa yayi ya nufi wasu maza dake zaune ya basu hannun suka gaisa sannan yace yariya ce na dauko tundazon da alama batasan garin ba Kuma batajin Hausa ko akwai bafulatani anan?

Bafulatana ce?

Amsa masu yayi da eh sannan ya daga Hannu ya Kira Aysha.

Tahowa tayi ta tsaya gabansu, daya daga cikin sune yace ke ya sunan ki???

Fulacin dai ta sake masu cikin takaici dayan yace ke bamejin fullanci anan gurin sunan ki akace, Yaya sunan ki??

Wannan karon tafara tsorata dasu domin ta fahimci cikin fada sukayi mgn.

Daya daga cikin sune yace, duk yadda akayi irin yaran nan ne masu guduwa daga gidan iyayen su, ke bakijin wani yaren ne sai fulatanci kadai?

Kaita daga dumin iya fahimtarta tambaya sukayi, fada mutanan sukaci gaba dayi yayin da Aysha ta tsaya idonta jawur.

Dayan ne ya kula da takardan dake hannunta batare data ankara ba ya amsa takardan ya bude.

Dagowa yayi ya kalli sauran tare da fadin, Ina tunanin wannan shine adireshin inda zata ke yariya wannan shine adireshin inda Zaki??

Kaita daga yayin da daya daga cikin mutanen yace ita kome zakace mata ai amsa maka zatayi ai daman fulani ba hankali suka cika ba🤪 inba hakama kya taso bakisan gariba Kuma baki da hausa.

Daya daga cikin su ne dai ya sake cewa yanxun abun da za'ayi ka taimaka ka kaita Dan kunma baro unguwar abaya, Kuma indai da gaske wannan shine adireshin to takwana gidan sauki, taimakawa zakayi ka kaita har gidan tunda akwai no gidan ajiki.

Eh to bance bazani ba, amman ni gaskiya sana'a nafito, idan tana da kudin da zata biyani har da bata lokacina toh zan kaita.

Toh babu laifi, kallon Aysha sukayi kina da kudi??

Raba ido kawai Aysha keyi dan haka suka shiga mata kurma kurma suna nunawa da hannun su.

Hannun tasa cikin akwatin ta dauko cajin da aka bata.

Gaskiya baxani awannan kudin ba.

Nan dai suka lallabe shi akan idan sunje acika masa kudin sa agidan, haka akayi Aysha ta shiga motar sannan suka dauki hanya.

*******

Sai yau ka tuna Dani agarin nan Aliyu?, Shekaran ka nawa yanzun, tunda naje akace min kana nan neke zarya gidan ku, Amman kullum nazo ace kana makarantanta, haba Aliyu?

Aini ban masan kinsan ina nan ba, Kuma ita Ummin da ta gaya miki ba itace ta koroni ba?

Ai Kai kajawo komai, idan bata koreka Yaya zatai dakai.

Eh shine Nima ai nakoma gefe.

Gara taka koma gefen, yanxun ma dakasani ai bakazo ba, wato sai abarka kayi abun da kaga dama.

Daure fuska Aliyu yayi sosai yana zaune falon Hajiya Rukayya cikin kakin sojojin sa fuskar nan tasa kirtim, lumshe ido yayi sannan yace, Ina Yaya Fahat?

Yana wankacan dakin ta numa masa da hannunta.

Kallon dakin yayi sannan yasake cewa ya jikin sa fah?

Jiki Alhamdulillah.

Amman akwai wani cigaba??

Toh Alhamdulillah yana nan dai a yadda yake.

Har cikin ransa yaji ba dadi mikewa yayi yana kokarin nufar dakin Aunty Ruqayya tace, " yaushe zaka je gida?"

Yanzun Yaya Fahat kawai zan gani na wuce"

Can gida nake nufi gurin Ummi"

Dan waigowa yayi ya kalleta sannan yace Aunty itafa ta koreni, ni bazani ba sai in ita ta nemeni, haka tace min ita burin ta in zauna gidan ubana.

Mikewa Anuty tayi tabi bayansa cikin dariya take fadin, dan auta sunyi fada da Ummi, bafa ason ranta bane.

Nima ai ba ason raina bane, da haka suka Isa dakin fahat, cikin wani irin farin ciki fahat din yake kallon Aliyu domin rabon su da juna sun dade sosai.

Zama yayi gefen sa yana me kura masa ido ko kiftawa babu, idon Aliyu cike da kwallah ya kama hannun sa yana fadin, Yaya Fahat nine Aliyu, Yaya kake?, Ya jikin ka?

Bude baki yake cikin kokarin amsawa da irin mgnr sa wadda ba'a ganewa sosai.

Hawaye ne ya zubowa Aliyu cikin sauri ya kawar da kansa ya share sannan yasa hannun sa cikin aljihu ya ciro kudi yasa a hannun fahat yana fadin, gashi inji Ummi tace na kawo maka.

Amsa yayi da murna akan fuskarsa, mikewa Aliyu yayi yana fadin barin je ai muna tare zan dawo kaji.

Amsawa yayi,yayin da Aliyu da aunty Rukayya suka fito har motar sa, BAyan ya shiga ya zauna ta kalleshi tace, " Auta an girma, to yaushe zakayi aure?, gaka yadda kai katoto kuwa, dan Allah kaje Ummi ta ganka.

Hmmmm,  aunty yaushe rabon ki da can?

Sakera biyu, amman nakusa komawa.

Tada motar yayi tare da fadin, idan kinje ki gaishe ta, amman Banda innawo.

Cikin dariya tace ita Kuma Innawo meta maka?

Itace nan ta zuga Ummi, tada motar yayi batare yajira me aunty zatace ba.

******

Ana Kiran sallan magarib suka iso kofar gidan kallon Ayaha yayi ya mika mata takardan tare da numa mata cewa wannan bayanin nata ya nuna wannan ne gidan dan haka ki shiga ki amso min cikon kudina.

Ganin kamar bata gane ba yai mata kamar mgnr kurame har saida yaga ta daga Kai sannan ya zauna saman motar tare da fadin ina nan.

Itako Aysha gidan ta nufa duk da cewa girman gidan yabata mamaki cikin dar dar ta shiga bugawa.......

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

Comment BA'KAR FURA *Sumayya Magaji*
*Tabdijam gsky yakamata iyaye sudauki darasi anan koba komai wani lokacin iyaye sukan dinga tsanantama yaransu akan abinda baikai yakawoba su aganinsu tarbiyace suke koya musu kuma yaro yanada wani Abu dik abinda yaga ana tsananta mishi akai koda abin baije yadawoba tofa shiyake qoqarin aikatawa aikatawa, Wanda aganina dik abinda zaman lpy baikawo ba to tabbas tashin hankali bazai taba kawoshiba, tin farko inda iyayinsu sunbi abin ahankali dayanxu hkn batafaru ba, yanxu wagari yawaya idan har iyayin Aisha suka sami Ibrn tagudo har Nigeria wajan Aliyu?*🤦🏿‍♀️

*Sann ko Yara wani lokacin danasu laifin iyaye fa sunfi qarfin wasa duniya daka rasa iyaye baxaka taba samun wasuba kuma dik abinda mukaga iyayen mu sukeyi mana bawai Dan basu sonmu bane Aa kwe dae sunayi ne dansuga sunkare martabar mu d mutuncin mu sann kuma susauke nauyin da ubangiji yadora musu.*
Kowa ya aikata daidai ba shakka zaiga daidai ammh dae wann yaxama ixina awurin iyaye kai harma damu yaransu💁🏼‍♀️

*Tin ba'aje ko inaba wann Ibrn yafara bayyana irin darasin da yake dauki dashi,*
*Ubangiji Allah kabamu ikon yiwa iyayin mu biyayya adukkan wani abu dasuka doramu akai muddin baisaba maka👏🏻*

*Ya Allah kasa mugama d iyayin mu Ipy👏🏻*
*Wadan da iyayinsu suka rigamu gidan gsky Allah yagafarta musu yayi musu rahama Amin ya rabbi*👏🏻

*Sis @Fadeela Lamido muna gdy sosai Allah yaqara basira da daukaka yasa kifi hk yashirya miki zuri'arki👏🏻🥰*

episode 27- 29

Kwankwasawa take ahankali cikin sanyin jiki, daga can taji an fara bude gidan.

Me gadine ya leko ya kalli Aysha tare da fadin Yaya dai?

Cikin fullacin tayi mgn wadda baya fahimtan koma sai Aliyu da take Kira.

Cikin tsananin mamaki yace Aliyu?, Iya sanin sa dai Aliyu ko mgn ba cika yinta yayi ba, tsareta da ido yayi, neman sa kike Aliyun?, tunawa da yayi fulacin takeji yasashi yace, Aliyu baya nan.

Wannan mutumin daya kawo Aysha ne ya matso yana faddin, waishin baka fahimci sunan wadda take Kira bane? Ko banan gidan yake ba?

Eh toh anan madai Akwai Aliyu amman Ina tunanin ba wadda take nema bane.

A'a Sam nan ne, gashinan Zane hannun ta, wannan yariyar bakuwa ce ba yar garibace tun da sauran rana nake yawo da ita acikin motar nan, yanzun dai bude mata ta shiga ta amso min kudina.

Gurin wa?

Aliyu take Kira Kuma Aliyu baya nan.

Toh ai saika bude mata kofar ta shiga ta jirashi ko, nadade Ina yawo da yariyar nan ba inda zani da ita kuma.

Tsaki Me gadin yayi sannan ya juya rufe gidan.

Cikin wani irin yanayi Aysha ta juyo ta tsuguna akasa saboda yadda kafarta tagaji, ga tarin yunwa a tattare da ita.

Ganin garin yayi duhu ta fara hawaye gaba daya cikinta ciwo yake mata ga wani masifar fiya yunwa da yake ji.

Mutumin ko na nan zaune sai masifa yake yayin da Aysha ta tsuguna a gefe tana share hawaye.

Wata katuwar mota ce ta shigo layin, yayin da duk hankalin su ya karkata kanta ahankali harta karaso gurin su, nan suka fahimci gidan zata shiga dan haka suka kauce.

Gate din gidan aka bude yayin da motar tasa hancin ta cikin gidan.

Fitowa Aliyu yayi daga cikin motar da saurin sa domin gani yake kamar Aysha ce awaje, idan kuwa ba Aysha bace lallai suna tsananin kama.

Yana daf da shiga gidan me gadin ke fadin, " ranka ya dade, akwai wata bafulatana tazo batajin Hausa amman tana Kiran sunan ka.

Aliyu bebi takansa ba yayi waje cikin tsananin mamaki yake binta da kallo yayin da itama tai saurin mikewa ta da tsareshi da ido.

Aysha?, Aysha kece anan ba gixo idona yake min ba???

Kwalkwal tayi da ido har yanzun tana kallon sa, gani take kamar bashi ba, sosai ya canza mata yayi wani irin kato ya tara kasumba ga Kuma kayan sojojin ajikin sa.

Kara matsawa yayi daf da ita tare da dafa kafadonta yana fadin, kimin mgn Mana inji muryan ki kece haka??

Fadawa tayi jikinshi cikin fashewa da kuka, yayin dayai saurin rungumeta tsayon lokaci sannan ya fara dan dukan bayanta tare da cewa ya Isa ya Isa cikin harcen fullacin.

Mutumin dake zaune ne saman motar yace taxo gari ita ba hausa ba tun dazon nake bulaye da ita agarin nan, tasan batajin ko wanni yare mezaisa tazo n........

Cikin sauri Aliyu ya dago Aysha daga jikinsa sannan ya juya ya kalli mutumin yana fadin, " Kai me kake jira??

Cikin furgici da tsawan da ya masa yace a'a ni cikon kudina za'a bani.

Hannun yasa  a aljhu ya ciro kudin dabesan ko nawa bane ya mika masa.

Cikin sauri mutumin yabar unguwar yayin da Aliyu ya tattara hankalin shi gaba daya gun Aysha yana fadin kedawa Aysha?, yaya akayi har kikazo nan?

Wasa da hannunta take cikin sunkuyar da kanta tsayon lokaci.

Kallonta yayi sannan yai murmushi tare da cewa, " har yanzun dai ana nan ba'abar wasa da hannun ba?, Juyawa yayi ya kalli akwatin ta sannan ya sake cewa inajin ki kedawa kikaxo nan??

Batare data dago ta kalleshi ba tace ni kadai.

Cikin sauri ya zaro ido, ke kadai????

Har yanzun idonta akasa tace eh.

Shiru yayi tsayon lokaci yana kallonta, tsarguwa tayi da kalon dan haka ta Kara saukar da idonta kasa kafin taji yana fadin.

Aysha ashe baki da hankali?, ina nan ina yabon halayen ki, yanzun ke kadai kika kamo hanya toh agida ansan kin taho?

Kanta ta girgi alanar a'a

Ina kikace masu Zaki?

Muryanta can kasa tace gidan babana.

Shiru ya sakeyi tsayon lokaci sannan ya sake cewa, amman dai baki da hankali Ayaha ta Yaya zaki baro gida babu izinin kowa kina da hankali kenan?, kina tunanin idan suka lura baki can wani irin tashn hankali zasu shiga?

Wasa take da hannunta yayin da hawaye ya fara sauka akan kumatun ta.

Cikin tsareta da ido ya sake cewa Aysha kina son mukara shiga cikin wata matsala ko?

Girgiza kanta tayi da sauri yayin data share hawaye tare da saurin tsugunawa ta dauki akwatin ta ta juya afusace ta fara tafiya.

Kallo yabita dashi zuwa can yace Ina Zaki???

Tafiya kawai take dan haka ya sake cewa zonan.

Ganin tacigaba da tafiya ya sashi daga murya tare da fadin, " Aysha kinaji nace ki dawo ko?

Ganin har yanzun tafiya take yasashi yabi bayanta, abuka da namiji nan danan yacin

mata, akwatin ya karba sannan yace juya muje, Ina miki mgn kina tafiya,, yanzun bada bane saina miki duka, wuce muje.

Juya tayi kamar yadda yace, yana gaba da akwatin ta ahannun sa yayin da take binsa abaya tana share hawaye.

Har cikin gidan suka shiga yayin daya doshi wani babban kofa da akwatinta ahannun, duk da cewa ma'aikata nata miko hannu yana girgiza kai.

Cikin wani katun falo suka bayyana yayin da taji ya ya bude murya yana Kiran Meenat.

******

Dirowa Meenat tayi daga gado, tana zare ido tare da kallon Islam tana fadin nashiga Uku, kamar Yaya Haydar ne ke kira na, ko Baffah ne??

A'a kamar dai Yaya Haydar din ne.

Cikin zaro ido Meenat tace bantabajin ya Kira sunana ba, kefa Islam yana Kiran sunan ki??

Kafin tabada amsa suka sakejin wani Kiran wannan karon duk su biyun ya Kira Meenat Islam"

Kusan atare suka amsa tare da saurin fitowa.

Akwatin ya mikawa Islam dake gaba sannan ya kauce Aysha ta bayyana yana fadin, ga bakuwa, kuje da ita dakin ku tai wanka taci abinci.

Amsawa sukayi, yayin da ya kalli Aysha yace ki bisu, kiyi wanka kici abinci.

Wucewa tayi kawai kamar yadda yace binta yayi da kallo har yanzun fushi take dan haka yadanyi murmushi sannan yace nayi farin ciki da zuwan ki, cikin harcen fullacin.

Juyowa tayi tadan mai wani irin kallo wadda yasa shi ya sake sakin murmushi.

*********

Misalin 09:30pm Islam ta shigo tace muje Yaya na Kiran ki.

Wanni irin kallo taiwa islam cikin rashin fahimta.

Suna ko mgn taita mata ganin dai taki ganewa ta fito zuwa falon Haydar tana fadin, Yaya

inata mgn bata kulani.

Lumshe ido yayi tare da fadin bata jinki ne ki kamo hannunta kawai.

Ai har kamo hannun nata nayi taki.

Kawar da kansa yayi yai murmushi sannan ya juya yace, " kin iya french"

Meenat dai tanayi kadan kadan.

Kice mata tai mata french zata amsa ta.

Juyawa Islam tayi zuwa can saika Meenat da Ayaha, Aysha na shigowa Meenat ta fice, kallo yaitabin Aysha dashi tsayon lakaci.

Itako zama tayi ta juyo masa baya tsayon lakaci yana kallon bayanta, zuwa can ya mike ya dawo kusa da ita yana fadin"

Har yanzun kina fushi?, Aysha dan namiki fada kike fushi, har yanzun kina nan da halin ki ko?

Hawaye ta fara sharewa can kasa da murya tace bakayi murna da ganina ba.

Inji waye ya gaye ya gaya miki?, Nayi farin ciki da ganin ki fiye da yadda kikai farin ciki da ganina Aysha, nafi son ace nine nabiki ba kece kika biyoni ba, sabo da darajarki ta 'ya mace, ni namiji ne dan nabiki ba wani abu bane, yanzun me kike tunani idan Kakarki ta fahimci haka??

Shiru Aysha tayi kwalla tap idonta.

Cigaba yayi da cewa nayi farin ciki da ganin ki, kin girma Aysha, amman farincin bashi zai hana nagaya miki gaskiya ba, Ina son kisani cewa meson ka shine yake gaya maka gaskiya, kin rigani kamo hanya ne kawai amman har yanzun kina zuciyata, yanzun mubar wannan mgnr Ina Ummi na?, Kina ganin ta?

Batare data kalleshi ba tace muna haduwa a hanya.

Innawo fah?

Itama haka.

Har yanzun baki shiga gidan??

Kaita daga.

Baki Zaki bude inji muryan ki.

Ahankali tace ban sake shiga ba.

Wani irin kallo yake mata na kasan ido, cikn ransa yake yaba hallitan ta, Allah yayi mata sura me kyau, da daukan hankali, tayi wankan ta, ta canja kaya, sai dai suma irin dinkin dazon din ne duk sun kamata, dan karamin gyalene kawai tasa akanta ko dan kwali babu sai bakin sumsrta yake hangowa yana kyalli

Kallonta da yayi na tsayon lokaci sosai ya saukar mishi da kasala irin wadda be tabajin taba, cikin ransa ya raya inama ace matarsa ce ta aure suke zaune tare adaidai wannan lokacin, idon sa ya sake kaiwa kan kirjinta ganin su cike tam yasashi saurin lasan leben sa batare daya shirya ba, cikin ransa yake Kara tabbatarwa lallai Aysha itace matar daya dace ya aura, duk da cewa abaya ba soyayya sukayi ba, amman yanzun ya tabbatarwa kansa cewa yana son Aysha, haka itama ya tabbatar soyayya ce ta kawota wadda ada suke gani kamar kauna ce.

Acikin ransa yaci gaba da cewa, yanzun haka take yawo a Cameroon, nonuna luntsum lumtsum, kawar da kansa yayi zuwa can ya juyo idon sa cike da kishi yace"

Samarin ki nawa?

Juyowa tayi ta kalleshi, can kasa tace, "da yawa"

Da yawa ko?, har kina saurin fada?, ai daman nasan zasuyi yawa, tunda kina yawo ahaka, kin gim katuwa dake kina yawo Kai ba dan kwali Koda dama can haka kike, baki damu da suturta jikin ki ba, anan bazan yadda da wannan ba.

Cikin sauri ta sake juyo mishi baya akaro na biyu.

Mikewa yayi ya dawo gabanta tare da mika hannun sa ya roko nata, yatsunta ya rike yana murzawa, karon farko arayuwar sa daya hakan taro dan haka yai saurin lumshe ido tare da sauke ajiyan zuciya.

Ahankali yake murza hannun ta wadda zoben sa yake Kai, cikin matsanancin farin ciki yace, " Aysha kin hadu, kin nuna min kauna, bazan taba mantawa dake ba arayuta, kina da kirki Ayaha kina da nutsuwa ga kamon Kai, gakuma tarin ilimi, tunda muka rabo nake tunanin ki, ban iya mgn da kowacce mace ba saike Aysha, nayi zamana ne kawai saboda Ummi ta nuna zamana anan shine farin cikin ta, nasan Ummi tana son in rabo dake kamar yadda yan gidan ku keson ki rabo Dani, Kuma haryau bandenajin abun da nakeji akanki ba kullum karuwama yakeyi, dan haka naki dawowa kawai.

Hawaye Aysha ta share da hannunta daya cikin kasa da murya tace nima wlh Yaya ban daina ba, Umma nata fada bana kula kuwa nikadai nasan abun da nakeji.

Hada kansa yayi dana Aysha yace nina fahimta Aysha, yanzun muyi tunani kina ganin zamuyi aure?, iyayen mu zasu bari kuwa?

Kawar da kanta tayi ta share hawaye tana fadin bansani ba Yaya Aliyu😭😭

Lumshe idon sa yayi sannan ya bude tare da share mata hawayen yana fadin, kidaina kuka, insha Allahu zamuyi aure, Allah ne ya daura mana kaunar juna batare da yayi shawara damu ba. Da yardan sa zamuyi aure insha Allahu dan ni Ina tunanin indai ban sameki ba bazanyi aure ba, kefa Aysha zakiyi aure ki barni??

Kukane ya kwacewa Aysha dan haka tai saurin fadawa jikin sa, saurin rungumeta yayi tsam ajikin sa tayon lokaci sannan ya shiga lallashinta daker ya iya yakeceta ajikinsa domin ji yake kamar su dauwama ahaka.

Kije ki kwanta Aysha dare yayi. hannunta ya riko ya kaita har bakin dakin su Meenat saida yaga shiganta sannan ya juya zuwa dakin sa.

Gado ya fada, yayin da yakejin tamkar Aysha ta fama masa ciwon dake karkashin zuciyar sa, wani irin masifar sonta yakeji yana bin duk wani sassan jikin sa, wadda yakejin tamkar idan aka hanasa aurenta zai iya mutuwa, gawani irin masifar tausayin Ayshan daya saukar masa, ganin irin yadda ta sadaukar da rayuwarta takamo hanya, jikawai take ayanzun bashi da wani babban buri daya wuce yaga ya mallaketa, tsintan kansa yayi da zubar da hawaye dan yasan akwai babban aiki agaban sa, bayaga haka yau daya da ya hada jikinsa dana Ayaha duk yana jinsa abirkice dan haka ya kwanta kawai yai rufda ciki yana cire kwallar dake taruwa gefen idon sa.

****

Washegari da Safe, Aliyu ne zaune gaban Baffah yayin da Momy take gefen  Baffah.

Cikin daure fuska Baffa ke fadin.

Kasan dai Ina da mutuncina ko?, Mutane suna ganina da daraja, nayi nayi dakai kayi aure kaki, Ina lallabaka dan banson in takura maka, ko na hanaka aure ne??

Leben na kasa ya lasa sannan yace a'a.

Toh akan me zaka dinga lebo yaran mutane kana kawo min cikin gida?

Momy Aliyu ya kalla sannan yace wacce yariya na kawo?

Baffah ne yace ni zaka kalla ka tambaya yariya da kazo da ita jiya, ina ka samota ko hausa bataji......

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

episode 30- 31

Dagowa yayi cike da kwarin guiwa yace Baffah matar aure ce ita, wannan yariyar tana da aurenta, matar abokinace daga Cameroon suke, ita da Mijinta, tafiya ce takamashi zuwa garin dabesan Ina zai sauka ba, gshi anan din ma batasan kowa ba, asalima bata hausa, shine ya nemi da in kawota gidan mu ta zauna nawani lokaci kafin ya dawo, cikin baccin rai ya sake cewa inda nemanta nake ai bazan kawota gidanmu ba, Kuma cikin kannaina Baffah, nadauka cewar Ina da damar da zankawo wadda naso.

Ajiyan zuciya Baffah yayi, cike da gamsuwa yace, " nafahimta Haydar, kana da damar shigo da duk wadda kaso kuwa domin gidan mahaifin kane, saidai inaga ba laifi bane  dan naga kamar zaka karkace natuhume ka, Kuma bayani yana da dadi, dole ne hankalina ya tashi ace yau na samu labarin ka sauki mace bana miji ba, batare da wani bayani ba, ya dace ace da abokin ka ya kawo matarsa ka kawoshi mugaisa, sannan ka sanar Mana cewa zaibar matarsa anan, kamar yadda kai bayani yanzun, dan haka nan gaba ka gyara wannan kuskure ne.

Kansa akasa ya amsa da toh yayin da Baffah yace wane sunan yariyar??

Muryan Aliyu adakushe yace, " Sunanta Humaira"

Allah sarki, toh Allah ya dawo da mijin nata lafiya.

Dakai ya amsa sannan ya mike yayi sallama ya wuce Office.

Ajiyan zuciya yaketa saukewa ajijjere, wani na korar wani, yayin da yake bakin cikin turkeshin da Baffah yayi tabbas yasan Momy ce ta zogoshi dan haka yaji abun nakara bata masa rai, kenan dan iska suka maidani, irin wannan tunanin yaita yi yayin da yakejin ransa na dada baci.

*******

Aisha zaune kusa da Islam, waige kawai Aysha take yau bataga Aliyu ba, hankalinta ne ya fara tashi sai raba ido take, tun safe take sarai da ganin sa, gashi yanzun har sha daya, cikin ranta ta fara tunanin gida Mama Umma acen bangaren Kuma ga Daddy ta duk tabarosu ta tahonan da kudin data dade tana tarawa gashi yanzun har yanzun bataga Aliyu ba, wata zuciyar ce tace mata yanzun idan  be dawo ba fah Yaya zakiyi, ki koma gida?, hawaye taji ya zubo mata sharrr, Hannu tasa ta share sannan tace duk acikin ranta, idan kin samu kudin motar Ina zakibi kihau motar? kinsan hanyar tashan ? Me zakicewa masu mutar?, yin wannan tunanin hawaye ya fara ziraro mata babu kaukautawa, Meenat ce ta kula tabajin kukanta kasa kasa waigawa tayi ta kalleta cikin mamaki tace da Islam kuka take🤔

Juyowa Islam tayi ta kalleta tare da tafata tana fadin kiyi hakuri baiwar Allah.

Meenat kuwa fadi take menene?

Islam ce tace ai kinsan baji take ba French Zaki mata.

Akace miki wani iyawa nayi?, ni bansan yadda zan lallasheta ba.

Islam ce ta saki bayan ta koma bakin gado ta zauna tana fadin, mudai mun shiga uku, ya hadamu da aiki ya wuce aiki abun sa, ni wlh abun nan haushi yake bani, ace kaita mgn da mutum besan me kake cewa ba.

Ayaha ko shashekar kuka take taree da Kiran sunan Aliyu, sunan kawai suke iya fahimta.

Meenat ce tace niman ya Haydar fa take bakijin tana cewa Aliyu ba, Islam kice mata yaje aiki anjima zai dawo.

Cike da fada Islam tace ke meya hana kice mata, gaki kusa da ita.

Ai bajina take ba, Meenat ta bata amsa.

Mikewa Islam tayi tana fadin, toh ni Jim nawa take ne?, Kofa ta nufa tana fadin wlh ni dakin Momy zanje inyi bacci na.

Dan Allah karki tafi kibarni da ita, bansan ya zanyi ba, ficewa Islam tayi, yayin da Meenat ta kalli Aysha sannan itama ta fice adakin.

Gun Momy suka Isa kallon su haka yasa tace Yaya dai?

Momy kuka fa take, tana fulani ni bangane me take cewa in Banda Kiran ya Haydar.

Aiki ya sameku, saiku koma ku lallasheta Kar abokin Mijinta ya dawo yaci ubanku, dan nikam karma kununa nasani, gara daku Niko idan ya wullo min wannan idon nasa, ba dai mgn zaiyi ba amman akwai kallon raini.

Batare da sun fahimci inda tasa gaba Islam tace, " Wlh Momy bazamu iya ba, nidai gaskiya nagaji.

Cikin sigan lallashi Momy tace kunga kuje ku zauna adakin, ko bakuce mata komai ba yafi dai ace an barta ita kadai.

Da haka ta lalabesu suka koma.

Misalin karfe 4:30 Aliyu ya dawo gida, masifar kosawa yayi ya dawo sabo da Aysha kawai, yana tunanin ko Yaya ta kwana, kawai ya iya daurewa ya barta ne dan Kar a fahimci akwai wani abu a tsakanin su.

Kai tsaye dakin sa ya wuce bayan yama Momy dake falo sannu, cikin sauri sauri ya shiga wanka, fitowa yayi yana tsane ruwan dake kansa, sannan ya shiga shiryawa, kananan kaya yasa tare da fesa turare, kokarin fita yake yaga Aysha idonta a kunbure.

Murmushi yayi idonsa cikin nata, yana me tsareta da ido sosai yace ya dai naga kamar kinci kuka kin koshi"

Kawar dakai tayi cikin sunkuyar da kanta kasa.

Meya faru ne?, nidai nasan Aysha jaruma ce an zanaki ma idon ki be kun bura haka ba, gaya min waye ya bata miki rai.

Lumshe ido tayi hawaye suka zobo ahankali tace tunani nayi.

Motsowa yayi daf da ita yana fadin, " tunanin me?

Ka barni anan bani da kudin komawa gida, Kuma gashi bansan haryar da zanbi in samu hanyar gida ba.

Dariya sosai Aliyu yayi yana kallon cikin idon ta, hannun sa ya mika ya dafa kafadanta ahankali yake turata da baya har suka Isa kujera ya zaunar da ita sanan ya zauna agaban ta, kinaji Aysha?, ki kwantar da hankalin ki, ni bazan gudu in barki ba, kuma Zaki koma gida cikin kwanciyar hankali inaha Allahu bazaki wahala ba, Ina son muyi hira sosai, sai dai kin San me??

A'a

Baffah na dazon yayi min mgn akan ki, kacenwar basu sanki ba bakuma Susan komai daga gareki ba.

Kallo ta tsare Aliyu dashi tsayon lokaci sosai ya fahimci tashin hankali a tattare da Aisha.

Bude baki tayi cikin shirin yin kuka yayin da Aliyu yai saurin daga mata Hannu tare da fadin, " a'a karki tada hankalin ki, nagaya masu ke matar abokina ce, tafiyar gaggawa ta kamashi ya bukacin ki zauna anan, dan haka daga yanzun ke matar abokina ce.

Sunkuyar dakai Aisha tayi har yanzun fuskarta babu sukuni, ido Aliyu yabita dashi sosai ya gama fahimtar ta sannan ya cire hannun sa daga kafadanta ya ruko habarta yana fadin, " karki damu kinji ko, wannan ba wani abu bane, bason su fahimci komai game dake, har na kaiki gida sannan na neme auren ki.

Kwallah ta share, har yanzun zuciyarta babu nutsuwa gata ga Aliyu amman kwanciyar hankali babu.

Tunanin me kike Aysha?

Hawaye ta sake sharewa akaro na biyu tare da fadin, ya Aliyu na damu sosai, inajin wani iri acan hankalina ba akwance ba anan ma hankalina be kwanta ba.

Toh meyasa?, Bana son ki koma gida kinajin haka, inason kiji dadi sosai, Ina son ki kasance cikin farin ciki domin hakan ne zaisa ki koma da walwala, Nima in tunaki inyi murmushi, Amman idan kika koma gida kina cikin wannan halin zuciyata zata kasa nutsuwa, yanzun kinsan me nake so dake?

Kaita girgiza yayin da Aliyu ya mika hannun sa yana kokarin share hawaye yake fadin, "  ke mata aure ce Aysha karki yadda wani ya gane cewa baki da aure, nace haka ne badan Ina tsoroba sai gudun Kar abun da ya faru abaya ya sake faruwa, Ina son na maidake gida sanan in

Kuma daukoki alokacin da kowa ya shaida nine mamallakin ki.

Sosai taji zuciyarta tai sanyin har ta sauke ajiyan zuciya.

Murmushi yayi tare da fadin ko kefa.

Itama murmushi tayi kadan tare da turi hannun sa daya rike habarta dashi, cikin sauri ya dauke hannun nasa yana fadin, " yi hakuri, na mance kin girma dauka nake dace.

Wani irin kallo ta masa wadda yasashi ya kumayin murmushi, amman naga kinyi sanyi da yawa bakiyin wannan darigar take dake Dani murmushi.

Yaya toh ai Kaine baka bani dariyar.

Shikenan, naji, ki shirya gobe idan na dawo aiki zan fita dake musha hira, kibani Ibrn Cameroon.

Amsawa tayi da toh.

Juyawa yayi ya dauko ledan dake bayansa ya mika mata, tare da fadin, wannan Hijjab ne Ina son ki rika sasu.

Godiya tayi sannan ta mike ta tai masa sallama.

*****

Ina zashi da ita Kuma?, amman sun matukar dacewa wlh, duk da cewa cikin nikaf take amman abun ya dace.

Babu ruwana ki, ki daina mgnr sa, kinsan halin sa saikiga kamar ba kallon ki yake ba amman duk yadda bakin ki ya motsa yasan me kike nufi.

Kara kintse hakora Islam tayi tana fadin, daka nace sun dace, gani nayi tayi kamar matar shi, gashi Kuma yace matar abokin sa ce, Kuma wlh ki waiga ahankali ki kalli wani kallon love da yake mata.

Kallon so?, matar abokina sa ce fah?

Nidai Naga ya Aliyu soja ne, Kuma bashi da aure bashi da mata, baya zama gari daya, abokai kala kala, 'yan mata kala kala, karuwai burjik, Kuma wlh daganin ya Haydar ba kanwan lasa bane nan dai gidan ne yake mana mazurai.

Cikin sauri Meenat ta kalli Islam tace me kike nufi?

Bance komai ba, nidai fatana Allah yasa kada ranar da abokin nasa zaidawo daukan matar sa ya tarar ya fita masa yawo da mata.

Lumshe ido Meenat tayi, sannan tace toh Ameen.

******

Tunda suka shigo babban gate din sojoji kawai take iya gani maza da mata, wasu na tafiya wasu na zaune wasu ko sintiri suke yi, wannan ya tabbatar mata da cewa waje ne da aka tanada domin sojoji, ahankali ta fara hango gidajen da bishiyoyi suka masu kawanya, wani abun mamaki, duk inda Aliyu ya ratso Sara masa ake, duk da cewa yana cikin motar da aka rufe gilashin ta.

Gidaje ne irin na sojoji, tafiya sukayi me nisa sannan ya tsaya, bude masa motar akayi ya fita sannan ya zagaya ya budewa Aisha, bayan ta fito rufewa yayi sannan ya shiga gaba tana binsa abaya.

Awani yalwa tattacen falo suka bayyana wadda yai matukar burge Aysha.

Ganin ya doshi wani daki ta zauna afalon, juyowa yayi ya kalleta sannan yace Ina zuwa.

Zaman kusan minti 39 tayi sannan ya fito yana sanye cikin wadon sojoji da farar riga.
Kallo
Kallon sa tayi sosai, sannan tayi murmushi.

Ahankali ya iso kusa da ita, yana fadin, ko baki fada ba nasan kina kallo nane sabo da Kinga nakara kyau, fiye da lakacin da Ina Can Cameroon.

Bawani, kana nan yadda kake, tsufa kawai ka Kara.

Tunkarota yayi gadan gadan yana fadin, kice Allah.

Mikewa tayi da sauri tana toshe bakinta yayin da Aliyun yace, Me kike nufi??

Dariya ce ta kamata, ganin inda ya hade ransa yana tunkaro ta"

Ahankali take komawa da baya harta Isa kofar tana fadin babu komai.

Kina nufin har yanzun Ina nan a baki na ban washe ba???

Dariya ta sake sawa, ganin yana dada tunkarota ta bude kofar ta tai waje aguje.

Wani irin dariya yayi har zuciyar sa tare da sauke ajiyan zuciya me karfi sannan ya fito cikin kokarin boye murmushim sa.

Babu kowa afarfajiyar da bishiyoyi suka zagaye, daga can gefe ana iya hango sajoji nata zirga zirga sai dai babu ruwan wani da wani.

Ahankali yake takawa zuwa inda take tare dajin dadin yanayin sosai cikin ransa.

Runtse ido tayi tunda ta hango tahowan sa tare da dago hannunta cikin nuna alamar karya taba ta cikin dariya take kare jikinta da hannunta duk biyu.

Tsaye yayi agabanta sannan yai saurin mamayanta ya cukuikuyi hijjabin ta cak yai sama da ita tare da fadin muje kimin bayani........ Pls kubi wannan link din ku dannan min subscribe tare da alamar kararrawa

https://youtu.be/3pYo_wvEN0M

*🕳BA'KAR FURA🕳*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍

https://youtu.be/ebcYnNjGbOI

episode 32- 33

Ganin yayi sama da ita fara fadin, " Ya Aliyu sauke ni wasane nake maka.

Cikin falon ya nufa da ita yana cikuikuye da hijjabinta, Aysha ko dariya take cikin wuntsula kafarta take rokon sa ya sauke ta tare da magiya.

Bisa kujere dake falon ya sauketa, sannan ya zame yasa guiyoyin sa akasa har yanzun yana rike da ita, hadiye murmushim sa yayi kina nufin har yanzun din dai abakin nake?

A'a Ya Aliyu yanzun kam kadan washe.

Nadan washe?, Aliyu ya tambaya yana tsare Aisha da idon sa.

Eh Mana ka Kara haske kadan.

Jimmmmm, yayi zuwa cen ya lumshe ido lokaci daya ya bude su tare da fadin, " toh naji ni baki ne, ahaka Kuma aka kanni ake Sona.

Murmushi Aysha tayi waye keson naka?

Mikewa yayi ya zauna daf da ita yana fadin wadda ya tsargu.

Hannunta ta mika ahankali ta Kara da hannun sa yayin da yai saurin janye nashi, dariya Aysha tayi Yaya nifa wasa nake maka fari ne Kai tasss.

Bawani, kinsan me??

A'a

Tsoro nake karmuyi aure mu dinga haihuwar bakaken yara.

Dariya Aysha ta Kuma sawa, yayin da Aliyu ya daure kamar ba shine yai mgnr ba, cikin kallon idon sa tace toh meye?, Yaya Aliyu kaifa ba baki bane, Kaine kake bani dariya da nafahimci baka son ace maka baki, bakin ka me kyau ne, kana da fari hasken fatane baka dashi Kuma kamafi kyau ahakan.

Lumshe ido yayi na kaiki?

Kama fini Yaya fa.

Haba?

Allah.

Ninasan duk wayoni kike min, nasan ke zarah ce acikin taurari, kina da kyau Aysha, tun kina karamar ki, yanzun ko da kika girma kin Kara kyau sosai, ni yanzun ma burina in ga na mallake ki, Aisha tunda naganki akaro na biyun nan naji na matsu inyi aure, kallon cikin idonta yayi sannan yace, ko kema kinajin irin wannan abun?

Cikin sauri ta sunkuyar da kanta kasa nidai kawai nasan namatsu ingan ka Kuma dana ganka naji dadi.

Ki ganni kawai shikenan?, Auren fah?

Cikin kukan shagwaba ta juya baya tare da fadin, " ni kabar wannan mgnr"

Shiru yayi idon sa akan nata tsayon lokaci sannan yace, " kina nufin baki damu da auren ba koko dai kinajin kunyata ne?

Yaya ni abar wannan mgnr.

Baza abarta ba, sai nayi, baki son muyi aure?

Ni intani a zauna ahaka.

Bangane azauna ahaka ba?, gaya min me kike nufi?, baki son aure?

Ni Yaya kabar mgnr nan muyi hirak kawai.

Ke!!, Karki Raina min hankali, an gama hiran sure nake so ni.

Toh ya Aliyu ai auren lokaci ne.

Kallonta yayi sosai sannan yace, eh lokaci ne, amman ya kusa zuwa me wayau kawai, kinajin kunyana nasani, daman kin saki jikin ki danni aure nake so nan kusa.

Can kasa kasa tace Kaine ka dade bakayi ba.

Sarai yajita amman sai yace me kika ce?

Nace ya kamata ace kayi tuni.

Kece kika hanani ai.

Ni Kuma Yaya?

Eh kece Amman komai ya kusa insha Allahu.

Jimmm tayi tsoyon lakaci sannan tace nifa banaji ajikina su Umma zasu bari muyi aure.

Lumshe ido yayi tsayon lokaci tare da wani irin faduwan gaba, ahankali ya ware idon sa, karki Kara irin wannan mgr nan.

Ganin inda ya shiga wani irin yanayi tabishi da kallo kawai  kansa ya dafa tsayon lokaci be gado ba ganin haka Aysha tace, yaya mene haka?

Dagowa yayi yana me sauke ajiyan zuciya tare da fadin, yanzun idan naje neman auren ki akaki bani Yaya zamuyi toh?

Ya Aliyu Ummi zata yadda ka aure ni ne?

Tunani ya Kara shiga me zurfi yayin da ya waiga yaga Aysha na share hawaye.

Ahankali ya mika hannun sa ya jawota jikin sa, kwanciya tayi akan faffadan kirjin sa kamar yadda ya bukata, hijjabinta ya tattaro ya cireshi tare da ajewa agefe sannan ya sake kwantar da ita akirjin sa yana mejin wani irin farin ciki da nutsuwa me wuyar misaltawa.

Lumshe idon sa yayi yana shinshinan gashin kanta dake fitar da kanshi me sanyi, hannun sa daya yasa yana buga bayanta cikin sigar lallashi.

Saidai shi ana shi banganren yanajin wani abu sosai game da ita yana yawo ajikin sa, itako Aysha jinta jikin Aliyu taji takara samun nutsuwa.

Wani abun mamaki daya daure kan Aysha akaron farko ta tsinci Aliyu na sumbatar ta kota Ina batare data ankara ba, shima Aliyu akwai Alamun ba acikin hayyacin sa yake ba, ajiyan zuciya ta fara saki a jejjere wani na korar wani,  kasa hana sa tayi yayin da yake kai mata sumbatar tsigar jikinta na tashi sosai.

Sosai Aisha ta gigice, harta rasa abin yi, bata taba shiga cikin irin wannan yanayin ba, babu wanna ya taba rike Koda hannunta bare yakai bakinsa gareta, jitayi Aliyu yana Kara gaba, domin ayanzun kokarin tura hannun sa cikin rigarta yake dan haka tai saurin mikewa.

Hijjab dinta ta dauka tana daga tsaye, cikin runannun idanun sa yake binta da kallo Yayin da Aysha ta kasa hada ido dashi.

Kallo yake binta dashi ko cire ido baya yi,   idon Aysha akasa tafara kokarin maida hijjabin ta.

Hannu taga ya miko mata yana kokarin amsa Hijjab din,

Mika masa tayi sai dai har yanzun taki yadda su hada ido, domin balakin nauyin sa  takeji, ko ada tasan yafi karfinta kota Ina bare yanzun daya Kara girma, babu wadda zai kallesa yace bashi da iyali agida, ga wani kasumba daya tara wadda kesa take ganin kwarjinin sa fiye da baya.

Amsa yayi idonsa akanta sanna yai wurgi dashi kan kujera.

Juyowa yayi ya kalleta sannan yace xo nan.

Cikin sanyin jiki ta karaso gaban shi yayin dayasa hannun sa ya jawota jikin shi ya rungumeta tsam, tsayon lokaci sannan ya sunbaci kumatun ta tare da saurin sakinta.

Da saurin sa ya juya dakin yaki bari su hada ido da Aysha.

Bayan sa Aysha tabi da kallo jikinta asanyaye bayan taga ya kule ta koma ta zauna, hijjabin ta ta dauka ta rike ahannunta hawaye taji sun zobo mata tai saurin sharewa, hanyar dakin taita kallo tsayon lokaci Amman ko motsin Aliyu babu.

Gajiya tayi da zama tun tana sa rai da fitowan sa harta fara cire tammani, sallah mangariba dataji anayi shine ya kara tayar mata hankali ganin har an tada sallah Aliyu be futo ba.

Wani irin fitsari takeji amman dole take matsewa domin batasan kan gidan ba, saida aka Kira sallah insha'i Aliyu ya fito, kansa tsaye ya nufi kofar da zata sada shi da waje yana fadin barin sallah muje in kaiki gida.

Ko iya amsawa batayi ba, cikin sauri ta nufi dakin da ya fito fitsari tayi sannan tayo al'awala ta dawo falon tai sallah.

Tana cikin sallah taji shigowansa, akujerar dake bayanta ya zauna, tana idarwa yace, " Zaki iya kwana anan?

Cikin sauri tace a'a.

Jimmm yayi zuwa can yace, Naga dare yayi ne dawai ki kwana anan dasafe saina maidaki gida.

Cikin rashin fahimta tace ni daya?

Eh.

Cikin sauri ta mike tare da nufar kofa tana gyara hijjabin ta take fadin, nidai gaskiya tafiya zanyi, ta Yaya zan kwana anan ni daya.

Duk da cewa yana cikin wani damuwa Amman dariya ce ta kamashi ba tare daya shirya ba, mikewa yayi yana bin bayanta cikin dariya yake fadin yanzun da kika fito nan Ina Zaki?, Idan nayi zama na anan Yaya zakiyi?

Tafiya zantayi Ina kuka inta Kiran sunan ka wlh.

Dariya yayi  darene fah Aysha waye zai kula ki ma bare har yagane kince Aliyu, baki tunanin wani abu ma ya sameki a hanya?, Yanzun da kizauna tare dani gara kita tafiya a titi?

A'a aikai cewa kayi ni daya zaka bari, haka kurin kafarni cikin daji ni daya kadangaru su danne ni.

Dariya ya sake yi adaidai lokacin da suka Isa kofar motar sa, kofar ya bude ma Aysha ta shiga ta zauna shima ya zagaya ya shiga.

Akofar gate dinsu ya sauke ta yana fadin, kishiga barin je na dawo yanzun.

Amsawa tayi da to sannan ta shiga gidan, cikin fara'a su Islam suka taryeta duk da cewa sun San ba Jin su take ba.

Ganin Aysha ita kadai yasa su tunanin Kila unguwa ya kaita shikuma ya wuce wani gurin.

Misalin karfe 10pm ya dawo gida gurin Baffah kawai yaje suka taba hira sannan ya wuce part din sa.

Tundaga wannan rana duk bayan kwana biyu Aliyu ke fita da Aysha zuwa wannan gidan cikin sirri babu wadda ya sani, zaton su unguwa yake kaita.

Aysha da Aliyu sun Kara shakuwa sosai, yawan fitan da suke ke Kara masu tsananin shakuwa, kulawa sosai Aliyu ke bata, tare da nuna ko kuda baya son ya tabata, ayanzun ne suke Jin tamkar ma dacen basu San komai ba, soyayya me zafi ta rike su wadda duk rana da basu haduba basa Jin dadi.

Sai dai yawancin duk ranar da ta kasance sun hado da Aysha ranar Aliyu na kwana ne

bashi da lafiya, sosai yake daurewa Dan karta gane halin da yake ciki, awannan gidan sukeyin wasa tare da Aliyu domin idan yana tare da Aysha komawa yake kamar wani karamin yaro. Kai bakace shine me daurewa kannin su fuska ba, yawan wasan da suke yasa har Aysha ta kwasa tsayon wata biyu da sati biyu batare da sun farga ba.

Yauma kamar kullum Aliyu ne da Aysha kan hanyar su ta dawowa gida, Aliyu ne ya kalli Aysha yace, ya kamata ki fara koyon hausa.

Inaso sosai Ya Aliyu su Islam sun fara koya min Ina dan fahimta dai dai bana iya mayarwa.

Lumshe ido yayi, ni ya dace in koya miki ai ko bani bane malamin ki?

Kaine yaya, amman yanzun aikai baka da lokaci suma zasu koya min.

Bancika son shiga harkar yaran nan ba domin naga kansu kamar yana rawa.

Kansu be rawa Yaya, suna da kirki sosai wlh suna min kirki, ji dani suke sosai.

A lallai, tunda sunaji dake nima zanji dasu.

*****

Bayan sun koma gida part dinsa ya wuce yayin da Aysha ta wuce gurin su Islam kamar yadda ta saba.

Misalin karfe 9 nadare Aliyu ne zaune gaban Baffan sa cikin bacin rai Baffah ke fadin, " tun kafin su gama secondary School nabasu zabi aure ko karatu, bakin su na rawa sukace min karatu, akan me yanzun zasu dinka taramin maza acikin gida saikace gidan caca.

Baffah kayi hakuri zan gansu ni bantaba gani ba Kuma bansan cewa haka na faruwa ba.

Ai bazasuyi kana nan ba, kasa ido akan su sosai inkaga sun shigo min da nimiji gida ka taka yariya.

Cike da kwarin guiwa Aliyu ya amsa sannan ya Kara bawa Baffan sa hakuri ya fice.

Afalon ya same su har Aysha, tsintan kansa yayi dason zama agurin, abun da be taba ba yau shi yake shirin yi, zama yayi a babban falon gidan ya daura kafa daya kan daya.

Ganin inda su Meenat duk suka firgice kowacce ta kasa nutsuwa ya shiga fadin, " naji abun da kukeyi, idan auren kuke so sai ku aje karatun bazai yuwu kuna tara mana maza acikin gida ba.

Sosai cikin su ya duri ruwa, yayin da gabansu ya shiga faduwa.

Islam ce tai karfin halin ce masa, bafa samari mu bane, yaran kawar Momy ne suka kawo mata......

Ke!! Ina wasa dake ne??, Aliyu ya fada cike da mazurai.

A'a yaya Haydar.

Na miki mgn ne dan kibani amsa ko kuwa?

A'a

Shikenan, gaba dayan ku karku daina, zaku gane koni wanene ranar da naga wani acikin gidan nan, ba ruwana da bagurina bane gurin islam, a'a gurin Meenat yazo, bare Kuma kucemin gurin momy, saina fasa bakin yariya.

Duk mgnr da suke bajin su take ba, ta fahimci dai fada yake masu dan haka tace cikin harcen filatanci, Ya Aliyu ka barsu haka mana.

Cikin sauri ya daga mata Hannu tare da canza harce daga hausa zuwa filatanci yace, " zan hada dake, banson ki Kara saka bakin ki.

Kallon sa tayi sannan ta lumshe ido tare da komawa ta ta kalli can gefe, tanajin sa ya cigaba da bala'i saida ya gaji Dan kansa sannan yai shiru tare da Satan kallon Ayaha

Kin kallon sa tayi tsayon lakaci tanaji ajikin ta kallon ta take zuwa can taji yace, " Aysha juyo.

Lumshe ido tayi tare da Kara juyar da kanta.

Kijuyo nace"

Jin bata amsa ba Kuma bata juyoba yace ki juyo nace.

Har yanzun bata motsa ba dan haka Aliyu ya juya ya kalli su Meenat da suka maida hankalin su ga tv sannan ya sake kallon Aysha yace.

Kijuyo mana Aysha sabo dake fa na zauna anan.

Wani irin kallo tamai sannan tace, ba dan ni bace, fada kazo yi.

A'a ninasan sabo dake na zauna anan.

Turo baki tayi kadan cikin yanayin dake nuna tana fushi, komawa yayi ya jingina da kujerar yana fadin, " kibar min haka agabansu ko kina son su fahimci akwai wani abu tsakanin mu.

Kara motsa bakinta tayi cikin nuna itafa bata huce ba.

Duk abun da suke idon Islama akansu sai dai duk iya baza kunnenta bata taba gane me suka ce.

Aysha?, Kijoyo kimin murmushi kawai inji in kwanta

Ganin ta hade rai yasashi ya mike yana fadin, " shikenan sai da safe.

Hanyar dakin sa ya nufa yayin daya sa hannun sa cikin aljihun sa yana tafe yana Satan kallon fuskarta sosai ta daure fuska, gani yayi har dai ya tafi ahaka bazai iya bacci ba dan haka ya dawo da baya cikin harcen filatanci yace, " Aysha akafar ki ga kadangare nan"

Wani irin zabura tayi ta daka tsallah ganin haka su Islam ma suka mike suna raba ido.

Aliyu kuwa tunda yaga Ayaha ta daka tsallaen nan ya wuce wuf kabar bashine yai mgnr ba yana shiga dakin sa ko ya fashe da dariya.

Shirin bacci yayi ya kwanta tare da karonta addu'a bacci sannan yaja bargo.

Aysha tabi Aliyu Nigeria, duk yadda za'ayi kumaido mana da yarmu idan ba haba wlh garin nan saiya gagareki zama keda ahakin ki.

Ta Yaya Aysha zatabi Aliyu, Aliyu fah shekarar sa biyar baya kasar nan.ta Ina zata bishi......

Ummi ce ta zaro ido ganin Aliyu rike da hannun Ayaha yayin da Umma tace Innalillahi wa inna ilaihir raju'un akwai babban masifa giwa tafito a ramin kiyashi.

Ummi ce ta bude baki cikin tsananin baccin rai ta nuna Aliyu da yatsa tana fadin Allah ya tsi......

Wani irin dirowavAliyu yayi daga gadon cikin tsananin tashin hankali mara misaltuwa, ganin gari har yayi haske ya saki ajiyan zuciya tare da mikewa ya nufi toilet har yanzun jikinsa rawa yake yi,.

Zuwa can ya fito yayi al'awa, sallah yayi anan dakin har yanzu Ajiyan zuciya yake saukewa, afali yace lokaci yayi da Aysha zata koma gida, wannan zanan be dace ba Sam koma menene ko me zai faru yakamata taje gida haka.

Pls kubi wannan link din ku dannan min  subscribe tare da alamar kararrawa

https://youtu.be/ebcYnNjGbOI

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

https://youtu.be/tfX94RbdUxE

Episode 34- 35

Tunani ya shiga me zurfi, ganin bashi da mafita ya mike yahau shiri, domin yau medoguri zai wuce, wannan mafarkin nasa sosai yasashi cikin tashin hankali,

Cikin sauri sauri ya fito ya leka dakin su Islam, tunkan ya shiga ya farajin dariyar su mamaki abun ya bashi, yadda yaji Aysha na kyalkyalar dariya cikin su Meenat abakin kofar ya tsaya cikin kaukausar murya yace, " Meke saki dariya?

Abun mamaki saiji yayi tace, hausa ake koya min, yadda ta furta kalmar daker yasashi saurin sakin dariya sannan yace, " cikin fulatacin eye, kinyi kokari, yadda yai mgnr Kai saika zaci fada yai mata.

Itama daurewa tayi sannan tace cikin fulatanci har ka shirya?

Eh zan fita, Kuma yau nisa zanyi, kicigaba da hausan mana, cike da yake da dariya kawai yana cijewa ne"

Meye ya baka dariya??

Naji dadi danaji kinyi hausa, saidai kin lalata Mana yare da wani bakin ki daya rike fulatanci sosai.

Murmushi tayi in bari kenan?

A, a'a Ina son ki iya ai, amman kibar yi gaban yaran nan karsuga dariya ta.

Wani irin kallo Aysha tamai sannan tai saurin cewa, jiya munci abinci, cikin hausa.

Murmushi ya fitar kadan sannan yace cikin fullatanci, ai kin karkace akan mgnr da muke, cewa zaki yi saina saka dariya gaban kannai ka da hausa.

Waigawa tayi ta kalli su Meenat da suka maida hankalin su kan tv, ganin tana kokarin tamasu mgn yace karki tambayi kowa.

Ai abu daya zan tambaya.

Jimmm yayi sannan yace to tambayi dayan munji.

Juyawa tayi ta kalli Meenat tai mata mgn tare da tsare Meenat din da ido.

Itako meenat cikin ladabi tace, kanwa ?

Cikin sauri ta juya tace da Aliyu cikin hausa, " kana dariya dariya da kanwa"

Dariya yayi sosai cikin kawar dakai yace kinyi kokari kiciba dayi, amman fa baki iya jara jummala ba.

Su Meenat ma sosai suke son yin dariya sai dai boyeta suke sabo da Aliyu, sarai suka ganne kureta yake son yi.

Agogon dake daure ahannun sa ya kallah yace, kalli yadda kika bata min lokaci, ki dan fito inason zanyi mgn dake ne.

Mikewa tayi daman shi yana mgnr ya fice"

Fitowa tayi suka tsaya falon yayin dayai kasa sosai da muryanr sa yana me kallon kwayar idon ta yake fadin, " zanje meduguri ne yau, bazan samu dawowa ayau ba.

Da saurin ta tace yaushe zaka dawo?

Bazance miki ga rana ba kowacce rana Zaki iya ganina amman duk halin da ake ciki bazan wuce sati ba.

Shiru tayi batace komai ba idonta akasa yayin da ta shiga wasa da yatsun ta.

Kallon ya tsun nata yayi da take ta faman lankwasawa yace, " na lura dake, duk lokacin da aka fara wata mgn da bata miki ba saiki hau lankwasa yazun ki, kibi ahankali kada kiyi masu ILLAH, sannan Ina son in tambaye ki??

Da sauri ta dago da idonta da suka tara ruwa ta kalleshi ko kifta ido bata yi.

Yaushe zaki koma gida???

Kurr tamai da idonta yayin da yaga hawaye yana sakkowa kumatun ta.

Menene haka?, Aysha me kike so?, Yaya zamuyi ki fada, kawo shawara Aysha, menene mafita, Nidai Ina ganin yakamata kije gida haka nan.

Nasani, Nima nasan dole zan koma, nima Ina son nakoma, amman yanzun idan na koma gida damuwar da zan shiga Kuma saitafi ta da, kashhh, Yaya Aliyu dama nasani da banzo ba.

Jimmm yayi zuwa can yace, Aysha ni zan kaiki gida da kaina, nikaina hankalina bazai taba kwanciya ba matsawar kina Cameroon ni Ina nan. ko ayanzun kawai Ina daurewa ne kawai amman Allah kadai yasan me nake ji.

Sheshekar kuka ta fara, domin gani take babu wani hanyar da zasu kasance tare matsawar Aliyu zai kaita gida, Kuma yace yana neman auren ta, akwai Babban matsala.

Shi kansa Aliyu yana fada ne kawai tare da karfafa ma kansa guiwa amman inya tuna wacece Umma gaban sa har faduwa yake yi akan irin kinsa da take

Aysha dan Allah ki share hawayen ki Kar Kuma ki sake yin kuka, insha Allahu zamu rayu tare, muyi zaman aure, mukuma haifi yaran da iyayen mu zasuyi alfari dasu, Allah ne yasa

mana kaunar juna bamu mukasawa kanmu ba, Kuma kisa azuciyar ke abun da Allah yaso ne kawai yake tabbata, idan kin rike wannan zakiji dadi cikin ranki,

Cigaba yayi da cewa, dana dawo zamu sa rana dan Allah ki kwantar da hankalin ki.

Amsawa tayi dakai tare da fadin, kaje ton, Allah ya kiyaye hanya.

Juyawa yayi yana fadin ki kula da kanki, harya Kai Kuma yaji tace, Yaya Aliyu?

Juyowa yayi yana fadin na'am Aysha.

Ka gaida budurwa ka....

Ke kadai ce.

Yaya Babba dakai?, ni ban yadda ba.

Wlh azim ke kaidai ce bantaba kallon wata 'ya mace naji wai Ina sonta ba.

Dariya take yi yayin da hawaye ke zobu mata, Hannu ya daga mata sannan ya juya ya tafi cike da tunani.

******

Dakin ta koma tana share hawaye, su Islam ne suka tambayeta lafiya, nunar masu tayi da tagaji da zama ne, ta kosa Mijinta ya dawo, lallashinta suitayi ganin tana cikin damuwa da yamma suka ce tazo suje islamiya.

Tundaga ranar suke tafiya makarantar tare, yayin da hausanta ke samun cigaba, ranar da Aliyu yayi kwana uku ma hausanta yayi kwari wuni suke suma mgn da su Islam sai dai hausar tsta babu dadi.

Yau kwanan sa shidda da tafiya dan haka suke saka ran gobe zai dawo.

Harabar gidan suka fita su uku can gefe suka zauna yayin da Meenat takewa Aysha kalaba, Islam kuwa zaune take tana basu Ibr, dukan su shiga iri daya ne ajikin su rikace yar karama me gajeren Hannu, sai siket din da ya wuce guiwa kadan.

Suna cikin hiran wani saurayin islam ya shigo, ganin su agurin yasa shi tahowa ya Dan tsaye daga nesa dasu kadan yana fadin"

Kitso kike ne??

Mikewa Islam tayi zuwa gurin sa tana fadin eh.

Waccen yariyar fah?, Wacece ita? badai nan gidan take ba?

A'a bakuwa ce, yar uwarmu ce.

Ok Amman kamar ba bahaushiya bace, tana da kyau sosai.

Lumshe ido Islam tayi, fulani ce.

Ku fulani ne daman?, amman bakijin fulatanci?

Muba fulani bane.

Naji kince yar uwarku ce.

Eh,  yar uwarmu ce, aikasan yayamu Haydar ko??

Eh nasan shi kwarai kuwa.

Toh wannan kanwar sa ce.

Ok nagane shi yanzun yanajin fulataancin?

Zaro ido Islam tayi tare da fadin, toh ai shima dama cen hausan shi bawani fita take ba, idan yana hausa saika gane fulatancin ya rike bakin sa, mamasun fulanin Cameroon ce gurinta ya girma Kuma.

Masha Allah, uwa daya uba daya suke ne?

Me kake tunani?, Itafa wannan ma matar aure ce.

Allah sarki Masha Allah.......

Gate din gidan suka hango ana wangalewa basu ankaraba suka ga hancin motar Aliyu ya sawo kai cikin gidan, cikin sauri islam ta durkusa bayan fulayoyin dake gurin tare da zaro ido.

Meenat kuwa zamanta tayi  tana cigaba dama Aysha kitson take fadin, Yaya Haydar ya dawo.

Saurayin Islam kuwa tsaye yake hannun sa cikin aljihun sa.

Wani irin sako kafa Aliyu yayi daga cikin motar, cikin kakinsa na sojoji fuskarsa daure tamau yake kallon inda su Aysha ke zaune, sannan ya hange saurayin dake basarwa yana kallon can gefe, lumshe ido yayi cikin tsananin bacin rai, gashin Aysha yake hangowa ana kitsashi a titi,  bude ido yayi ya sake kallon su, cikin sauri ya waiga ya kalli bakin gate din gidan cikin wani irin tafiya ya Karasa gurin wayar wutar datakai wuta dakin megadin ya kallah, wani irin tsalle yayi  ya finciko ta sannan yayi kansu Aysha aguje.

Meenat ce tai saurin sakin kan Aysha ta kwasa aguje  hakama Islam mikewa tayi tana fadin Momy!!

Shima saurayin na Islam asttin ya bar gidan Aliyu kuwa bayan su Mennat yabi yayin da yajefesu da wayar wutar daya ciro.

Azaban zafin da sukaji saukan wayar wutar ajikinsu yasa suka tsananta gudu tare da Kiran Momy.

Arikece Momy ta fito cikin tsananin tashin hankali tace Haydar me sukayi ne, run gumesu tayi ajikinta adaidai lokacin da Aliyu ya karaso gurin

Wayar wutan ya dauka yana fadin kuxu nan.

Sakin su Momy tayi tana me dada turosu duk da riketa da suke yi, adai dai wannan lokacin Aysha ta shigo dan kwalinta rike ahannunta, wucesu take kokarin yi yace kema zo nan.

Zaro ido Momy tayi tana fadin, itama dukan ta zakayi ne?

Be saurareta ba, fadin yake zakuci ubanku yau, daman kasuwa akeci agidan idan ban nan, ganin yana murde wayar Aysha tai saurin shiga bayan mommy tanama Aliyu wani irin kallo gaba daya ya canza mata.

Tana kallo ya Zane su Islam sai ihu suke sannan ya nufo gurin Momy yana fadin saura ke.

Sai dai ka zanemu tare, baka da hankali ne, aiko amakaranta ba'a dukan matar wani, sabo da darajan aure.

Wlh saina daketa, aitafi su laifi.

Toh Bismillah kazo ka dakemu tare bakomai, Kuma tunda ni baka ganina da mutunci barin aika akira baban ka idan mahaifiyar kace ai bazata ce  bari kaki bari ba.

Sakin wayar yayi da sauri yabar dakin cikin sanyin jiki Aysha ta fara kuka.

Su Meenat ma duk kuka suke
Domin bakaramin duka ya musu ba.

Tunda abun ya faru yau kwana uku kenan bataga Aliyu ba, tasan fushi yake da ita shiyasa be nemeta ba, tagumi tasa yayin dataga  Islam ta shigo tana murna.

Meenat ce tace Yaya dai?

Yaya Haydar zaiyi tafiya harna tsayon wata hudu💃💃

Cikin sauri Meenat tace, wow, abun ya burge, kice zamu huta kwana biyu.

Gane me suke nufi yasata ta mike da sauri ta nufi kofar fita, tafe take tana tunani harta Isa falon sa, ahankalin ta tura kofar tare da sallama.

Kasa kasa ya amsa sannan ta shiga ta zauna, zaune yake akujera da alamar bayajin dadi dan harya dan rame, ahankali tace Ina kwana.

Lafiya Lau

Cikin in Inna tace Yaya Kai hakuri dan Allah kaji?

Murmushi yayi mekama da yake sannan yace naji, ya wuce Aysha, na huce tuni ko baki zoba yau nai niyar yau na kiraki, Ina son ki aramin hankalin ki.

Dagowa tayi ta kalle shi.

Kinaji Aysha, naso in kaiki gida da kaina amman tafiya ta taso min  ban shirya ba, zanfi waje harna tsayon wata hudu.

Nan danan hawaye suka zubo mata.

Kawar dakai yayi tsayon laci batare daya juyoba, zuwa can yace, kibar kuka, ki yadda dani, zan dawo na miki alkawari, jibi zan wuce ki shirya  gobe zansaki a mota ki koma gida, jiya na gayawa Baffah gobe mijin ki zai dawo.......

Idonta cike da hawaye ta kalleshi yayin da yai saurin kawar da kansa tare da cire kwallar dake son zubo masa.....

https://youtu.be/tfX94RbdUxE

*⚫BA'KAR FURA⚫*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

episode 35- 36

Gaba dayan su wani irin tashin hankali suka shiga ciki lokaci daya.

Ahankali yakejin sheshekar kukan Aysha yayin da ya kasa kallonta, Kuma ya kasa hanata kukan.

Tsayon lokaci suka dauka ahaka sannan Aysha ta mike tana kokarin fita taji yana cewa.

Kibar kuka kinji.

Batace komai ba ta fita cikin wani irin yana yi, kafin ta Isa danin su Islam saidata share hawayen ta sannan ta Isa, Kai tsaye bayi ta shiga ta wanke fuskarta sannan ta fito ta fara tattara kayanta, wannan karon akwati biyu tayi domin zaman ta anan Aliyu yakan mata sayya hakama Baffah indai zaikawowa su Islam wani abun to tare yake kawo masu.

Bayan tagama hada kayanta tsaf ta ta mike ta Isa dakin Momy acan ta samu su Islam, Meenat naganin ta tafara fadin.

Aysha ashe gobe Zaki wuce yanzun Baffah ke gaya mana.

Murmushi tayi kadan tace eh nima yanzun ne yaya Aliyu ya gaya min gobe zai dawo

zamu wuce.

Wayyo Allah sarki wlh kamar karki tafi, kamar kiyi zaman ki anan.

Islam ce tace ta zauna mijin nata fah?, kawai dai musa rana muje Cameroon din dama bamu taba ganin Ummi ba.

Momy ce tace eh ai yayan naku ne wani irin mutum ne, amman yanzun in kunso zuwa kwaje kota dalilin Aysha sai dai Kuma baku da Dan jagoro.

Zanwa Baffah mgn, wata rana idan Yaya zaije yace masa yaje damu.

Lallai kuwa, toh Allah ya kaimu muga ni.

Haka sukaita hiran kewan Aysha, misalin karfe 04:30pm Aliyu ya dauki Aysha, sayya ya kaita tayi, acewarsa wai tsaraba ne kaya da yawa ya saya mata naci Dana sawa sannan ya kamo hanya gida da ita.

Ganin haka Aysha tace yau bazamu gidan ka bane?

Kawar da kansa yayi sannan yace eh,

Jimmm tayi tsayon lokaci sannan tace, bazamu yi hiran sallama ba??

Atakaice ya sake cewa eh.

Wani irin abu ta hadiye sannan ta sake cewa , sabo dame?

Juyowa yayi ya dan kalleta kadan sannan yace, sabo da kiyayewa.

Bangane ba?

Eh tana iya yiyuwa ki kasa ganewa,  Ina nufin Kinga kowa yana dauka ke matar abokina ce, Kuma nace masu gobe Zaki wuce bana son su zarki wani abu.

Kallon shi tayi sosai sannan tace, " aiko da kowa yasan da wannan amman muna fita"

Kawar da kansa yayi sannan yace, mubar wannan mgnr Aysha, duk abun da kikaga nayi kisa azuciyarki Ina da dalilina nayin shi, nafi kowa son mu kasance tare harke kanki, tun da kikaga na zabi hakan toh nayi zurfin tunani ne Naga hakan ne mafita.

Har yanzun Aysha bagane inda ya nufa tayi ba dan haka taji ya bata haushi, Koda suka Isa gida ficewa tayi batare data masa sallama ba, shi da kanshi ya dauki kayan ya bita dashi

tare da fadin, gobe kina idar da sallah asuba Zaki wuce, dana dawo masallaci zanzo na dauke ki.

Kasa kasa tayi da murya tace ka kaini tun dare ma kawai ai daman nasan ka kosa na wuce.

Tsayawa yayi yana kallonta tsayon lokaci sannan yace, kin kasa ganewa ne Ayaha, amman bakomai duk me zakice naji, ninasan Ina da dalilina nayin hakan, ficewa yayi abin sa yayin da Ayaha tabi bayan sa da kallo.

Daren yau Aliyu be iya Koda runtsawa ba haka yaita mutsu mutsu agado cikin wani irin damuwa wadda baya tunanin ya taba shiga cikin sa,

Haka itama Aysha ji take tamkar bata taba shiga wani damuwa ba sai yau, idon ya bushe kandas babu alamar bacci acikin ta gashi batasan me zataje ta tarar a gidan ba.

Tunkafin akira sallah ta tashi tai wanka ta shirya.

Kamar yadda Aliyu yace ana fitowa masallaci ya taho dakin su Islam yana fadin idan kin gama muje.

Momy ce taji muryan Aljyu ta fito tana fadin Aina dauka mijin nata me zaizo ya dauke ta?

Eh yana tasha, cikin dare suka iso, yace nakaita kawai daga baya zaizo ku gaisa.

Toh Babu laifi, amman taje tayi sallama da baban ku.

Haka akayi cikin rakiyar momy Aysha tayi sallama da Baffah yayin da yaita masu addu'a Isa gida lafiya da zaman lafiya tsakanin ta da mijin ta, sannan ya dauko kudi ya mika mata, fitowa sukayi cikin rakiyar su Islam da Momy har bakin motar Yaya Aliyu, sunso suje harcen Amman Aliyu yace a'a

*******

Cikin motar ma zaman kurame akayi, kin mgn Aysha tayi tare da kin kallon gefen da take, shikuwa kallonta yaketayi yana Jin wani zafi cikin ransa.

Lokacin da suka iso motar harta kusa cika, wani mutuni ne ya taho dattijo yana fadin, Aliyu ka kusa makara.

Wlh Baba kasan shirin mta, saukowa yayi yana kokarin fito da kayan Aysha dake cikin motar sa, Aisha kuwa motar tai saurin shiga gefen window ta zauna, da Aliyu aka sanya kayan Aysha amotar, sannan ya juyo yaga wata mata dake kokarin shiga cikin motar dan ahaka yai

saurin fadin"

Aunty Ina kwana?

Amsawa tayi cikin fara sannan Aliyu yace mata kema can Cameroon Zaki?

Amasa masa tayi da eh"

Yauwa dan Allah aunty ga amanar kanwata, juyo Aysha tayi ta kalleshi kadan ta kauda kanta, tanajin sa yana gayawa matar sunan unguwar da zata.

Motar matar ta shigo saidai wani ya rigata zama kusa da Ayaha ganin haka Aliyu yai saurin cewa, abokina ka zauna agaba mana, ko musu meyi ba cikin sauri ya fita ya koma gaban, yayin da matar ta zauna kusa da ita.

Ahankali ya dawo gurin window kasa yayi damurya saitin kunnenta yace saina zo Aysha, insha Allahu dana dawo can zan sauka.

Nikabar min mgn.

Murmushi yayi mekama da yake sannan yace, kina nufin ahaka zamu rabo kina fushi Dani??

Toh Yaya bakai bane baka damu dani ba"

Ai daman nasan haka kike gani ban damu dake ba, ni bakaramin yaro bane Ayaha nasan abun da nake yi, ke kuma yarinya ce, da kuruciya akan ki, shiyasa kike ganin haka.

Hawaye ta share sannan tai kasa da murya sannan tace, ai dai baka haifi kamata ba dazaka dinga cemin yariya.

Kallo yabita dashi tsayon lokaci sannan yace, " Ashe kin iya tsiwa?, wannan ba halin ki bane, nasan ke yariya ce me hankali, Allah ne kadai yasan halin da zuciyata take ciki ayanzun, Aysha badan Ina dagewa ba da yanzun zazzabi ya kwantar dani, wlh bana farin ciki da tafiyan ki, amman ta wani bangaren farin ciki nake, domin zuwanki gidan shine yafi dacewa, idan har ni masoyin ki ne na hakika bekamata in rike ki anan ba, nai miki alkawari Aysha kome zai faru dana dawo zanzo, kibar zargina, Ina tsananin son ki, kuma da yardan Allah ke matata ce.

Kuka Aysha ta fara, Yaya Aliyu da gaske zaka zo?

Insha Allahu, inaso ki yadda dani kamar yadda na yadda dake, ni bani da wani haufi akan sonda kike min, nasan cewa nine kaidai azuciyar ki, ko tunani na beyi daidai ba???

Kukanta ne ya Kara yawa tana fadin hakane Yaya Aliyu Ina son ka sosai.

Toh ki rike min amana ni bazan cuceki ba ke kanwata ce wadda nake tsananin so.

Kuka tasa harda shasheka yayin da Aliyu yayi saurin hada kanshi dana Aysha sannan ya saka hannun shi ya share hawaye, batare daya dago ba yace, kibar kuka Aysha, dan Allah ki bari karki sani kuka a titi, ko kina son mutane su tafi suna cewa sunga wani soja yana kuka dan kanwarsa zatayi tafiya?

Eh kayi kukan, ta fada kanta na manne da nasa.

A'a idan naje gida zanyi, ni namiji ne ba mace ba Aysha.

Ni Ina son naga kayi.

Batare daya dago ba yace toh kisa hannun ki kishafa fuskata kiji, cikin sauri tayi yadda yace din nan taji hawayen sa akan tafin hannun sa.

Cikin mamaki tabi gashin kansa da kallo adaidai lokacin da motar take kokarin tashi.

Dagowa Aliyu yayi idon sa cikin na Aysha hannun sa ya sa cikin aljihu tare da cizon leben sa, yanna kallon yadda Aysha ke zubar da hawaye tana dago masa hannun ta, duk iya daurewa da yake, sannan tsintakan kansa yayi yana daga mata Hannu yayin da hawaye ya zobo masa, ahankali motar tabar wajen har suka fita daga cikin gate din yana hango hannun Aysha, cikin sauri ya shiga cikin motar sa yabar wajen da masifar gudu.

Kai tsaye gidan ya wuce yayi da hawaye sukaki tsayawa a idon sa, Koda ya shiga kansa tsaye fada gado, cikin tsananin tashin hankali, halin da ya shiga yasashi ganin yayi ganganci daya turata gida, gani yake kamar yanzun babu wani abu da zai iya yi, Aysha tayi karfi azuciyar sa fiye da da, Kuma yana ji ajikin sa itama hakance azuciyar ta.

Mummunan tashin hankalin daya shiga shiya haifar masa da zazzabi me zafin gaske, kuka yaci irin wadda betaba yin sa ba kamar wani karamin yaro yana Kiran Ayaha.

Ahankali yaji ana boga kofar.

Jimmm, yayi yana tunanin waye zaizo masa nan, iya sanin sa bawani da sukayi zaizo dan haka yai kwanciyar sa, ji yayi bugun yaki karewa, dan haka ya taso daker ya Isa bakin kofar ya bude.

Cikin tsananin mamaki yake kallon ta tsayon lokaci.

Itama kallon sa take idon ta fal fa hawaye.

Daker ya iya hada kalmomin yace, Yaya haka kuma?, Aysha meyasa kika dawo?

Lumshe ido tayi nakasa tafiya yaya zuciyata zafi take min.

Lumshe ido yayi tare da cije lebensa, sannan ya zuba mata ido tsayon lokaci, cikin saurin ya ware mata Hannu ta fada jikin sa, wani irin rungumeta yayi tsam ajikinsa tsayon lokaci, sannan ya dagota ya kalli fuskarta tare da sumbatan goshinta, becire bakin saba har saida ya gangara cikin bakin ta, ajiyan zuciya sukayi atare yayin da labarin ya fara canza salo, nanda nan suka gigice tare da fita cikin hayyacin su.

Kasancewar al'amari ne yazo masu bako gaba dayan su kafarsu kasa daukan su tayi dan haka Aliyu ya dauketa cak yai cikin dakin sa da ita, kan gadon ya tireta cikin wani irin shauki tunanin sa gaba daya ya dauke awanan lokacin, haka itama Ayaha soyayya ta rufe idon su gaba daya, wasa kawai Aliyu yake da Aysha yana sauke numfarfashi har ba adadi, ahankalin ya fara rabata da kayan jikinta kamar yadda ya riga daya cire nasa, kamar me fada Aliyu yake taba jikinta Aysha son ransa, ahankali ya daura bakin sa akan dukiyarta sannan yasa hannun sa duk biyun ya runtse su duk biyun cikin wani irin gurnani yake fitar da numfashi, Aysha kuwa duk abun da yake tanajin sa saidai bata iya hanawa, wani irin radadi dataji ya gewaye ilahirin jikin ta yasa ta sakin wani gigitaccen kara, ko Ina najikin ta Jin radadin take har tsakar kanta dan haka ta kasa daina ihun, yi take da matsancin karfi.

Aliyu kuwa hakan kamar ma wani kaimi ake Kara masa, ihu take yayin da take ganin kamar tunzura shi yake, dan haka ta shiga Kai masa duka tare da shushure kafafuwan ta.

Bata ankaraba taji ya nadeta gaba daya, ta inda ko hannun ta bata iya kwantan sa wajen sa, baki kawai gareta dan haka taita kwala ihu tana Kiran sunan sa, zuwa can taji ya rike bakin da nasa daga nan bata sake sanin inda kanta yake ba......

*BA'KAR FURA*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

https://youtu.be/ejQDIoQWEig

Episode 37- 38

Tsayon lokaci Aliyu ya dauka yana abu daya, baji ba gani, cikin tsabar gigicewa da sambatu kala kala,  gaba daya ya rasa inda zaisa  kansa,  bayan kusan minti 30 nutsuwa ta samesa bayan ya samu gamsuwa me tarin yawa.

Ahankali yake janyewa daga cikin ta, gefenta ya kwanta yana fadin, " ya subuhanallah, astagafurullahi wa atubu ilaika, kashhh, nashiga uku, wayyo Ummi na.

Kukan Ayaha yakeji yana tashi kasa kasa kara jawota yayi jikinsa sosai yana fadin"

Yi hakuri Aysha, ki yafe min, na tabka babban kuskure, Aysha, Aysha kinaji na?

Kuka kawai take yi kasa kasa, yayin da yakejin hawayen ta na jika girjin shi.

Rasa inda zaisa kansa yayi, saboda tsabar takaici da tashin hankali, dan haka ya shiga rarrashin Aysha dake kwance akan kirjin sa, lamu tayi a jikin sa, saidai fah kukanta Kara yawa yake, ganin ba kulawasa take ba ya sakko gadon ya nufi toilet wanka yayi, yanayi yana zubar da hawaye, kafin ya gama wankan idon shi yayi jawur sannan ya hada ruwan Aysha ya fito, bece mata komai ba ya dauketa cak ya nufi toilet da ita, zuwa wannan lokacin tureshi tafarayi duk da cewa bata da karfi sam.

Cikin ruwan daya Tara me dumi sosai yake kokarin sakata, yayin da tafara cewa banso nika barni.

Cikin ido ya kalleta sannan yace, barin saki mana saina barkin.

Ni banaso😭😭

Kawar da kansa yayi sannan yace, toh barin fita na baki guri, amman kafin na fita inason naga kin zauna acikin ruwan.

Cikin matsanancin kuka muyar bata fita sosai tace, bazan shigaba ubanane kai?

A'a Sam Aysha, amman lallai sai naga kin shiga ruwan nan zan fita.

Bazan shiga ba toh.

Toh naji Allah ya baki hakuri, juyawa yayi kamar zai fita sai Kuma ya juyo da saurin sa ya dauketa cak ya dannata cikin ruwan.

Wani irin ihu ta yanka, yayin da Aliyu yake danne da ita, zuwa can tai shiru yayin da yaga gumi na tsatsafo mata agoshi, idon shi cikin nata, sakinta yayi sannan ya fito yabar mata bayin.

Aliyu ko Koda ya fito kasa shiryawa yayi saboda tsabar damuwa da tunanin daya shiga, sosai yaji tashin hankali mara missaltuwa, hakika ya aikata babban kuskure.

Hawaye ne suka shiga zobo masa ahankali ya juya ya kalli zanin kadonsa dayai kaca kaca da jinin Aysha, nan take yaji kanshi na ciwo. Be ankara ba yaga Aysha na kokarin fitowa, Amman tunda ta leko ta ganshi daure da towel har yanxun saitai saurin komawa.

Ganin haka Aliyu ya mike, Hajjabin ta ya dauka ya Isa bakin toilet din ya tura kofar kadan ya mika mata, sannan ya dawo ya dauki jallabiya yasa, tare da yaye zanin gadon yai nufi falo.

Tsawon lokaci ya dauka afalon sannan ya dawo lokacin Aysha tana zaune akasa ta hada kanta da guiwa sai kuka ta ke cikin tsananin tashin hankali tare da danasani mara amfani.

Ahankali ya Isa gefenta, Ayaha nace kiyi hakuri kinji.

Cikin matsanancin kuka tace, " Nina shiga uku Yaya Aliyu, rayuwata babu dadi, yanzun idan baka aure ni bafah?😭😭.

Yi shiru, ki shiyiru Aysha, nine mijin ki insha Allahu, kibar irin wannan tunanin, kiyi addu'a kawai Allah ya cika Mana burin mu.

Bawani nan,nasan yanzun barina zakayi tunda bani da abun da kowacce mace ke takama dashi, nashiga uku na lalace.

Kashhh, nagaya miki kibar wannan mgnr, ni ke kanki nake so bawani abu dake jikin kiba, aure nake son muyi ba lalata ba, wannan abun da daya faru ki daukeshi ama matsayin kaddaramu ce, nayi iya bakin kokarina kawai dan ganin nakauce ma hakan, Aysha meyasa kika dawo????

Kuka kawai take ganin baxata amsa ba yace toh yanzun ki gi kwanta ki huta.

Mikewa yayi ya dauko zanin Gado ya shinfida, sannan yace kizo ki kwanta bari nemo miki abun da zakici rana tayi.

Kin kulasa tayi dan haka ya sake cewa ki kwanta nace,

Cikin sauri ta juyo masa bayanta, kallonta yayi tsayon lokaci sannan ya kada kansa ya fita.

Bayan taga fitansa Kara tsananta kukanta tayi, saida tayi me isarta, nan gurin bacci ya dauketa.

Koda Aliyu ya dawo ya samu tana bacci ledojin hannun sa ya aje sannan ya koma falon ya zauna cikin damuwa sosai, hawaye ne ya fara zubo masa yana sharewa, azaune take baccin wata zuciyar kece masa ka gyara mata kwanciyar yayin da wata zuciyar ke hanasa yin hakan,

Ayanzun tausayin Aysha yafi ji fiye da tunanin Umma, sosai yakejin tausayinta cikin ransa, yasan yariyace karama, wadannan tashin hankalin sun mata girma, har aka Kira sallah Azahar Aysha bata tashi ba, bayan ya dawo sau uku yana lekata, ganin har da yadawo sallah la'asar bata tashi ba ya shigo dakin yana Kiran Sunanta.

Aysha, kitashi kiyi sallah.

Kula yayi tana rawan sanyi, dan haka ya karasa ya taba wuyanta zafi yaji rau, take yaji gaban sa ya fadi.

Tsaye yayi yana binta da kallo tsayon lakaci idonta abude suke da alama ma ba bacci take ba,

Juyawa yayi, cikin rasa abun yi, bayason ma a ganta akwance haka adakin sa, daya Kira likita ya duba ta, mutane na ganin sa da mutunci, baya son ashiga shargin sa dan haka ya yanke shawaran sawo magani kawai, daker yasata tadanci Naman daya sawo mata sannan Tasha maganin ta kwanta.

Kafin dare ta danji dadin jikinta harta  tai sallah

Kula Aliyu yayi bata dawo da kayanta ba dan haka da daddare ya fita, kaya kala biyu ya sawo ma Aysha sannan ya dawo gida lokacin tayi bacci dan haka ya ajiye kayan sannan ya dauki filo ya koma falo.

Kokaci bayan lokaci yana leka Ayaha sannan ya koma ya kwanta, saidai fa bacci ya gagaresa jiya beyi bacci ba yauma babu sannan tashin hankalin da yake tattare dashi yau yafi na jiya dan haka yaji duk wani iri yake ji.

Aysha ko baccin ma da take bame dadi bane, cikin mawucin hali take baccin gashi duk jikinta ciwo yake mata, ji take kamar jijiyoyin jikinta ya rake.

******

Washegari tunda Aliyu ya dawo masallaci yazo ya tashi Ayaha, yana fadin, kiyi wanka muje"

Mikewa tayi ahankali tanufi toilet, Aliyu kusa juyawa yayi zuwa falon bayan ya ajiye mata kayan daya sawo mata agefen gadon.

Koda ya koma falon kansa ya sake hadawa da guiwa, mafita kawai yake nema cikin sauki.

Bayan kusan minti 30 Aysha ta shigo falon cikin sunkuyar da kanta.

Zama tayi hannun kujera ta kalli can gefe, binta da kallo Aliyu yayi sannan yace, " Ina kwana.

Kara dauke kanta tayi can gefe yayin da ya sake cewa Ina kwana Aysha?

Wannan karon ma bata tankashi ba.

Aysha nace Ina kwana, ya jiki?

Cikin sauri tasa hannun ta tashere hawaye tare da zunboro baki.

Mikewa yayi cikin sanyin jiki yana kokarin dawowa kusa da ita, ganin haka tai saurin mikewa.

Lumshe ido yayi sannan ya kalleta yace, " shikenan, komawa yayi ya zauna sannan yace, jiya me ya dawo dake??

Banza tamai, tare da cuno baki.

Ina kayan ki?

Murya can kasa tace, suna can.

Inajinki meyasa kika dawo???

Ganin bata da niyar mgn yace shikenan ki tashi muje.

Mikewa tayi yana gaba tana binsa abaya

Cikin motar ma Aysha baya ta juyo ma Aliyu, Sam beson su rabo ahaka, dan haka ya kasa tada motar sai kallonta yake yi ahankali yace, " Aysha mufahimci juna dan Allah kafin ki tafi, kibar fushi nan beda wani amfani, bada gangan nayi ba kema kinsani, idan kika tafi kina fushi Dani kin zalince ni.

Toni zalincin daka min fa??😭😭 Kara juyo masa baya tayi bayan ta fadi haka.

Naji nazalinceki Aysha, amman banyi da niya ba, nata gudun kada hakanta faru, inaji azuciyata nafiki damuwa, kwata kwata bansoba Ayaha, amman ki kwantar da hankalin ki aana dawo zanzo.

Hawaye take sharewa nidai ya Aliyu bansan inda zansa rayuwata ba, nashiga uku.

Aysha ki nutsu Mana, ni bani da burin cutar ki, gaya jiya bayan nasaki amota meyasa kika dawo??

Ni Yaya Aliyu kasa tafiya nayi, nafison mutafi tare, shiyasa na dawo ince maka kazo mutafi ne kawai, Kuma ga abun da ya faru😭😭😭,

Lumshe idon shi yayi, yayin da hawaye suka zobo masa, hannun sa ya mika ya jawota suka hada kansu waje guda yana fadin, " Nima naso haka Aysha, amman baxai yiyuba bane, wannan tafiyan dole dani acikin ta, kuma bekamata ki zauna har indawo ba, domin agida za'a nemeki, zaman naki anan beda wani amfani idan kinyi tunani Ayaha, kiyi kahuri kije gida, kibani wata uku na miki alkawarin zanzo, zanzo da mgnr auren ki.

Cikin kuka sosai tace zaka zo da gaske??

Zanzo ki yadda dani.

Yaya Aliyu?

Na'am Aysha

Meyasa Allah ya jarabceni da son ka har haka?

Ya jarabce mudai Aysha, Allah ne kadai yasan wannan, Aysha in tambaye ki mana?

Tam Yaya Ina jinka.

Ki share wayen ki, ki saki ranki sai muyi mgnr.

Dagowa tayi daga jikin shi ta koma kujerar tana share hawaye.

Saidai ta gama share hawayen sannan yace kinajina?

Eh.

Nawa ga wata kikeyin al'adan ki??

Cikin sauri ta sunkuyar da kanta sannan tace, " ashirin da hudu"

Jimmm yayi sannan ya kalleta yace" ashirin da hidu?, to ai yau talatin ga wata fah?

Eh, jiya nayi wanka kafin mu fito.

Leben sa nakasa ya cija da hakorin sa sannan ya fita a motar yana fadin Ina zuwa"

Kusan minti shabiyar ya dauka sannan ya dawo, idon sa jawur ya zauna amotar sannan ya suka tafi, gudu yake dan haka nan danan suka isa

Inda ta bada ijiyan kayanta sukaje suka amsa, sanan yasa mata amotar dake shirin tashi yanzun, Jakarta ya karba ya bude sannan yasa hannun sa ya ciwo kudi me yawa yasa aciki, rufewa yayi kalleta, Aysha ki shiga motar karki ce zakisake sauka, nima yanzun ko gidan baxan koma ba wucewa zanyi daga nan, sannan komenene yake faruwa a Cameroon ko wani hali Zaki shiga karki sake cewa Zaki dawo Nigeria, ko Ina nan bazan so ki sake kamo hanyar nan ba bare bana nan, namiki alkawarin dana dawo zanzo, kema kimin alkawarin baxaki sake kamo hanyar nan ba sai tare dani.

Cikin sauri tace bazan dawo ba ai daman Yaya, amman kacika alkawari.

Insha Allahu Aysha

Rakata yayi har bakin motar ta shiga sannan aka rufe motar, Hannu yaita daga mata itama take daga masa har suka daina ganin juna, sannan ya koma motar sa ya zauna tare da hada kansa da guiwa, zaman kusan awa daya yayi agurin ya kasa tafiya, tunanin sa ko Aysha zata dawo, Koda ya fito cikin tashar ya dade abakin hanga saida ya tabbar yanzun sun bar Kano sannan ya wuce gidan Aunty rukayya

******

Aunty bani da lafiya.

Meye haka Aliyu, kuka kuma kake katon ka dakai, meke damun ka haka?

Bansani ba aunty, haka nan nakejina wani iri narasa inda zansa kaina naji dadi aunty.

Subuhanallah, kana addu'a kuwa?

Inayi aunty, komai da ya dace inayi, sannan Ina kokarin hana zuciyata sabon Allah, amman hankalina Kara tashi kawai yake, idan Ina tunanin Ina cikin damuwa sai wani abu yazo ya kifto min wadda yafi na baya, gaba daya na kasa nutsuwa.

Kana da damuwa ne Aliyu bazaka fada bane dai kawai, toh koma menene kaita addu'a.

Aunty ni ki rarrasheni, ki kwantar min da hankali kamar yadda Ummi kemin

Hmmmm, ka fara kewanta kenan, kayi hakuri kabar kukan nan kada Yaya Fahat ya gani, idan yagani hankalin sa tashi zaiyi, lallashin ka Kuma babu wadda zai iya maka kamar nata, waye zai zauna yana rarrashin kato kamar ka ai sai ita Ummin, da kasan danine agarinan shekaranka biyar amman sau daya kazo gidana.

Kansa ya kwantar kan kafadar aunty Ruqayya yana fadin, kiyi hakuri na bari.

Tausayi ya bata dan haka ta daura hannunta akan sumar sa tace, "  Allah ya yaye maka abun da yake damun ka, ya Kuma kawo maka mafita.

Har cikin ransa yaji dadi sannan yai masu sallama ya fito, daga nan gida ya wuce yayi wanka tare dayin sallama dasu Baffah, farfe 04:00pm jirgin su ya tashi.

Cameroon

Misalin 01:44pm Aysha ce ake sauke mata kayanta atasha, wata motar ta tare tana zuba kayan tare da fada masa inda zata.

Cikin motar ta zauna duk jikinta asanyaye hanya suka kama yayin da take kallon garin nasu duk ya mata wani iri, inda ta shiga tunanin yau watanta Uku da sati biyu rabonta da Cameroon, gabanta taji yayi mugun faduwa, ko me zataje ta tarar agida?, Me zace masu?, Yanzun  Sunan bana gidan Daddy na,  idan suna sani Ina zance masu naje?😔🙊

https://youtu.be/ejQDIoQWEig

*⚫BA'KAR FURA⚫*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

episode. 30- 40

Tsintan kanta tayi da zubar da hawaye, cikin tsananin tashin hakankali take jinta sosai mara misaltuwa, babban abun dake damun ta ada bewuce taje dan taga Aliyu taji dadi ba, amman gashi zuciyarta har yanzun babu dadin

Hawaye ta fara sharewa ganin motar ta shiga cikin unguwar su gabanta yaci gaba da faduwa,

Akofar gidan su motar ta tsaya, fuskarta ta share dakayu sannan ta fito cikin motar, yayin da ake sauke mata kayanta, ahakali ta shiga Jan akwatin ta tanufi cikin gidan, gabanta na tsanta faduwa, cikin siririyar muryanta tai sallama.

Ummace tai saurin fitowa daga cikin dakinta tana fadin, "Aysha idon ki kenan' Kinga kayana nan nadaure Ina shirin zuwa biko, saiki tafi ki share gindi kiyi zaman ki?

Daker Aysha ta iya daurewa tace, keda ba zaman lafiya muke dake ba Ina ruwanki da zamana.

A'a, ai da baki wlh duk gidan babu dadi, koma dai yayane nafison dai kina gidan Koda zakita sani surutu ne, juyawa Aysha tayi domin dauko dayan akwatinta, yayin da Umma ta biyowata abaya cikin tsananin farin ciki take cigaba da fadin"

Wlh ba irin tunanin da banyi ba, nace to ko ubanki ya riki ne, inda ko ya rikeki wlh bazan yadda ba, ko sama da kasa zata hade saina amso ki, haba, naji ki shiru shiru, itama uwarki duk kawaicin ta saida tagaji tai mgn, zuwa wannan lokacin har sun shigo cikin gida.

Falon Umma ta zauna akasa tana fadin Ina mamana?

Mamanki yanzun sukaje dubiya ita da Murja.

Ajiyan zuciya Aysha take saukewa ahankali ganin babu wani alamun dake nuna cewa sunsan bataje gidan Daddyn ta ba.

Hira sama sama sukayi da Umma yayin da Umma keta nan nan da ita, wanka Aysha tayi tai sallah sannan tahau gado ta kwanta, abun da ya faru tsakaninta da Aliyu jiya taita tunawa yayin da take share hawayen gefen idon ta.

Wani irin bakin ciki takeji idan ta tuna tarasa budurcin ta, duk da cewa tana son Aliyu amman wani Shashi na zuciyarta ya shiga Jin haushin sa, musamnan idan ta tuna azabar daya gana mata duk da irin ihun da take zubawa be saurara mata ba ko ya tausaya mata ba har saida ya gama abun da yai niyya, wannan dalilin yake sata take danjin zafin sa cikin ranta saidai duk da haka batabar Jin sonsa ba.

Kuka tayi sosai tana daga kwance taji dawowan su mama ita da Murja, kasa kallon su tayi dan haka tayi lamo kamar me bacci.

Daga can bacci ya dauketa, bacci tayi sosai domin Daman akwai gajiya ajikin ta, yamma lilis ta tashi, tsakar gida ta samu Mama da Umma, Mamanta ta gaisar cikin tsanin fara'a Mama ta amsa sannan tace ya Baban ki?, ai mun dauka ya rike ki ne"

A'a mama nice bance zan dawo ba.

Yayi miki kyau, tunda Umma tana miki zancen aure ke Kuma baki so ko??, Yaya mgnr karatun naki me yace akai??

Mama yace zaizo da kansa kuyi mgn.

Yamutsa fuska Mama tayi, ni meye nawa, ai kin girma kema aiba yariya bace, ko dake ai zaiyi mgn.

Umma ce tace tunda yace haka ai shikenan, yazo din munajira.

Da daddare kasa bacci Aysha tayi Aliyu kawai ke fado mata, gashi tun da Aliyu ya kusanceta zazzabi ya sameta har yanzun batabar Jin zafin jiki ba, duk kuwa da maganin data sha.

Washegari Umma ta kula da yawan kwanciya da Aysha keyi dan haka ta mike tana fadin, " barin sa miki ruwan dumi kiyi wanka, na kula ke ragowa ce wannan dan tafiyan da kiya sai wani nan nad'ewa kike yi"

Cikin kankanin Lokaci Umma ta juyewa Aysha ruwan wanka, sosai taji dadi bayan tafito wankan maganin zazzabi tasha tare dana ciwon jiki sannan ta koma ta kwanta, kusan kwana hudu Aysha tayi akwance sannan ta fara zuwa islamiyya, sai dai ko a islamiyyar hankalin ta rabuwa biyu take yi, wani lokacin har a tashi bata fahimtan me ake yi, babban abun da yafi dama mata lissafi kusantanta da Aliyu yayi ne, gashi wani shashin nazuciyarta yana ce mata anya kuwa Aliyu zai dawo, fakar idon mutane take ta share hawaye ita kadai tasan me zuciyarta yake mata.

Satin Aysha biyu da dawowa suna zaune ita da Umma a tsakar gida wani yaro ya shigo yai sallama, Umma ce ta amsa tare da bin yaron da kallo.

Wai ana kiran Aysha, yaron ya fada tare da raba ido.

Cikin sauri Aysha tace babu Aysha anan gidan.

Umma ce tai saurin kallonta tana fadin, me kike nufi?, Kai jekace gata nan zuwa.

Juyawa yayi yayin da Aysha ke fadin, wlh saidai in ke kije amman ni bazani ba.

Mama nadaga daki takwala mata Kira Aysha?

Na'am.

Banson iskanci tashi kije.

Mama nace babu Aysha tace akwai, toh ita basai taje ba.

Wlh Aysha nasameki gurin nan ranki zai baci, sa'arki ce ita?

Mikewa tayi cikin kokarin yin kuka take fadin, wlh Umma nan kin cika hada rigima, ko Ina ruwanki dani oho, duk kinbi kinsa min ido.

Eh naji, Kuma bazan bar saka miki idon ba sai ranar da kika fidda miji kikayi aure.

Dan karamin hijjabi Aysha ta dauka tana fadin wlh idan wannan satin ya kare Daddy be zoba komawa zanyi yasani makaranta ni bawani auren da zanyi yanzun.

Ficewa tayi yayin da Umma tabi bayan Aysha da kallo tana fadin, Bilkisu wannan yariyar taki duk yadda akayi aljanu gareta bantaba ganin gandareriyar budurwa kamar Aysha dake kin aure ba har haka.

Umma rashin kunya ke damun ta, bata da komai tana sani, yanzun haka ita da babanta

suka shirya cewa bazatayi auren yanzun ba.

Cikin gamsuwa Umma tace toh Allah ya zama mana abun da yafi alheri.

Ranar da Aysha ta cika sati Uku da dawowa ta shirya zuwa gidan Babanta wannan karon bata dauki kaya ko kala daya ba, daya daga cikin hijjabinta da Aliyu ya saya mata tasa wadda yakai mata har kasa.

Mamace ke fadin, Aysha karki zauna kiyi sauri ki dawo.

Amsawa tayi, Kai tsaye gidan mahaifin ta nufa, acikin tafiyan da batafi ta awa daya ba ta iso.

Babban gida ne babu laifi, motarsa ta hanga tayi ajiyan zuciya duk da cewa daman tayi tunanin zata same shi a gidan.

Tana shiga cikin falon wasu yan mata biyu suka tasu suka rungumeta, itama rungume su tayi yayin da wani dan saurayi da bazai wuce shekara 16 ba ya roko hannun Ayaha yana fadin, har Daddy yace zai kawo mu gidan ku kin dade bakizo.

Wayyo inataso inxo makaranta ne ya hanani zuwa kuyi hakuri, karasawa cikin falon tayi yayin dataga Daddyn ta yayi saurin mikewa zai fice

Sakin hannun kannenta tayi tabi bayan Daddy tare da saurin riko hannun sa tana fadin, Daddy yi hakuri.

Batare daya kalleta ba yace nasan yau ma batan hanya kikayi.

Wlh Daddy gunka nazo, makaranta ne kawai yake hanani zuwa.

Wannan yaron ne yace Aunty ai kin gama makaranta fa Daddy ya gaya mana.

Hararan sa tayi kadan tare da fadin, ai mu kunsan muna zuwa islamiyya Sama'ila

Cike da gamsu Daddy yace toh kin kawo azuri, hannunta ya rike cikin murmushi yake fadin ya kike, Ina fatan kina lafiya.

Lafiya Lau Daddy.

Ina mutanen gidan ku, suma suna lafiya dai ko?

Lafiya Lau Daddy sunce in gaida ka.

Nagode, aini da nayi fushi dake nadauka da kika gama secondary zakizo kimana kwana biyu

Koda yake kinfi son mamanki akaina ko?

Daddy ba haka bane, karatu ne kawai itama tana ta cewa inzo.

Wani irin kallo yake mata me cike da nuna kauna yayin da 'yan uwanta mata biyu suita taba hijjabinta tare da nuna sha'awar su akai.

Hira sukayi sosai cikin yan uwanta da Daddy ta har yamma tayi sannan tai masu sallama har wannan lokacin mahaifiyar su Sama'ila tana gurin aiki.

Da Daddy da Sama'ila har kofar gida suka kawo Aysha, kudi Daddy ya bata tare ta tabbatar mata nan bada jimawa ba zata fara zuwa makaranta.

**********

Wai ke Aysha yanzun kin baci da bacci, bacin ki yayi yawa, wannan ma zuwa makarantar taki ai babu amfani.

Dagowa Aysha tayi idonta cike da Bacci, mikewa tayi ta fita ajin, can baya ta zaga ta zubar da yawon da ya taro abakinta  sannan ta matsa gurin tsofin dake saida abuwan ci ta saya garin kuka ta bude ta dau kwallo daya tasa a bakinta sannan ta koma ajin ta zauna.

Ina kikaje?, Wannan kawar tata ce ta tambaye ta.

Cike da fada, a Aysha tace, " kincika tambaya toh yawo na zubar to.

Yawu?, to yanzun me kike sha?

Kwallon kuka nasa a bakina dan idan babu komai cikin bakina yawu tarowa yake.

Lumshe ido yariyar tayi sannan tace, Aysha saikace me ciki?, Bacci, yawu, yanxun kuma ga garin kuka?

Wani irin mumunan faduwan gaba Aysha ta shiga, take jikinta ya fara rawa, saidai bataso kawarta Zenat ta fahimta dan haka tace, wani irin mgn ce wannan, me kike nufi"

A'a cewa nayi saikace me ciki.

Tsaki Aysha taja, tundaga lokacin ta fara kokarin hana kanta baccin duk da cewa kuwa yana fizganta, ana tashi ta nufi gida cikin tsananin damuwa tare da fargaba, sai a yanzun ta tuna, idan fa mace da namji suka kebe irin ke bewan da sukayi ita da Aliyu ana iya samun ciki duk kuwa da cewa sau daya ne,

Kafafuwanta ne suka kasa daukan ta dan haka ta nemi wani kofar gida ta zauna, idan tana kirgawa daidai yau kwananta sattin da uku da dawowa daga Nigeria Kuma har wannan lokacin bata sakiyin al'ada ba. bude murya tayi tace kenan Ina da ciki?

Tabbatarwa da tayi babu me bata amsa yasa ta shiga zubar da hawaye, daman shiyasa nake yawan bacci, shiyasa akoda yaushe bakina yake tara yawu, nashiga uku na, kuka taci sosai sannan ta tashi ta nufi gida.

Tunda zinat tai mata wannan mgnr ta fargar da ita, damuwa takeji sosai musaman data tuna batayi al'adaba tun wadda tayi wankansa aranar da Aliyu yasata a mota na farko.

Koda ta shiga gida ko gayan makaranta kasa cirewa tayi gado kawai ta haye yayin data kasa tsaida hawayen ta.

Ke Aysha meya sameki kika dawo agigice haka?, Umma ta tambaya tana bin Aysha da kallo.

Kaina ne yake ciwo Umma.

Allah ya sauwake barin dauko miki magani kisha, maganin Umma ta bata hartasha Takoma ta kwanta bata yadda sun hada ido da Umma ba, wani irin yanayi ta shiga me wuyar misaltawa.

Daddare tanajin su Umma da Mama sunata hira, itako tsabar damuwa ya hana mata Jin dadi, ayanzun gani take ashe dacan acikin ni'imar Allah take, bata da matsala yanzun ne take da gaggarumim matsala, waye zata gayawa wannan mgnr taji sanyi. Kuka taji tanasonyi sosai dan haka ta mike ta nufi toilet kukanta taci ta koshi ta fito idonta duk a kunbure.

Washegari kin zuwa makaranta tayi saboda karma asake mata irin zargin jiya, bacci taitayi har misalin 11 shima saida mama ta tasheta tana fadin, " wai Aysha wannan bacci naki na lafiya ne kuwa?🤔

Innawo ce tace, Nima naso in miki mgn, yariyar nan bata da lafiya tuni, karfin hali ne kawai dason makaranta kesata fita, amman bata da lafiya,inajin shawara ce baki ganin duk ta d'ashe.

Mama ce tace toh aiko dai barin je in nemo mata magani, tun da kikaga Aysha ta kwanta agida lallai ba karamin ciwo bane.

Aysha kuwa data juyar da kanta can gefe hawaye take sharewa tare dajin kunyan su Umma me tsanani daya shigeta har bata iya hada ido dasu.

Da yamma Umma ce ta dafawa Aysha maganin da mama ta sawo mata nasha Dana wanka, kwana uku tayi tana amman jikin Aysha Kara rikicewa yake yi.

Yadda Ayaha takejin damuwa yasa ta rasa abun yi, gashi babu wadda zaa gaya mawa taji sanyi dan haka ta fara tunanin gayawa Mamanta cewa wata biyu kenan batayi al'ada ba, sau uku tana zama gaban mama da nufin ta gaya mata amman saita kasa dan haka take Kara shiga cikin matsananciyan damuwa.

Yau sati biyu kenan Aysha tana kwance agida har wannan ranar Aysha bata bari su hada ido dasu Umma ba, wata yar kamar roba ta samu tana boyewa ta zuba yawun da yake yawan taruwa mata abaki.

*******

Innawo?

Na'am Fatima

Kinji wani labari da ake kishin kishin dinsa a unguwar nan kuwa?

Ai kinsan tsegumin unguwar nan yawa garai menene ya faru?

Yariyar nan Aysha jikar Umma, ana jita jitan tayi ciki.

Innalillahi wa inna ilaihir raju'un, Aysha fa kawar Husna mutunkyar Aliko?

Itafa Innawo, kinsan da Aliyu na kasar nan da yanzun ya shiga zargi.

Kwarai kuwa Allah ya rufa mana asiri, yana dai can ko wanni hali ake ciki oho,shekara biyar kenan, nasan fushi yayi kin sanshi da bakar zuciya.

Yaje yaita bakar zuciyar shi acan tunda be dauko mana mgn ba.

*****

Aysha zonan.

Ahankali ta tashi zaune tare da kallon fuskar mama, hannun mama ta sake kallo, robar da take zuba yawu tagani ahannun mama dan haka ta sake dagowa ta kalli fuskar mama, wani irin mummunan tashin hankali tagani a fuskar mama yayin da taji maman na fadin.

Ki sauko nace miki.

Sakkowa tayi ta tsaya gaban mama yayin da cike da tuhuma Mama tace daman jira nake Umma tafita intabbatar da zargina akanki, meye abakin ki???

*🕳️BA'KAR FURA🕳️*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

episode 41- 42

Cikin sauri Aysha ta sunkuyar da kanta ahankali ta shiga lankwasa yatsunta tare dayin kwalkwal da ido.

Magana nake maki fah, Ummi ta sake fadi cikin daga murya.

Kwallon kuka ne, Aysha ta fada cikin kasa dakai.

Kwallon kuka Aysha?, Yaushe rabon ki da al'ada kuma?😭😭

Dagowa Aysha tayi ta kalli yadda Ummi ke zubar da hawaye tai saurin sunkuyar da kanta tare da zubar ta hawayen itama.

Cikin matsanancin kuka Ummi kecewa, Aysha mgn nake miki Kar dai ace zargin da nake kanki ya tabbata Aysha😭😭

Hawaye kawai Aysha ke zubarwa tana lankwasa hannunta yayin da hawaye ke zubowa wani na kora wani.

Komawa bakin gado Ummi tayi ta zauna yayin da Aysha ke tsaye agabanta tana kuka sosai,

zuwa can Ummi ta dago idon ta jawur tace"

Aysha wanene yai miki ciki?

Kuka Aysha tasa yayin da tai saurin zubewa kan guiwowin ta, tana matsancin kuka?

Kinci mutuncin mu Aysha, kin zubar Mana da mutunci, kin bata mana tarihin gidan nan, tambayan ki nake ki gaya min, wanene yai miki ciki"

Cikin matsancin kuka Aysha tace Mama kiyi hakuri dan Allah. 😭😭

Kallon Aysha mama take tana zubar da hawayen takaici, wani irin bakin ciki takeji cikin kokon ranta tare da addu'ar Allah yasa cikin mafarki take ganin wannan abun ba gaske ba.

Aysha da gaske ciki gareki kenan?, Aysha da gaske kinyi cikin shege gina gida bakiyi aure ba?.

Mama kiyi hakuri dan Allah, nima bansa ni ba Naga dai kawai banda lafiya ne Kuma banga....

Kasa karasawa tayi tare da fashewa da kuka.

Shikenan Ayaha, bakomai, nagode Allah ya saka miki da alheri, bakiga al'adarki ba kenan kin san kina kefewa da wani, kinyi asara Aysha, kin lakata rayuwarki, kin Kuma zubar da kimarki da darajan ki ta 'ya mace, kin cuceni Kuma Aysha kin munafunceni, babu wadda zaice Zaki aikata, ashe kina kula samarin ki na banza ne?, ashe kina zuwa ki mikawa wani kanki sabodake baki da lissafi Ashe....😭😭

Mama wlh sau daya ne😭😭😭

Wani irin bakin ciki ne ya cika mama wadda yasata ta dauke bukitin karfen dake kusa da ita ta wurgawa Aysha, cikin tsananin bacin rai Ummi tacigaba da fadin, " fice kibani guri banson ganin ki agaba na.

Cikin matsanancin kuka Aysha ta durkushe akasa yayin da hawayenta ya dame da majina tace mama kiyi hakuri dan Allah 😭😭😭.

Idan kika sake bani hakuri saina sa itace namiki dukan mutuwa, dan Ubanki waye yai miki ciki?

Sheshekar kuka Aysha keya idonta akasa, tabbatarwa da Ummi tayi Aysha bazatayi mgn ba yasata ta mike kawai ta shige daki tare da turo kofar.

Itako Aysha nan tsakar gidan ta zauna dirshen akasa taci kukanta me matsanancin karfi ta bude murya, saidai harta lafa babu wadda yace mata ci kanki.

Zuwa can ta fara yunkurin amai, dan haka ta mike aguje ta Isa gefen fanfo, kwarara amai. bayan ya lafa ta shiga wanke jikinta Sam babu kwari ko kadan.

Can gefen kitchen Aysha ta koma ta kwanta a kasa tare da curewa guri daya, hawaye ke xobo mata tana sharewa.

A lissafinta saura kwana Ashirin da biyu yau wata ukun da Aliyu ya fada su cika, idan yazo zaiji mummunan Ibr, 😭😭, idan yaji Inai yaya zaiyi?,😭😭 Me zaici?, Nasan bazaiji dadi ba, wata zuciyar ce tace toh yanzun idan bezoba fah🤔, shikenan nikuma na shiga uku na.😭😭😭

Tana cikin wannan kukan Umma ta dawo, kallonta tayi cikin tausayawa tace Aysha jikin ne?, Meyasa Zaki kwanta akasa ko tabarma babu?

Bata samu amsa ba domin sabo da kukan dake cin ranta ko mgn bata iyawa.

Dan haka Umma ta shiga kwalawa Ummi Kira, Bilkisu ke Bilkisu haka ake jinya ki shige daki ki rofe kofa?

Jin Mama bata amsa ba yasa Umma ta nufi dakin cikin fada ta tura kofar.

Ke Haka ake jinya, Ina mgn kinajina?, Kallon fuskanta yasata hadiye zancenta, sosai ta tsura mata ido cikin tsananin faduwan gaba tace menene?, Lafiya kuwa?

Ki zauna Umma, murya adashe tai mgna dan haka Ummi ta zauna dambar akasa har yanzun idonta akan Mama.

Umma Aysha ba shawara bace ke damunta kamar yadda kike tunani, Umma Aysha ciki gareta.

Dafe kirji Umma tayi tare da fadin, Innalillahi wa inna ilaihir raju'un, ciki?, Cikin haihuwa?

Kukan da Ummi keyi yasa ta kasa amsawa Umma yayin da Umma tai saurin mikewa tana fadin, munshiga uku acikin unguwar nan amman kuwa Aysha akwai matsiyaciyar yariyar, kitchen Umma ta nufa yayin da ta dauko wani katon itace tayo kan Aysha dake kwnce, ita ko Aysha awannan lokacin bata da karfin tashi dan haka Umma tashiga dukanta da itacen tana fadin wani dan iskan ne yai miki ciki?

Dukanta Umma ketayi babu me ceton ta, yayin da Aysha ko ihu bata iyawa kare fuskarta kawai take da hannunta hawaye na tsiyaya akan fuskarta.

Dan kanta tagaji tabari domin Aysha bata gudu ba, Ummako sai haki take cikin tsananin bacin rai tace, aiko saidai ki tattara kayanki kibar gidan nan dan baza'a haifarmin shige acikin gida ba, ke Bilkisu kifito ki tambayeta ta gaya miki wadda yai mata cikin, idan ba hakaba wlh saidai tabar gidan nan, munafukar yariya kawai wadda zuciyarta babu alheri, haba, gaskiya naga makota namin wani irin kallo, aahe kallona kawai suke inata shela a unguwa shawara na damun jikata ba'azo aka duba min ita ba, shikenan tafaru ta kare, Aysha wlh kinyi asara, kinyi asara duniya data lahira kina abu kamar bakisan komai ba ashe duk munafuncine, kije kin bude ma wani takon kawai kafafuwa ya gama dake, tirrrr wlh tirrr baki dauko halin uwarki ba, shegiya fitinanniya, kinsan auren kike so meya hana ki nuna Mana, a'a ke munafunci kika sa gaban ki, Zaki fadamin dan iskan naki koko saina tara miki jama'a?

Sosai Aysha ke zubar da hawaye ganin da Umma tayi Aysha ba mgn zatayi ba ta mike ta zari gyalen ta tai waje tana cigaba da masifa.

Aysha kuwa na nan zube, yau wani irin amai take kwarawa wadda ta rasa Kona menene, tunda tafara ciwo bata tabayin amai ba saiyau, da akasan da cikin. wani irin ramewa tayi rana daya.

Umma kuwa kusan awa daya ta share sannan ta dawo sauran 'yaranta mata har uku suna minta abaya, biyu yayyen mama ne sai Kuma aunty Murja wadda kebin Mama.

Nunata Umma tayi da hannunta tafadin ga watsartsiyar nan, kuyita dukanta harsai ta fada maku dan iskan dayai mata ciki.

Tashi Aysha tayi zaune yayin da Yan uwan mama suka zagaye ta saidai yin duniya taki mgn kuka kawai takeyi dan haka suka shiga surfa mata zagi, wasu nakai mata duka.

Sosai fuskarta tai jawur saboda Marin da suka yanyanka mata, ayanzun radadin fuskar kawai takeji zuwa wannan lokacin hawaye ya kafi a idonta sai sunkuyar dakai kawai take yi.

Mamace ta fito tana fadin ta fada maku wadda yai mata?

Inafah?, ai kinsanta da kafiyan tsiya, wlh yariyar nan Sam bata da mutunci, tantiriyar yar iskace, saboda bakin hali tabude baki ma tayi mgn ya gagareta shige barbadadiya.

Ai maman Sadam kuita dukanta har sai ta sumai.

Weadda Mama takira da maman Sadam ce tace, " me cikin ?, Idan jini ya balle mata fah"

Ummace tace duk abun da zai faru ya faru, ni wlh ko mutuwa Aysha tayi yanzun bani da asara.

Hada baki sukayi wajen fadin, wlh da haihuwar Aysha gara barin ta.

Tafarfasa kawai zuciyar Aysha kiyi, kuka ya bushe cikin idonta, haka gidan Umma ya zama kamar gidan makoki wasuma acikin su kwana suke, babu irin tambaya da ba'a ma Aysha ba taki fada, duka kuwa da Zaki marasu dadi babu irin wadda bata Shashi ba, har takai gaba daya masa mgn da ita bare ma har akara mata tambaya kowa tirrr da halinta kawai yake, dan haka arakube take acikin gidan, babban wan Mama ma cewa yayi ahada mata kayanta taje duk inda zataje, mama ma haka tace, ta tafi gurin wadda yai mata cikin ita ko ganinta bata son yi.

Sosai Aysha ta cansa nan danan ta fita cikin hayyacinta, wuya take shan ba kadan ba Koda yaushe yawo cike fal da bakinta, ga yawjun sun abubuwa saidai babu me bata haka take hakuri har aka dauki tsayon sati biyar.

Har wannan lokacin babu mema Aysha mgn acikin gidan, abincima saidai ta faki idon Umma ta diba, Mama ko ko kallon inda take batayi, dan haka duk ta rame ta lalace, zuro zuro tayi har yanzun laulayi bebarta ba kamar ma karuwa yake.

Yauma Ayaha ce kwance adakin mama, wadda tun ranar da Akasan tana da ciki takoma kwana cikin sa, Mama dakin Umma ta koma domin tace ita ko son ganin Aysha batai.

Sati Uku kenan Aliyu ya Kara akan lokacin da yace zaizo, amman har yanzun babu alamarsa, tun ranar da yacika wata uku kamar yadda yace yake saka ran ganin sa, kullum zura ido take ganin har andau sati Uku bayan ranar da yace yasa hankalin ta duk ya tashi, kuka taci sosai, yanzun kam tacire rai da zuwansa, harma ta fara ganin rashin hankalin ta data debi kafa tabishi can, ahankali tace gashi yanzun ya barni da ciki Kuma yaki zuwa kamar yadda ya min alkawari.

Sosai taji ta shiga jin haushin Aliyu me tsanani, gashi cikin sosai yake wahalar da ita, kasa kasa take fadin, shikenan zan haifi shege wadda zai dawwama babu Uba domin yanzun Aliyu yana ma iya cewa banashi bane tunda kowa yasan baya kasar nan, wayyo ni Allah nashiga uku😭😭

Kuka tayi sosai duk idonta ya kod'e bakinta ya bushe.

Ita kadai azaune a tsakar gida ji tayi tana son ta sha kukar fulani, dan haka ta mike tasa hijjabi ta fita, hanyar gidan su Aliyu ta nufa tun kafin ta karaso take bin gidan da ido, sosai taji ta tsana ko ganin gidan dan haka tai saurin dauke kanta, har ta sawo ta dawo bata sake kallon gidan ba .

********"

Ina kikaje?

Wani irin faduwa gaban Aysha taji tunda taji muryan Umma, Dan ta dade bataji ta mata mgn ba.

Ledan Hannunta ta nunawa Umma cikin sunkuyar dakai tace wannan na sawo.

Umma taji tana fadin, " Bilkisu yariyar nan fah batasan zuru ba, idan mukayi wasa saidai muji inya, lokaci yayi daya dace ubanta ya sani, lallai kije ki same ubanta asan abun yi.

Mama batace komai ba har Aysha ta shige daki.

Misalin biyar na yamma taji Muryan Daddy ta acikin gidan dan haka jikinta duk ya kama rawa domin tunda tasan Daddyn ta bata taba ganin bacin ransa ba dan haka ma yanzun duk jikinta ya dau rawa.

Ke! Aisha fito ga Baban ki?

Fitowa tayi tana sanye da hijjabi Daddy na hango Aysha ya yamutsa fuska yana fadin"

Lafiya?

Umma ce tace matso nan ki zauna ki gaya masa.

Kallo Daddy yake kare mata sama da kasa duk ta rame ta d'ashe idonta duk sun zurma yace Aysha menene ya same ki??

Wasa Aysha ta fara da yatsunta yayin da wasu hawaye masu zafi suka shiga zubo mata.

Juyawa yayi ya kalli Umma yace Meya sameta?

Ciki tayi.

Cikin sauri ya runtse ido, sannan ya juya ya kalli Aysha yana fadin, " cikin haihuwa ?

Kuma anyi anyi ta fada wadda yai mata ta ki, duka ba irin Wanda bata sha ba amman takk mgn, amman taki mgn.

Daddy ne ya sake cema Aysha, Aysha waye yai miki ciki?

Har yanxun bata dago ba kuma batar wasa da yatsun ba hawayenta kawai yake gani yana diga, dan hska ya mike yaje gabanta cikin tsananin baccin rai ya watsa mata mari.

Sosai zafin ya rudata tana jinshi acikin kanta taji Daddy ya sake cewa, "

Bazaki bude bakimin mgn ba?

Durkushewa tayi cikin matsanancin kuka take cewa, Daddy kayi hakuri, wallahi Nima bansan kowaye ba, 😭😭 dan Allah kuyi hakuri ku yafe min.

Wani irin kuka take me shiga rai dan haka Daddy ya Isa gabanta ya dagata, kirjinsa ya sata rungumeta yayin data tsananta kukan ta, ahankali Daddy ke share hawaye yayin da take dafa bayanta cikin sigar lallashi, sosai ya rungumeta zuwa can ya dago ya sunbaceta sannan ya rike hannunta ya kalli Umma yana fadin, " Umma bari muje muyi mgn nida ita kawai.

Toh kaje, ka tirketa ta fada maka idan ba hakaba kuwa ni bame haifar min d'ana shege agida....

*🕳BA'KAR FURA🕳*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

Episode 43- 45

Rike da hannun Aysha suka fito, cikin motar yasata, suka bar unguwan, wani asibiti yakaita bayan an tabbatar masa da Aysha tana dauke da cikin daya kusa cika wata 4.

Baro Asibintin yayi cike da tashin hankali daker ya Isa saita kansa ya juyo ya kalli Aysha dake matsanan cin kuka yace' " ba kuka zakiyi ba Aysha, bude baki zakiyi ki gaya min wadda yai miki, ba zancen rigima bane ko tashin hankali, abun bukata kawai yasan da cikin, Kuma ya amince cikin nashi ne, matsala anriga an sameta, kuskure Kuma an riga anyi, waye ne Uban cikin?

Daddy kayi hakuri dan Allah, wlh basani ba.

Baki sani ba?, Kina nufin baki san waye yai miki cikin ba?

Kaita daga ahankali.

Shiru Daddy yayi tare da tsurawa guri daya ido tsayon lokaci sannan yace, " shikenan, idan cutarki akayi Allah ya saka miki,ya Kuma kawo miki mafita, idan Kuma kece nan kika Kai kanki, toh sai nace miki ki nemi sunan da Zaki Kira 'yarki ko danki, sannan ki neme amsar da Zaki bawa abin da kika haifa aduk ranar daya tambaye ki ubanshi, inason ki sani, idan baki yi mgn yanzun ba bayan kin haihu babu wani mataki dazan iya dauka, baza 'a zubar da cikin nan ba kamar yadda Kakarki ta bukata dole saikin haifi shi.

Kuka Aysha keyi sosai, bayan sunyi tafiya me tsayo ya tsaya yai mata sayayya sannan suka kama hanyar.

Zuwa can yacigaba da cewa, " naso ki zama kamar mamar ki, maman ki yariya ce me nutsuwa, akanta nafara sha'awan musulunci, Kuma har yanzun itace ta gujeni bani ne na gujeta ba, ke ko yanzun waye zaiso dansa ya aureki, har dai yaji abun da kika aikata?, Kin bata wayaun ki, mutanen unguwar ku, zasu dinga yin tirrrr dake, shiru yayi tsayon lokaci sannan ya sake cewa,  kina sa hijjab kina Sallah, kince amiki aure ne ba'a miki ba?

Gargiza Kai tayi idonta cike da hawaye.

Koko akwai wannda kike so ne ban sani ba?

Nan ma hawaye ne suke zobo mata tasa hannun ta share tare da girgiza kai.

Daddy ne ya sake fadin, Ina tsananin son ki Aysha, amman ga abun da kika min, duk cikin 'ya'yana nafi son ki, Ina alfahari dake Amman kinje kinyi abun da mutane zasu min dariya dangina sun dade suna min korafin nabarki kina Islam, kinci amanata bantaba zaton haka daga gareki ba.

Daddy kayi hakuri dan girman Allah ka yafe min.

Ya zanyi dake, Allah ya rabaki da cikin lafiya ya Kuma kawo miki mafita.

Daidai wannan lokacin suka Isa kofar gidan, Aysha agaba, Daddy ta nabinta abaya suka shiga gidan, dakinta ta nufa yayin da Daddy ya nufi dakin Umma.

*******

Batasan Kona waye ba???, Aysha fa da kake ganinta munafukar yariya ce, munafunci ne cike da cikinta, nafi ganin a tutsuyeta ta fada, idan ba'ayiwa tufkar hanci ba ko, anrabata da wannan tana iya kwason wani, ba fata nake mata ba, Amman wlh idan ba wani ikon Allah ba zata jima bata auro ba.

Umma wannan yana daya daga cikin dalilin dayasa nace abarta da cikin, idan aka cire cikin kamar an bude mata hanya ne, idan ko aka barta dashi shine zata fahimci illar abun, annan zata gane inda matsalar take, dan haka nake son kuyi hakuri mu rungume wannan kaddaran.

Cikin sauri Mama dake kan gado tace, " aikuwa saidai ka wuce da ita, baza'a haifi wannan kazantar anan gidan ba.

Kashhh, Daddy ya fada, kuyi hakuri Aysha tacigaba da zama anan, jama'ar unguwar ku sun riga sunsa ni, tafiya da ita kamar Kara baza zancen ne, dangine sun dade suna korafin nabarta tana musulunci yanxun suna Jin wannan lamarin dariya zasuyi, nafi ganin muyi hakuri kawai.

Duk ta yadda Umma ta fillo Daddy toshewa yake, har dai suka yadda sannan yai masu sallama tare da jadda masu zai ringa zuwa akai akai.

******

Ai kullum Kara godewa Allah nake da ya daddara Aliyu baya kasanan, da yanzun an jingina mana shege.

Hmmmm, aini nayi farin ciki nagodewa Allah, Kinga yayi zamansa shima yanzun ya samu abun da ransa ke so, sai dai fah yaci ace zuwa yanzun ya waiwaye mu.

Bazai zo ba, ai kin sanshi da bakin rai, yana can yana fushine ne, yasha zamanshi idan zai yi aure naje ni.

Dariya Innawo tayi, aifa yai zaman sa fitina bata da dadi, duk da dai yanxun kam ya girma nasan yayi hankali.

******

Tundaga ranar da Daddy yazo su Umma suka Dan rage zafin su akanta, ayanzun suna bata abinci, saidai ko taci ko kartaci babu abun da ya dame su, sannan yawancin abincin nasu bashi take so ba, tsananin damuwar da take ciki be barin ta taci abincin, haka har cikin ya shiga wata na biyar, har wannan lokacin acikin 'yan uwan mamanta aunty Murja ce kawai take mata mgn, kowa harara ne da zagi tsakanin su.

Sosai rashin zuwan Aliyu har wannan lokacin yake dagula mata lissafi, ashe bazai zoba, amman yace min in bashi wata uku, gashi har yanzun shiru, besan da ciki ba, nasan ko yanzun yazo bazai karba ba, dan haka babu amfanin Kiran sunan shi, shekaran sa biyar baya kasar nan yana cewa karya nake shikenan ta zauna, kowa cewa zaiyi sharri zan masa tun da narasa uban cikina, kuka ta kwana tanayi wadda yai dadlili Kafin safiya ta tashi da matsanancin ciwon mara me tsanani.

Ganin tun safe Aysha bata leko ba Mama ta faki idon Umma ta shiga dakin.

Yau Yaya dai?

Mama cikina ne ke ciwo.

Allah ya sauka ta fada sannan ta fice, ganin har anyi azahar Aysha bata fito ba yasa Mama ta koma dakin.

Kudi mama ta mika mata amshi kije asibiti.

Daker Aysha ta iya mikewa tana tunanin ta Ina zata fara zuwa asibiti ita daya.

Tana fitowa layin aka fara binta da kallo rabon data fito ta manta, dan haka taji sai hardewa takeyi, daker ta karasa gidan.

Da fada aunty Murja ta rufeta dashi, meyasa tazo mata gidanta, acewarta bata son mijinta ya sani.

Irin wannan abubun sunyiwa Aysha yawa Dan haka saita yi da gaske hawaye ke zuwar mata.

Meya kawo ki?, taji muryan aunty Murja bayan ta gama fadan.

Cikinna ke cewa shine na fito inje asibiti.

Ba dole cikin ki yai ciwo ba, kina sane sarai, cikin ki ya girma, ko bakici abinci Dan kanki ba dole kice sabo da abun dake cikin, yunwace kawai take damun cikin.

Cikin sauri Aysha tasa hannunta ta dafa cikin, jinsa tayi ya cure guri daya, sai yanzun ta tabbatar eh lallai me raine acikin ta.

Kunun gyada Murja ta damawa Aysha tashashi da lumishi, yayin da tana gamawa bacci ya dauketa.

Bayan ta tashi ruwan wanka Murja ta bata tai wanka sannan ta kamo hanyar gida tana mejim dadin jikinta ba kama sanda ta fito ba.

********

Sannun ahankali kwanakin suke juyawa zuwa watanni, ayanzun cikin Aysha ya cika wata 9, wani irin girma yayi naban mamaki, tuni tabar saka kayanta domin duk sun mata kadan, Kuma har cikin ya tsufa nan wuya kawai take sha, bama kamar daya girman nan yafi bata wahala, zama daker tashi dake babu wani me taimakonta, komai ita takewa kanta har wannan lokacin da ta tabbatarwa kanta cikinta ya kusa fita.

Babban abun da yafi kona mata rai shine watanta tara da dawowa Nigeria amman har yau wata ukun Aliyu basu cika ba, wani irin zafi sa takeji fiye da misali, sosai ranta yakebaci data tunashi domin kuwa yanxun ta tabbatar ya yaudareta, cikin matsanancin kuka ta shiga rokon Allah ya dauki ranta wajen haihuwar ita da cikin baki daya, saidai tana addu'ar tanajin yadda dan cikin nata ke zillo kamar zai barka cikin.

Cikin matsancin kukan da sai zuwa yanzun hawaye ya fara zubo mata tace, "ya rabbi na rokokeka, ko a lahira karka hadani da Aliyu, Allah kasa nagama ganin shi kenan har rayuta ta kare, Allah ka hanini ganin duk wani abun daya shafe shi barema shi da kansa. Mugu kawai azzalumi wadda besan girman alkawari ba, yasan ya cuceni shiyasa bazaizo ba.

Cikin matsancin kuka take Kiran sunan Allah tare da addu'ar ya dauke ranta ita da dan cikin nata.

Bayan Sati biyu ta tashi da matsanancin ciwon mara.

Murkususu take tun safe har rana tana saman katifar ta, ganin har rana tayi, Mama ta tashi ta leka dakin tana fadin ke lafiya kuwa!

Mama marana ke ciwo.

Lumshe ido Mama tayi tare da fadin, Bismillahir rahamanir rahim, Allah nagode maka daka jarabceni da ganin wannan mummuna al'amari wadda bame dadi ba agareni.

Umma ce tace lafiya?

Aysha nakuda take yi Umma.

Munshiga Uku,, naka takaine Yaya zamu yi?

Umma ko asibiti zakuje?

A'a ai batai awo ba, adai Kira mata unguwar zoma.

Umma, Amman kinsan Innawo ce kadai keyi anan haka, Kuma Innawo nasan bazata zo.

Gyale Umma ta dauka tana fadin kedai Ina zuwa.

**********

Innawo karkije dan Allah, lallai ma matar nan bata da Kunya ko kunya bataji ba ta iya tskowa gidan nan meya hana sukaita asibiti.

Bakomai Fatima barin je, wlh taban tausayi, zanje idan naga da matsala zance suje asibiti, idan ina iyawa Kuma zan amsa, ai da nakowa ne.

Kofar gidan Innawo ta nufa yayin da Ummi ke fadin, kashh, dan Allah Innawo ki dawo karkije.

********

Wani dan karamin littafi ya bude, ya zubawa shafin ido sannan ya mayar ya rufe, mikewa yayi ya dauko a kwatin sa tare da zuba kayansa aciki ahankali ya mayar ya rufe, yana daga tsaye ya zuba hannun sa duk biyun cikin aljihu, guri daya ya tsirawa ido, bakin gilashi sanye a idon sa  cike da kwarin guiwa yake sauke ajiyan zuciya.......

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

episode 46- 47

Da Sallama Innawo ta shiga gidan, yayin data samu Umma rike da Aysha acikin dakin Ayashan, cikin nuna kwarewa Innawo tace, "haihuwa ce , abani leda da reza"

Cikin sauri Umma ta fice adakin tare da daukan gyale tai waje, bata jamaba ta dawo dakin.

Sosai Aysha ke murkususu Innawo na mata sannu su biyu a dakin.

Murkususu take yi tsayon lokaci tare da share hawaye, sosai tagaji iya gajiya, ciwo takeji bana wasa ba.

Innawo kuwa fadi take daure dai Aysha.

Kusan awa uku aka kwashe ana abu daya, ganin mangariba na gabatuwa Shiru babu wani Ibr yasa Hankalin Mama ya tashi sosai, wani irin tashin hankali takeji, Daman yadda cikin Aysha ya girma abun tsoro yake bata.

Bayan isha'i ne abun ya tsananta, daga dakin Umma tana jiyo nishin Ayaha, Innawo kuwa tana rike da Ayaha tana mata addu'ar neman sauki tare da sauka lafiya, kokarin yariyar tagani sosai.

Misalin tara da rabi na dare kan dan ya fara turowa, cikin kwarin guiwa Innawo ke fadin, " yauwa Ayaha, kadan ya rage, yi karfi da jikin ki saura kadan ya fita ki huta.

Wannan mgrn ta Innawo ke karawa Aysha karfen guiwa cikin ikon Allah jaririn ya gama fitowa tare da uwar gaba daya.

Ajiyan zuciya Ayaha ta sauke, hakika haihuwa akwai raradi wadda bashi missaltuwa yanzun ji tayi kamar an zare mata ciwon.

Innawo kuwa harta yanke ciben ta nade abin da aka samu cikin zanin Aysha yayin da gidan ya karade da iho, Umma ce ta shigo tana tambayar Innawo ta sauka ne, cike da kwarin guiwa Innawo tace ta sauka ga danta nan kwaton gaske.

Hmmmm, kawai Umma tace sannan ta juya ta fita.

Ganin haka Innawo ta tsaya ta gyara komai tare da wanke kayan da aka b'ata, ganin inda Umma ke shashsharewa Innawo tace abata ruwan zafi tama yaron wanka.

Nan danan ko Umma ta kawo ruwan, bude yaron Innawo tayi tana kokarin saka shi aruwan wankan take fadin, wai, wannan yaron baki ne, beyo farin uwarshi ba, juyawa tayi ta kalli kunnen yaro sannan ta kalli keyarsa, zabura Innawo tayi tare da dan zaro ido.

Mamace ta shigo ta fita da Aysha domin yi mata wanka, dan haka Innawo ta shiga duba yaron dakyau.

Gani take kamar Aliyu ne yayi kaki ya tufar, cikin tashin hankali ta furta Innalillahi wa inna ilaihir raju'un, wannan yaron bashi da banbanci da Aliyu, haka yake sak lokacin da aka haifeshi, katon gaske ga tsandara ihun tsiya, haka wannan yaron tunda yazo duniya be rufe baki ba Kona sakan daya.

Cike da rude Innawo ta shirya yaron cikin wani kayan sanyi da Umma ta kawo.

Gashi an samu karuwa Amman Umma da mama zuciyar su babu dadi, fitowa Innawo tayi adaidai lokacin da Aysha ta fito wanka, godiya Umma tai mata sannan ta fita ta nufa gida.

Har Allah Allah Innawo take ta Isa gida, dumin hankali ta atashe yake, lokacin har Ummi ta kwanta dan haka tasa hannunta tana buguntа tana fadin, Fatima tashi ki zauna.

Innawo sai yanzun kika dawo, tun rana ko lekowa gida ki koma bakiyi ba fa.

Katseta Innawo tayi da fadin, "ke Fatima ba wannan ba, akwai matsala"

Matsala wacce iri Innawo?, bata haihu bane?

Ta haihu, ki zauna dakyau nace miki.

Gyara zama Ummi tayi tana daga bakin gado.

Innawo ce tai kasa da murya tace, "dan da Ayaha ta haifa kamar Aliyu ne yayi kaki ya tofar"

Dirowa Ummi tayi daga gadon, tsintan kanta tayi akasa wanwar, Innawo ban fahimceki ba?

Hmmmm, Fatima yaron kama yake da Aliyu, kama bana wasa ba.

Innalillahi wa inna ilaihir raju'un, Innawo dan Allah ki bari, kin manta shekaran Aliyu biyar baya kasar nan gaba daya?, Innawo karki sake fada, bazamuga shege ba insha Allahu, Aliyu bazai haifamana  dan xina insha Allahu.

Ai saidai Kar akuma Fatima, amman duk inda akeje aka dawo wannan yaron namune ko shakka bana yi.

Innawo kiyi shiru dan Allah, kibar jingina mana shege, kamace kawai tai yawa.

Shiru kawai Innawo tayi domin bata son jayayyan nan da Ummi ke yi.

******

Wannan abun bakin ciki dame yai kama, ni dan takaici ma na kasa kallon yaron, ita kanta Aysha yaron kwana yayi yana tsandara ihu taki daukan kasa, danaji najin da jin kukan sa nace mata tashi ta bashi nono sai tasa min kuka, haka muka kwana ita tana kuka danta nayi, ba irin abin da ake gudu kenan ba, yanzun da aure ne ya kawo wannan yaron me shegen kwakwazo haka nan zamuyita ririta shi, amman wlh yanxun danaji muryan yaron sai inji kamar in hadiyi zuciya in mace.

Kawar dakai mama tayi tare da fadin, tana daukan alhakin yaron ne, shi meye nashi nashi? adolenta ta shayar dashi. ni yanzun abun dake cimin rai ace wai Aysha ta rufe ido tace ita Sam batasan uban yaron ba, wlh Umma ban yadda da wannan ba.

Ita ta jiyo, yanxun dai ai ga tukuicin rashin Jin mgn nan Allah ya bata, idan ta yaye shi idan Allah ya bata miji ko wanni iri ne sai a kukuta ta tafi, hankalin mu ya kwanta.

Umma waye zai aureta da yaron?

Indai ta samu mijin saidai tabar Dan nan dan musamu ta zauna agidan mijin cikin kwanciyar rai.

Saidai ubanta ya dauka, wlh ni Umma ko ganin dan bani kauna.

Ai kiyi hakuri kawai, indai ba Koran Aysha zamuyi ta shiga duniya ba toh rayuwa da danta yazamar mana dole, Kinga lokaci na tafiya barinje ingayowa 'yan uwanki, ke Kuma kije ki ma yaron wanka ga ruwa can ya gama dahuwa har gurin babanta zanje.

A'a Umma kibari abawa abawa iro kudin mota yaje duk ya gayo masu, ni bad'an dazama wanka.

Jimmm Umma tayi sannan tace toh shikenan.

Mikewa Umma tayi ta debi ruwan zafin ta koma dakin, itako Mama gyale ta dauka ta nufi waje domin aika iro.

*****

Wai har yanxun kukan kike?, ai wannan kukan beda amfani, kuma d'an ba laifinsa bane ki dauke shi maza kibashi nono, kafin asashi a ruwan wanka.

Karawa kawar dakai Aysha tayi, dan haka Umma ta nufi dan ta dagoshi ta daura cinyan Aysha dake zaune sannan tagama hannun Aysha ta tallabo kan yaron dake ta tsandara uhu, kallon Aysha Umma tayi tace toh fito da nonon kisa masa abaki.

Hawaye kawai Aysha ki zubarwa yayin da kukan yaron ya dami Umma dan haka ta daga rigar Aysha ta ciro nonon tare dasa hannunta ta Kara dago kan yaron dumin nonon yasamu shiga bakin sa, carab kuwa ya rike nonon tare da fara tsotsonsa bada wani bata lokacin.

Jin yaron yayi shiru yasa Umma takai idonta fuskan yaron tana fadin, " kin bani da tsotso ai ku......

Cak ta tsaya tana me karewa yaron kallo, Rabon data tuna Aliyu ta mance, dagowa tayi ta kalli Aysha dake hawaye sannan ta kara maida idonta kan yaro, idonta akan yaron take fadin, " Bilkisu fito ki gani!!, Bikisu kina ina!!

Tunawa tayi Mama ta fita dan haka tamaida hankalin ta ga Ayaha tare da fadin, "wannan yaron uwa Aliyu aka zuke ya zama 'kankani. Duk yadda akayi Aliyu nashigowa garin nan, shiyasa kikace baki san wadda yai miki cikin ba.

Kawar dakai Aysha tayi har yanxun hawaye na zubo mata ga wani irin faduwa dataji gabanta nayi tunda Umma ta Kira sunan Aliyu.

Cikin wani irin yanayi Umma tace, " rike danki, kan yaron Aysha ta kama yayin da Umma ta matsa can gefe tana kallon Ayasha sannan ta juya ta kalli yaron tsayon lokaci ta dauka ahaka sannan Umma tace akwai tashin hankali agarin nan, wlh wlh bazan yi shiru ba, kowa yaci tuwo dani miya yasha, Sam bazan yadda ba.

Mama ce daga waje take fadin, " Umma Yaya aka yi?

Ai tana kwala miki kira, shigo kiga Aliyu a hannun Aysha, wallahi wannan yaron na Aliyu ne, ko kaffara banayi jikan Innawo ne.

Cike da sauri suka shiga dakin gaba dayan su, Maman Sadam da Murja Koda suka kalli yaron salati. Suka fara, Aysha kuwa kawar da fuskanta kawai take babu bakin mgn.

Maman Sadam ce ta fige yaron daga hannun Aysha ta fice adakin yayin da aunty Murja

da Umma suka rufa mata baya.

****"

Innawo ki daina damun kanki, Ina kallon ki Innawo bakiyi bacci ba da daddare, ni Ina da tabbacin abun da nake fada miki ko kina ganin Aliyu zaizo garin nan ne ya juya batare dayazo nan ba?

Nima abun da ya tsaya mun arai kenan Amman fa Fatima koma dai ta yaya ne yaron nan na Aliyu ne, domin har kafa, hannun, ido, baki hanji ke har sumar kan yaron irin na Aliyu ne, yadda kikasan Aliyu sanda yazo duniya haka garon yake.

Innawo ki kwantar da hankalin ki, ni Ina da tabbacin banasa ban.....
.

Har gowan mutane yasa suka maida kallon su ka kofar shigowa gidan, inda Maman Sadam tai saurin daura yaron kan cinyar Ummi tana fadin, ki duba kiga abun da danki ya shuka.

Mikewa Ummi tayi rike da yaron tabas taga kamar da Innawo ke fadin, cikin azama ta shilla yaron yayin da Murja tai saurin cabewa tana zare ido, cikin zaro ido Ummi ke fadin nafiku hauka, wato yarku ta haife d'a kun rasa inda zakiyi dashi zaku kakaba Mana, toh duk inda za'aje aje bazan taba yadda ba, shekaran Aliyu biyar kenan kwarara baya kasar nan, kowa cikin unguwar nan yasani tunda Aliyu yasa kafa yabar gidan nan be sake lekowa ba, dan haka bazan taba karban dannan ba, ko sama da kasa ce zata hade, 'karyar bala'i kuke yi.

Ai kuwa kowa ya kalli yaron nan yasan na Aliyu ne, Umma ke fadin haka tana me nuna yaron.

Ummi ce tace, " Inna hujar take?, Kije ki nemo hujja ki kawo, idan ba haka ba wlh zanyi karan ku.

Jiki babu kwari suka fita domin dai basu da wata hujja suna komawa suka tarar Baban Aysha yazo da kaya niki niki, Aysha kuwa har wannan lokacin kuka take yi nan suka shiga gaya masa duk yadda aka yi.

Kawar dakai yayi tare da fadin, "aina gaya mata, ita yakamata ta bude baki tai magana tuni, nayi nayi da ita taki, tunda batai mgn ba kuwa Nima bani da ita, dan haka ku rabu da ita.

Sallama ya masu akan da yamma zai dawo , bayan tafiyan sa yaran Umma duk sun hallara dan haka suka Kara yanke shawaran akara komawa da yaron gidan Innawo.

Lokacin da suka Isa tunkafin su shiga gidan Alhaji Umar ya taresu, domin harda maza cikin su, anan Alhaji Umar ya kara tabbatar masu da bazasu karba ba domin babu wata hujja da

ke nuna Aliyu yazo garin nan acewar Alhaji Umar idan akwai hujja suje su kawo.

Haka suka sake komawa da yaron, ayanzun duk uguwar ta dauka, akan wannan tirka tirka da ake tsakanin gidajen guda biyu, yayin da duk jamar unguwar ke goyon bayan Ummi akan cewa karta karba, domin dai kowa yasan Aliyu be Kuma dawowa kasar ba, ko Ina cikin unguwar mgnr da ake kenan.

Gidan Innawo kuwa gaba dayan su tutsiye Aysha sukayi akan ta bude baki tai mgn amman abu ya gagara, zagi babu irin Wanda basu mata ba yayin da wasu suke cewa amata dukan ne, wannan abu ya dauke su tsayon lokaci har misalin karfe biyar na yamma so kawai suke Aysha ta fada masu domin su samu hujjar komawa gidan Innawo.

******

Karfe biyar da kwata ya shiga cikin unguwar, acikin abu biyu yasan tabbas zai tarar da daya, kodai Aysha tagaji da jiran sa tayi aure, ko Kuma tana dauke da tsohon cikin sa, wadda jikin sa yafi bashi na karshen, a zuciyarsa yasan mayuwacin abu ne ace Aysha bata da cikin sa, saidai idan wani ikon Allah, dan haka yanzun bashi da burin daya wuce yaji labarin Aysha tunkafin ya Isa gida.

Adaidai kofar gidan su Innawo motar ta tsaya, yayin da yake ganin komai ya cansa masa, akwatin sa ya sauke sannan ya Kira wani matashi yace dan Allah ka shigar min da kayana nan gidan.

Dauka yaron yayi ya shiga, yayin da Aliyu yai saurin karasawa gurin Idi me shago.

Wa nake gani haka kamar Aliyu?

Cikin murmushi Aliyu yace, " ba kama bace nine"

Aliyu Kaine?, Kallon Aliyu yake sosai yayin da yaga ya zama katon sajo babban mutum.

Nine Idi.

Nayi farin ciki da zuwan ka ta wani bangaren Kuma banyi ba.

Menene yake faruwa?

Hannun idi yasa yaja Aliyu bayan sagon sa yana fadin, " bayan tafiyan ka abubuwa da dama sun faru, kayi hakuri zan gaya maka wata mgn wadda bata da dadi, Aysha tayi ciki....

Tun kafin ya rufe baki Aliyu yace, " nasani"

Au ka sani???🤔

Eh na sani, idi yanzun Aysha tana Ina?, Cikin na nan ko babu shi?

Ai ciki ma an haifeshi jiya da daddare.....

Bebari ya karasa ba yace ita Aysha tana Ina?

Tana nan cikin gidan su ....

Nan ma be bari ya rufe bakiba ya doshi gidan, acikin zauren gidan ya tsaya hannun sa cikin aljihun sa, cikin karkausar murya ya rangada sallama Har sau uku sannan aka amsa.

Innawo ce ta tahowa tare da fadin, " waye nan??

Acikin daga muryar irin na sojoji yace, " nine.....

https://youtu.be/2eTqqbS_xq0

*SUBSCRIBE*
*COMMENT*
*LIKE AND SHARE*

*🕳 BA'KAR FURA🕳*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍

Episode 46- 47

Kaine wa?, Umma ta fada tana kokarin lekowa.

Shiko Aliyu hannun sa ya ciro cikin aljihun sa yana gyara gilashin idon sa, adaidai wannan lokacin Umma ta iso tai tsaye tana kare masa kallo zuwa can tace, Yaya dai"

Idon ta na nuna mata kamar Aliyu ne, amman ganin ya Kara budewa da cika sosai fuskarsa cike da 'kasumba ta tsaya tamtama, yayin da wata zuciyar ke ganin kamar gizo yake mata kawai dan dai suna mgnr sa ne Kuma suna tsananin son ganin nasa.

Cikin 'Kara kankance idonta tace kamar Aliyu ne nake gani?🤔

Miskilancin sa na baya ne ya dawo daidai wannan lokacin kasa yayi da murya yace, " shine"

Shine???🤔, Ko gizo ne??

Wani guri ya tsayar da idonsa dake cikin gilashi, ba kizo bane nine Aliyu.

Kai Umma ta gyad'a dake nuna eh lallai, sannan tace, " da wacce kozo?"

Dan Alheri nazon, Ina son naga Aysha ne😎

Jarr ubancen, Umma ta fada sannan tace Bismillah.

Cikin sauri ta koma cikin gidan tana fadin duk ku fito daga dakin nan in kalli ikon Allah.

Aliyu kuwa Umma na juyawa yabi bayanta, yana tsaye yaga su Aunty Murja na fitowa daga dakin kowanne fuska cike da masifa, ciki harda maza kawun nan Aysha.

Umma ce ta kalli Aliyu dake tsaye agefe cikin kakin sa na Sojoji sannan ta juya ta kalli yaranta tace, " ga Aliyu nan wai yazo ne zaiga Aysha😒😒😒

Mazanne suka nemiyin mgn cikin sauri Umma ta dakatar dasu cike da kwarin guiwa tace ku bashi hanya ya shiga ya kanta.

Ya shiga Kuma??

Eh ya shiga Mana, tunda ita ba iya fitowa zatayi ba, kuzo ku shiga nan ku basu waje.

Matan ne suka fara kaucewa yayin da Mama take a bayansu dan haka yana fara takowa yai kasa da kanshi yace, Ina wuni?

Wucewanta tayi bata amsa ba, shima be damu ba yasa kansa cikin dakin yayin da duk yaran Umma sukayi tsaye a tsakar gidan.

Itako Aysha tunda aka fara kiran Aliyu, Aliyu, gabanta ke faduwa bata yadda shid'in bane saida taga shigowansa sukayi 4 dashi.

Wanni irin kallo ta masa me cike da tuhuma tsayon lokaci, yayin da hawaye ke ziraro mata, shima kallo yabita dashi fuska adan sake sannan ya fara takawa, bakin gadon da Aysha take Kai ya zauna, yayin da Aisha tai saurin mikewa tana kokarin barin dakin.

Zo, Ayaha karki fita.

Ficewa tayi sai dai tana d'aga labulen idanuwa suka mata cah  cike da tuhuma dan haka tai saurin komawa tai tsaye abakin kofar.

Kallonta Aliyu yayi cikin sanyin jiki sosai yace, " kiyi hakuri, nasani ni me laifine, zo ki zauna.

Runtse ido tayi, bazan zauna ba kazo ka fitar mana agida.

Murmushi yayi sannan ya Kara komawa bakin gadon ya zauna tare da dauko yaron ya daura akan cinyarsa  tare da zuba masa ido.

Wani irin farin ciki yaji ganin inda yaron yayi tsananin kama dashi, eh lallai da anga wannan yaron an ganni, dagowa yayi ya kalli Aysha tare da fadin zo ki zauna muyi mgn.

Ka tashi ka fita kafin Umma tazo, duk abun da ta maka kaika saya, dan rashin mutunci ka shigo har cikin gida😏😭

Eh naji, bani da mutunci, amman ni bana tsoron Umma, bama Umma ba, kowa ma, kisani ba yadda za'ayi mutum ya tashi ya tafi filin yaki shi daya  batare daya shirya ba, kuma ni wannan abun ba zuwa nayi na sawoshi a kasuwa ba, cikin sa na tsinta kaina, duk da cewa nayi kokarin kauce ma hakan, nasan daman zanzo in tarar da haka daga gareki, tunda na wuce lokacin da nace zanzo, amman nina ki zuwa ne saboda nasan mawucin abu ne ace baki da ciki, Kuma  har jiya da na taso jikina yana tabbatar min da zan tarar da makamancin wannan.

Cikin zubar da hawaye Aysha tace shine kabarni da wahala ni daya bakazo mukaci wuyar tare ba ko?, koda yake ba laifinka bane yazon ma kana da damar da zakace dan banaka bane, tunda kowa yasan baka garin nan nice na kawo kaina dan haka koma mene nic.......

Meyasa kike min irin wannan tunanin Aysha, niba azzalumi bane, kuma niba makaryace bane, akan me zance ba nawa bane, alhalin jinina ya yafi karfi ajikin yaron ma, yaro nawa ne, yaron ya sake kallo, sannan ya dagoshi ya sumbace shi, tare da kai Kunnen sa saitin bakin sa, ya jima, sannan ya sauke shi kan ciyarsa yana fadin, " sunan sa Khalipa, Baba nane shi, Aysha Moh'd Bello ne, sunan Baffana kenan, Kuma Ina tabbatar miki Ina tsananin son shi.

Waigowa tayi cike da masifa sai dai ganin hawaye akan fuskansa yasa tai saurin kawar da kanta, shiko Aliyu juyawa yayi ya aje yaron sannan ya mike yana fadin, " zoki zauna kinji, banshiga gida ba hankali na ne yaki nutsuwa shiyasa na fara zuwa nan.

Kin joyowa tayi har yanzun can gefe take kallo.

Kasa ya karayi da Murya yana fadin, kixo ko zauna ki bashi abincin sa, kinga wawure wawure yake yi akwai alamar yunwa a tattare dashi.

Wani kofe dake kasa ta tsuguna ta dauka cikin sauri ta maka masa akirji ragowan ruwan dake ciki ya jika rigarsa.

Cikin zare ido yace, " washess Allah na, akwai zafi, akwai zafi sosai, ya fada yana sosa wajen,, dan Allah badan halina ba kibashi yasha.

Batare data kallesa ba tace Allah ya 'kauta nabawa wannan dan bura'uban yaron nono na sha.

Subuhanallahi, kallonta yayi cikin ido sannan yace ni bansan lokacin da kika zama masifaffiya har haka ba, shikenan ynzun ki samo bulala kita dukana harsai kin huce tunda naga kamar kina sha'awan dukana.

Wuceshi tayi ta dawo bakin gado ta zauna, cike da bacin rai take kokarin hana idonta kallon shi.

Shima kallon ya gama kare mata sannan yace barin je gida kinji.

Tabbatarwa da yayi bazata amsa ba ya sashi ya kad'a kansa ya fita adakin, yayin da ya tardasu cirko cirko a tsakar gidan.

Ganin Aliyu zai fito duk suka taho kusa, yayin da yake kokarin ratsasu kawun Aysha yace Ina zaka bayan baka fito da d'anka ba?

Ba abin da ya kawuni kenan ba, Aliya fada fuskarsa ahade"

Innawo ce tasha gaban Aliyu cike da bala'i tace, " me kake nufi Aliyu?, kowa ya kalli Dan

nan ya ganka, dan haka d'a naka ne, maza ka koma ka dauko d'anka, ke Murjanatu dauko min yaron nan.

Cikin daga murya Aliyu yace Bafa zan amsa ba, dan ba abin da ya kawoni kenan ba.

Sosai gaban Aysha ya buga, bugawa me tsanani, ganin yanzun ya amsa nasane harga masa hud'uba, me hakan ke nufi to, mikewa tayi azubure ta fito ta tsaya ta rike labulen tana kallon cikin idon Aliyu da zuwa yanzun ya canza launi ya zama jawur.

Umma ce tace, " Wlh Aliyu baka Isa ba, idan Kai dan duniya ne nikuma yar guguwa ce, d'a naka ne, idan ba naka bane meya kawo ka?, Me kazoyi gurin Ayaha?

Maman Sadam ce tace, a'a Umma tsaya, Kai d'an naka ne ko banaka bane??

Kawunnan Aysha ne suka fara cewa akan me Zaki masa wannan tambayan?

Shikuwa Aliyu kallon fuskar Aysha yayi sannan ya kawar da kansa tare da fadin, " nawa ne, d'ana ne"

Alhamdulillah, Umma ta fada, yayin da tai saurin komawa dakin ta dauko yaron ta mikawa Aliyu tana fadin' " amshi kayan ka"

Bazan amsa, bana so, nabar miki"

Ka bar min, kace dai ka shirya babban masifa garin nan, domin kuwa idan Kai baka amsa ba Uwarka zata amsa dole, mara mutunci kawai, dan iska, fitsararre, na dade da sanin baka da Kunya, baka da mutunci, ka kalli tsabar idona kace wai ka barmin, ka barma uwar ka dai.

Kawun Aysha ne ya daki kirjin Aliyu tare da fadin, " dan ubanka ka amsa danka kabar mana gida.

Cikin zaro idon tare da hargowa Aliyu ya nuna shi da yatsa tare da cewa, " karka kara tabani ko zagina Ida ka Kara zan rama.

Yadda yayi mgnr cikin hargowa yasa duk gidan saida suka zabura har Aysha, da kallo kawai suka bishi harya fice a gidan.

Umma kuwa saida Aliyu ya dade ta fita sannan a sauke ajiyan zuciya tana jinjina kanta take fadin, " jar Uban can"

Kawun Aysha ne yace wai yaron nan dame yake takama ne??, kiduba kiga yadda ya shigo Mana gida, naso in hanashi ganin Aysha ai Umma ke kikace abarshi.

Aini duk tunani na d'ansa yazo dauka.

Mama Sadam ce tace kinji yace d'ansa ne amman beso, wai yabarwa Umma wato tunda kece nan kika hana masu aure yabar miki, ku dan iska.

Aunty Murja ce tace ga yar iska cen adaki, aini wlh nadawo daga rakiyar Ayaha, ba irin horon da ba'a mata ba ta fada nawaye tace ita sam bata san meshi ba.

Maman Sadam ce ta amshi xance aini Aysha taban tsoro, muguwar yariya ce me taurin ran tsiya, ko aina suka hadu oho, ita uwarsa tace shekaransa biyar be kasar

Rabu da munafukai duk su biyun munafukai ne nikuma sainaga uban daya tsayawa Aliyu.

*******

Da Sallama ya shiga falon yayin da akwatin sa yake tsakiyar falon, cikin murmushi ya ware hannun sa tare da fadin Oyoyo Ummi na, jikinta yai saurin fadawa tana zaune kusa da Innawo.

Ya dade rungume da ita duk da ya lura bata cikin walwala, fuskan ta daure tamau be hanasa dagawa ya sunbaceta ba,  cikin sauri tasa hannun ta ta share inda ya sunbata tare da fadin, " meya kawo ka?, Aliyu me kazo yi  awannan lokacin?"

Mika hannun yayi ya riko na Innawo yana fadin matass anya kuwa kinyi farin ciki da ganina.

Banyi ba, duk ka tsofa kayi gemo biya biya sannan zaka waiwaye mu?, Wai ma Ina kaje ne ka iso ka kasa shigowa gida??

Wani sako na bada, duk kuna lafiya.

Lafiya Lau Innawa ta fada sannan ya juya ya kalli Umminsa da har yanxun yana kan kafadan ta yace, " Ummi ke fa"

Cikin daure fuska tace na tambaye ka baka bani amsa ba, Kuma kana tambaya ta, nace me kazo yi kasar nan adaidai wannan lokacin.

Ni, Ummi nazo na ganku ne.

Karya kakeyi Aliyu, Ina kaje yanzun kafin ka shigo nan??

Jimmm Aliyu yayi tare da kauda kansa, zuwa can ya juyo yace"

Can gidan naje.

Innawo ce ta kalleshi ta kauda kanta tare da sa tagumi.

Itako Ummi tsare shi da idon tayi tana fadin, "  gidan su Ayaha??

Kasa amsawa yayi yayin da Ummi ta sake jefa masa wata tambayar, d'an naka ne ko kuwa banaka bane?

Lebensa na kasa ya cija da karfi sannan ya sunkuyar da kansa sosai tare da fadin, " Ummi ki tsaya nai miki bayani.

Tambayan ka nayi, Aliyu kabani amsa, d'an naka ne ko banaka bane?

Shine zan miki bayani ai yanzun Ummi.

Wlh Aliyu zanci ubanka, bana wasa dakai, niba sa'arka bace, na tambaye ka ka bani amsa daya tal, idan ba hakaba wlh ranka zai baci.

Juyawa yayi ya kalli Innawo cikin tsananin tashin hankali yace, innawu dan Allah kice mata ta tsaya nayi mata baya ni.

Kin juyowa Innawo tayi kota kalleshi, cike da tashin hankali yace, Innawo kema fushi kikayi,  dan Allah ku tsaya ku fahimce ni"

Ba wadda zai tsaya ya saurareka anan magana daya nake son ji agurin ka, naka ne ko banaka bane d'an?

Jimmm yayi idon shi cike da hawaye, sosai yake kokarin maidasu ahankali yace, " nawa ne Ummi.

Tirrrrr, kayin asara Aliyu, ashe baka da mutunci, ashe dan iska ne Kai wawa mazinaci.

Innalillahi wa inna ilaihir raju'un Aliyu yake maimaitawa da karfi.

Dole ka kira Allah, munafuki kawai wadda bejin tsoron Allah, saikaje ka dauki dan ka kaima ubanka kusan yadda zakuyi ni babu abun da ya dame ni.

Rasa inda zaisa kansa yayi cikin sauri ya nufi  hanyar dakin sa yayin da yai saurin juyowa ya nufi kofar gida.

Innawo ce  Kai Ina zaka?

Tafiya kawai yake da alama baya sanin inda yake saka kafar sa, kofar gidan ya zauna tare

da hada kansa da guiwa.

Ya dade zaune agurin sannan yaji taku kafafuwa na kusanto su dan haka yai saurin dago kansa, Maman Sadam ce da aunty Murja rungume da jaririn sai Umma dake binsu abaya, cikin sauri Aliyu ya mike yayi saurin saka kafarsa daya akan dukin kofar gidan yayin da daya take kasa hannun sa duk biyun cikin aljihu.

Ja sukayi suka tsaya, Maman Sadam ce tace bamu hanya zamu wuce"

Kubar walar da kanku na zuwa nan gidan, na shirya zuwa duk koma inane, Inanan akan bakana bazan amsa yaron ba, nan gidan ma babu me amsa, dan haka kujuya kawai

Kai, wani ni shin in tambaye ka?, Dan naka ne wai ko ba naka ba?......

Katseta yayi da fadin, nawa ne, amman baxan amsa ba, duk inda za'aje aje bana so nabar maku, bazan amsa ba.

Wlh baka Isa ba, indai nice kamar ka amsa ka gama, idan Kai baka amsaba sabo da idon ka atsaye suke Uwarka zata amsa

Cikin tsawa yace, zaku tabbatar bazan amsa bane idan wata mata ta sake takowa kofar gidan nan, domon duk wata kafa data sake takowa nan saina balla ta

Zaro ido sukayi gaba daya, cikin sauri Umma ta juya tana fadin kuzo mutafi, saida sukayi nisa sannan Umma ta tsaya tace, " Idan kana takama ne kafi karfin hukuma ai baka fi karfin alkali ba, dani kake mgnr.

Innawo kuwa zuwa tayi bakin kofar ta cikin gidan take fadin wai Kai kana ma da hankali kuwa, ko hauka kayi ne?

Lafiyana lau Innawo, Ina sane.

Akofar gidan ya wuni
da yammacin ranar misalin 4:34pm ta kardan sammaci ta samu Aliyu, bude takardan yayi fuskarsa cike da murmushi......

*⬬ BA'KAR  FURA⬬*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

Episode 48- 49

Mikewa yayi da takardan a hannun sa ya shiga gidan, tunda ya bude ta be rufeba.

Afalon ya samu Ummi sai faman sheshekar kuka take yi, yayin da yaji muryan Innawo daga cikin dakin maccin ta tana fadin, " tunda bazaki bari ba saikije kita yi, idan wani ciwo ya sameki sai kizo kiyi jinya, ace mutum ya wuni yana kuka, komai yayi zafi maganin sa Allah, ni ko Aliyu bezo yanzun ba na tabbatar koma yaya ne d'an nan nasa ne.

Jikin Aliyu a matukar sanyaye ya zauna afalon nesa da Ummi, yayin da kowanni saukan hawayen ta yakejin takaicin sa cikin ransa, dan haka ya shiga fadin, " Ummi dan Allah kiyi hakuri"

Cike da tsananin zafi tace, "ranka zai baci ka sake ka sake min mgn, babu ruwana dakai, mara mutunci kawai, wadda besan mutunciba, Dan iska kawai wadda ya dauki zina ba abakin komai,  gara daka nunana min ka zama tantirin dan iska, kaje ka amsa kazantarka tun wuri ga kaima Ubanka, nan bama rike  d'an iska bare mu rike kazantar ka.

Ji Aliyu yayi kamar Ummi na watsa masa wuta, dan haka duk jikin shi ya Kara sanyi, cikin sanyi sosai yace, " Ummi kiyi hakuri dan Allah ki Kuma tsaya kiji Uzurina.

Dallah gafara cen, Kai dan baka da Kunya har kake tunanin ni zan saurara ta tsuniyar ka?, Mara kunya kawai, kama yariya ciki saboda tsabar rashin kunya jiya tana haihuwa har ka iya shigowa garin nan,  kowa na kallon ka bakajin kunya Kai?, to idan Kai baka da digon kunya mu muna dashi, nasan ka riga ka zubar Mana da mutunci kowa yasan wannan Ibrn acikin unguwan nan, harma da kewayeta, dan haka yau yau dinan kaje ka amsa danka kabar kasar nan, baxaka kwanar Mana agida ba kaji Kuma na gaya maka.

Mikewa Aliyu yayi cikin rasa abun yi, adaidai wannan lokacin Innawo ta fito tana fadin, " ni yanxun ba wannan ba, surutun nan bashi da amfani, ke ki bari yayyan ki suzo kwai anemi

mafita.

Innawo idan Ina kaunar ganin Aliyu toh Ina kaunar ganin mutuwata, wlh banson kallon shi idan Ina kallon shi raina namin zafi, zuciya ta nafarfasa, jibeshi kawai, katon banza mazinaci dan isaka fasiki matsiyaci kaw......

Cikin sauri Innawo ta katse Ummi da fadin, " ke!! , Ki dawo cikin nutsuwarki, naga kina da niyar yi masa baki, karki fara, wlh ranki zai baci.

Toh Innawo wadda ya aikata irin wannan abun kuma meya rage mishi?, ai ya riga da ya lalace.

Nace miki kiyi shiru ko, bakama yima yaron mugun baki ba kenan inaga ka mishi?, Kai Aliyu tashi ka shiga ciki.

Ajiyan zuciya Aliyu ya sauke me karfi sannan ya mike muryan shi can kasa yace, " Ummi kiyi hakuri dan Allah, nasan ni me laifine, bacewa nayi akan daidai nake ba, matsala kawai aka samu, kokarin shiga dakin yake ya sake cewa Innawo kema kiyi hakuri ba ason raina bane, tsintan kaina kawai nayi ahaka.

Sosai wannan kalamin nasa ya shiga jikin Innawo, tausayin Aliyu taji ya dan shige ta dan haka ta hada abinci ta nufi Kai masa, sai dai tana dire abincin yace Innawo bazan iyacin komai ba, hankali na ba akwance yake ba.

Murmushi Innawo tayi me kama da yake sannan tace, " duk jarumtar daka taho da ita Aliyu?, ai naga ka taho da jarumta, naji kanace ma Umma d'a naka ne, amman bazaka amsa ba, wai kabata, toh Kai kanka kasan ba abu me iya yuwa kake fada ba, kasan masifa da balaki irin na Umma, da ace ba Umma bace sai mu roki tashayar da yaron bayan tagama shayar dashi tabamu, toh Umma kota amince da haka na tabbatar hankali bazai taba kwanciya ba idan ba dan nan aka amsa ba......

Innawo nifa baxan amsa yaron ba.

Bangane ba Aliyu?, kafa amsa d'an naka ne?

Amman wlh Innawo bazan amsa ba, ko ita ta kirkiro masifa.

Ashe kuwa Umma zatai karan ka.

Ai tamayi, ga takardan yanzun aka kawo min.

Innalillahi wa inna ilaihir raju'un, shikenan zancen ya wade duniya, naso arufe abun.

Ninafi son haka Innawo.

Aliyu bakajin kunya?, Wannan fa babban abun kunya ne, ace acikin zuri'armu muna da shege.

Kashhh,😬 Aliyu ya fada, Innawo shege fa kuke cewa, shige shine wada ba'asan ubanshi ba ai,

Ai ba aure kukayi ba?, Ko auren sirri kukayi?, Idan kuwa har ba aure Aliyu ko kaki ko kaso sunan sa kenan.

Yamutsa fuska Aliyu yayi tare da kawar da kansa yake fadin, " amman Inawo wannan yaron ba sunan sa kenan ba, kuma idan har ana gaya masa haka za'a dinga samun matsala.

Mikewa Innawo tayi tana fadin, Allah ya rabamu da ita, Kuma Ina baka sharawa aje duk wata rashin kunyarka harsai zuciyar Ummin ka yayi sanyi inba haka ba ta iya gaya maka kalma mara dadi, dan tana cikin fushi sosai.

Tana gaba fadin haka ta fice yayin da yabi bayanta da kallo.

*******

Koda rana da Alhaji Umar da Sani sukazo gaba sukasa Aliyu, fada babu irin wadda basu masa ba, sosai ya roki su tsaya su saurari uzurin shi, amman Alhaji Umar yaki bashi wannan damar, acewar sa, bashi da wani uxuri da zaisa su saurareshi, idan har zina ne ba aure ba, basu bukatar uzurin shi, dan haka ya sunkuyar takai kawai, cikin yanayin dake nuna yanajin kunya, daga karshe Ahaji Umar yace, tunda sunkai mgnr kutu babu wani hukunci da zasu iya dauka abari ashiga kotun.

Cike da fada Ummi tace ai shikadai zaije babu wadda zaije kotu acikin gidan nan.

Kara sunkuyar dakai Aliyu yayi yayin da yaji muryan Ahajin yana fadin, " kedai ki zauna agida, amman dole asamu wadda zai rakashi, hannun ka baya rufewa ka yanke ka yar, dan haka yazun mafita ake nema.

Mikewa Ummi tayi tabar dakin, yayin da duk suka shiga yima Aliyu nashiha.

Bayan sun gama da Aliyu gurin Ummi suka nufa, nan ma dai nasiha sukaita mata akan hakuri, aduk halin daka tsinta kanka aciki.

Washegari misali 7: 30 Aliyu ne ya fito cikin kananan kaya, a kitchen ya samu Innawo

bayan sun gaisa yace, "  ina Ummi na?"

Kallon shi tayi tace, " tana kwance sai bayan sallan Asuba ta samu bacci.

Jimmm yayi, sannan yace, " dan Allah Innawo ki bata hakuri, kinji, wlh tsautayi ne kawai.

Hmmmm, toh naji ai Allah ya kawo Mana mafita.

Ameen, ya fada ahankali, sannan ya juya ya fita.

*******

Wannan Zaki mikawa Aysha Idan da hali ki dauko yaron.

Amsan jibga jifga ledojin guda biyu matar malam Idi tayi a hannun Mijinta sannan ta kalli Aliyu dake gefe ta kada Kai tai waje.

Gurin zama Malam idi yabawa Aliyu sannan ya zauna kusa dashi, kusan minti 10 sannan matar malam Idi ta dawo rugume da jaririn ahannun ta.

Malam idi ne ya mika hannun ya amsa yaron, sannan ya mikawa Aliyu, nan danan murmushi ya bayyana afuskan Aliyu yayin da ya kurawa yaron ido.

Daker ya iya dagowa ya kalli Matar malam idin yace, " aunty Aysha tana lafiya dai ko??

Eh lafiya lau take.

Maida Hankalinsa yayi kan yaron dake kokarin wangale baki sannan ya sake dagowa yace, " bata cikin wata matsala ko?"

Eh toh, gaskiya dai na sameta tana kuka dai, ga yaron ma ba'a masa wanka ba, ita dai naga alamar tayi wanka.

Jimmm Aliyu yayi cikin sanyin jiki sosai zuwa can yace to ta karya kuwa?

Gaskiya bana tunanin ta karya, da alamar dai tana cikin damuwa sosai, dan kayan da nakai yanzun ma cewa tayi indawo maka dasu daker tabar su.

Ajiyan zuciya Aliyu ya sauke, sannnan yace, aunty dan Allah kimin kokari kisata taci abinci, sannan kice mata ta kwantar da hankalin ta, Ina nan bazan tafi ba harsai mun samu mafita, da yardan Allah, ta kwantar da hankalin ta Ina tare da ita.

Daga idi har matarsa cike da tausayawa suke kallon Aliyu, hakika shima cikin damuwa

yake, ruwa matar malam Idi tasa taiwa yaron wanka sannan ta nadeshi da nufin idan ta mayar dashi zata canza masa kaya cikin Wanda takai yanzun.

Aliyu bebar gidan ba harsaida ya tabbatar Aysha taci abinci sannan yabawa matar idi kudi yace ta dinga lekata akai akai abun da babu acikin kayan asaya idan ana bukatar wani abu Kuma amasa mgn.

Ranar da Aysha tayi kwana 4 haihuwa ranar ce ta kasance ranar da za'a shiga kotu, misalin 8:00am Aliyu ya gama shiryawa tsaf cikin manyan kaya shadda ce wadda ta amsa sunanta, sosai ta karbesa matuka yayi kyau sannan ya daura hula, baka taba kallon sa kace baida iyali agida sabo da kwarjinin sa, Aliyu kyakyawa ne na gaske hasken fata ne kadai beda ita, dogone me dogon hanci uwa uba iya daukan wanka, Dan koga yasa kaya saika dauka ya shirya yin gayune Koda kuwa cikin damuwa yayi ta.

Afalo yacidda Innawo tana tana fadin, kawun ka yace daga can zai wuce nikuma Ina nan zuwa.

Gyada Kai yayi sannan ya fice agidan.

Cike harabar kotun yake da mutane, Babban kotune da ake shari'a kala kala, ganin ba'a fara shiga kotun ba ya nemi guri ya zauna, bega wani daga cikin yan gidansu Aysha ba, hakama kawun nansa basu zoba, zuwa can ya hango Umma da gayyan yaranta sun sakko daga mota saidai babu Aysha acikin su, balakin kosawa da yayi yaga Aysha yasashi Jin hankalin sa ya fara tashi.

Zuwa can Hankalinsa ya koma gun Innawo ganinta tare da Ummin da abun yai matukar bashi mamaki, zuwa wannan lokaci bakin babban kotun cike yake da dan mutum, saidai har wannan lokacin bega Aysha ba.

Duk inda zai kallah ya kalla Amman babu ita, daga can ya hangi wata mota ta faka, wani mutumi yaka ya fito dattijo ya zagayo ya bude kofar motar, Aysha yaga ta sako kafa tana rungume da yaron a hannunta, saidai bata iya dago kanta harta fara takowa tana boye sukanta da hijjabinta, can gefen su Umma ta koma ta rakube yayin da Daddyn ta ta Isa gurin su Umma.

Tunda ta sako kafarta kasa Ummi take mata kallon tsana  tare dabita ita da dan nata da kallon sosai takejin tsanar Ayaha ita da abun da ta haifa har cikin kokon ranta.

Shikuwa Aliyu, tunda Aysha ta zauna kallonta yake yi, yadda ta takure sosai ita daya agefe yaji beson hakan dan haka ya mike ya fara takawo kai tsaye yake ratsa mutane har ya Isa gurinta fuskanta yana daga cikin hijjabi.

Tsaye yayi akanta ya kalleta ya kalli yaron yayin da duk idon mutane ya koma kansu.

Umma kuwa wani irin tafarfasa zuciyarta keyi, hakama maman Ayaha gaba daya jitake ta tsana Aliyu hukunci me nauyin gaske take son amasa wadda zai raina kansa, gaba daya yaran Umma hakalin sune ya tashi yayin da suke ganin yaje ne ya dada hure mata kunne ta basu kunya.

Sukuwa jamar dake gurin waddan suka San abun dake faruwa mamaki sukeyi sabo yadda suka kula kamar Aliyun na nuna kulawan sa akan dan dayaki karba dan ganin ya mika hannun sa ya gyara ma jaririn hular dake kansa.

Da yawa mutanen dake gurin kosawa sukayi ashiga kotun ciki harda iyalan gidajen guda biyu domin duk kusawa sukayi ya tashi daga gaban Aysha.

Shikuwa Aliyu tsaye yake akanta yake fadin, " malama ki bude fuskarki, ke kike karawa kanki damuwa da kanki, kece ma zaki jawo mutane su kalleki, da an ganki anga mara gaskiya, dan Allah ki nutsu sosai karkije kimin shirme, inba kinsan bazaki iya mgn ba kiyi shiru kawai.

Batare data bude idontaba tace, " ai dole kace nayi shiru tunda kanson ka barni da yaron.

Kawar da kansa yayi sannan ya juyo ya kalleta tana kudundune da fuska yace, " eh zan barki da yaron ne amman ai nine ubanshi.

Shikenan naji bakomai jeka.

Bazan tafiba saikin tashi kin goya yaron nan, kina rufe fuka saikin je kin yadda shi?

Wlh bazan goya shi ba, Kai ka amsa ka goya mana.

Kawar da kansa yayi tare da cizon lebensa yace, "  badan wani dalili guda daya ba Dana baki mamaki"

Kuka Aysha tafara harda shasheka adaidai lokacin da aka fara shiga cikin kotu, cikin sauri ya bi ta bayanta tare dasa hannun sa akanta yaja hijjabin baya fuskarta ta bayyana sannan ya wuce ya shiga cikin kotun......

*⬬ BA'KAR  FURA⬬*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

Episode 50- 51

Ahankali akai ta shigowa har aka cika kotun makil da jama'a.

Bayan kowa ya nutsu kotun yayi tsinta yayin da aka shiga kiran kararrakin.

Shari'a biyar akayi sannan aka karanto Karan su Aliyu.

Sosai gaban Innawo Dana Ummi ya buga Jin yadda aka fadi karan.

Hajiya Umma ke Karan Aliyu Moh'd Bello akan cewa yayiwa jikarta ciki ya Kuma ki amsan d'an.

Kotu ce ta bukaci ganin Aliyu Muh'd agaban ta.

Wani irin mikewa yayi cike da kwarin guiwa ya kamo hanya yana me cire gilashin idonsa ya maida cikin aljihu sannan ya Isa inda ya dace ya tsaya ya tsaya.

Bayan Aliyu ya tsaya agaban kotu sannan aka bukaci ganin Umma, sosai mutane suke mamakin Aliyu domin daka ganin shi babu alamar lalacewa ko rashin gaskiya a tattare dashi, daka ganshi kaga cikakken mutum me mutunci, dan haka dayawan mutane suka shiga mamaki, gashi ance yayima yariya ciki yakuma ki amsan d'an, gashi Kuma cike da kwarin guiwa.

Fitowa Umma, tayi ta tsaya, yayin da aka bukaci ta maimaita abun da take karansa akai.

Tama kallon Aliyu da nuna kwarewa asurutu Umma tace, "toh wannan yaro dai gashi Aliyu ya azabtar Dani arayuwuta, wato tun Ayaha na kankanuwarta ya fara lalatata, tare da hure mata kunne ta guje mu, nayi, nayi, ba yadda banyi ba akan ya rabommun da jika, bayan na dauki duk matakin dazan iya dauka yaki bari, gurin 'yan sanda ne, kofar sarki, har kotu munje daga karshe

uwarsa ta dauke shi nan ta maidashi Nigeria, shekara biyar kenan da tafiyarsa, duk na saki jiki bekasar Ashe, Ashe yana lallabowa yana amfani da ita, kawai sai ganin ta mukayi da ciki, dan haka nake rokon kotu data bima jikata Aysha hakkin ta na rayuwarta daya lalata mata.

Da yawan mutane kallon su suka mayar kan Aliyu har yanzun yana tsaye idonsa akan Umma sosai yake Jin haushin Umma cikin ransa.

Alkalin ne yace akwai Aysha acikin kotu??

Eh, ranka ya dade, juyawa Umma tayi tana nuna Aysha, yayin da Aysha ta mike, Aunty Murja ce ta amsa yaron, sannan ta fito cikin sunkuyar dakai har ta Isa gaban kotun bata iya dago fuskanta ba.

Alkalin ne ya kalli ta ya cire gilashin idon sa cikin tare gida sosai alamar babu wasa ya kalli Aliyu, gyaran murya yayi sannan yace,  malam Aliyu kaji abun da Hajiya Umma  take zargin ka dasu?, Hane ko kuwa kana da abun da zakace?

Ina dashi ranka ya dade, duk  abun da ta fada ba haka suke ba.

Uwarka ce take karya mara kunya, kana nufin ni makarya......

Tsawan da Alkalin ya buga mata ya sata Ummata tai saurin rufe bakinta batare data shirya, ido ta zubawa Alkalin Jin irin tsawan da ya buga sannan yaci gaba da cewa karki sake yin mgn batare da an bukaceta daga kareki ba, nan ba filin yaki bane.

Kar me karatu ya manta duk cikin harcen filatanci ne suke mgnr.

Maida hankalin  yayi kan Aliyu tare da daukan alkalamin rubutun sa sannan yace Ina sauraron Aliyu.

Awancen lokacin da Aysha take shigowa gidanmu karamar yariya ce da mata wuce shekara 13 zuwa 14 ba, Kuma karatu ke kawuta, dalilin tana samun inawa kanwata karatu take zuwa Ina masu tare, Kuma babu wata alaka da muke da ita nida Aysha bayan ta karatun, banta nementa da wani abun na iskanci ba iyaka dai inmata karatu ta wuce gida, gata Kuma a tambayeta, na taba nemanta da iskanci?

Kowa hankalin sa ya ya mayar kan Aysha dake hawaye yayin da taji an sake jeho mata irin tambayan da Aliyu yayi, kanta ta girgiza tare da fadin a'a.

Rubutu Alkalin yayi sannan ya maida kallon shi ga Aliyu yace, " amaganganun da Hajiya Umma tayi tafada cewa, tata nuna bata son kula jikarta da kake, wadda har tafada cewa anje police station, anje Kofar sarki, harta Kara da cewa anjema kotu, meyasa baka rabu da yariyar ba tunda ka fahimci danginta basa so Kuma Kai kafi Aysha hankali?

Ranka ya dade nashaku da ita sosai, Kuma haka nan Allah yasamin tausayinta acikin Raina, a wacen lokacin idan bangantaba banajin dadi, duk da cewa babu wata alaka da muke da ita bayaga karatu kawai.

Jinjina Kai Alkalin yayi sannan yace muje ga zargin Hajiya Umma na gama, munji Umma tace bayan faruwar duk waddan abubuwan mahaifiyar ka ta turaka Nigeria da zama, amman saika shigowa ciki Sirri, kana kwatsam sai tsintar Aysha sukayi da ciki.

Kawar dakai Aliyu yayi sannan yace, ranka ya dade ba haka bane, tunda mahaifiyarta ta turani Nigeria shekara biyar kenan zan iya rantsuwa da alqur'ani me girma cewa banta dawowa kasar nan ba sai wannan karon.

Sosai cikin Aysha ya luri ruwa, dama cikin hawaye take duk jikinta taji babu karfi, ji take kamar ta zube akasa domin kafa fuwanta rawa suke.

Cike da mamaki Alkalin ya maida idonsa kan Aysha yana kallon inda take zubar da hawaye yace, " Aysha Ina kika samu ciki?, Aliyu yace tun bayan tafiyan shi shekara biyar kenan be dawo ba, ki saki jikin ki kiyi mgn, anan muna kokarin kwato miki hakkin ki ne"

Hawaye kawai Ayaha take zubarwa dataga ma idon mutane yayi cah akanta saita fara shashshrkar kuka.

Sosai hankalin Aliyu ya tashi ganin inda take kuka, dan haka ya daga hannun sa alamar yana da mgn.

Kallonsa Alkalin yayi tare da bashi dama.

Ranka ya dade bayan nakwashe tsayon waddan shekarun na fahimci inason Aysha, kullum bani da tunani sai nata, har nafara kokarin inason indawo in nemi auren ta, saidai Ina tunanin gidan su da gidan mu, akarshe na yanke shawaran dawowa, saidai yanayin aiki na bansamu daman ba, kawai wata rana na dawo gidan mu na samu Aysha akofar gidan....

Wanni gidan??, Alkalin ya tambaya yayin da mutane suka Kara baza ido.

Gidan mahaifina a Kano Nigeria.

Cikin tsananin mamaki kowa ya Kara baza kunnen sa yayin da Umma tabi Aysha da kallon cikin ranta take fadin kaji tsinan ne matsiyaci.

Itako Aysha kuka kawai take.

Taya Ayaha tasan gidan ku a Nigeria bayan kun rabo da Aysha tana da shekara 14 kamar

yadda kaima da bakinka ka fada?

Ranka ya dade akwai adireshin Dana bata na gidan mahaifina, Alokacin da zanyi tafiyar nazo nai mata sallama, ganin tana kuka nai mata alkarin idan aurenta ya tashi ta rubuta ta aiko min zanzo, dan haka na bata adireshin da zata aiko sakon, wadda dashi tayi amfani tazo gidan mu.

Mamaki jama'a suka shiga yiyin da alkalin ajuya ya kalli Aysha yace, Aysha kinji abun da Aliyu yace, " da gaske ne kinje Nigeria?

Kara kudundunewa Aysha tayi, sheshekar kukanta kawai take, yayin da Umma ta daga hannunta.

Dama aka bata, Dan haka ta fito tace, " ranka ya dade, karya yake, ni jikata babu inda take zuwa, daga makaranta tana gida bata tabayin kwana daya ma bata gida ba, dan haka babu inda za'ayi Aysha ta tafi har Nigeria batare da sanin mu ba, Kuma Aliyu ya riga ya amsa mana ba sau daya ba cewa dan nasa ne, yanzun Kuma yanata mgn Kashi Kashi, yace zai rantse be taba zuwa ba, yanzun Kuma yace Aysha ce ta bishi.

Kallon Ayaha dake kuka Alkalin yayi sannan ya kalli Aliyu yace, "Malam Aliyu Ayaha acikin rana daya taje Nigeria ta dawo?

A'a tayi kwanakin da suka Kai wata uku da kwana sha biyu, kuma ta gaya min cewa gidan mahaifinta aka turata hutu.

Sosai jama'ar gurin suka zaro ido, ciki harda Umma da tai saurin kallon Daddy Aysha, yayin da Aliyu yacigaba da cewa, " nayi kokarin nayi mata fada wancen lokacin sannan na kaita cikin gidan mu wajen kannaina ta zauna, tafiya tsakanin Cameroon da Nigeria ba karamin tafiya bace dan haka nafara neman ranar da zan iya kawota gida da kaina nakuma nemi aurenta, sabo da Ina sonta, Kuma nasan itama soyayya ce ta kawota da rauni irin na mace, amman yanayin aikina be bani dama ba, ganin lokaci nata tafiya gashi wata tafiya harna tsayon wata Uku ta taso min na yanke shawaran sakata amota ta dawo gida, bayan na fito da ita daga gidan mahaifina ne Kuma awannan ranar garin sallama tsautayi yasani na kusanceta, hawayen gefen ido Aliyu ya cire sannan yai saurin ciro gilashin sa ya maida.

Zuwa wannan lokacin dayawa agurin sunyi kuka, shiru kotun yayi tsayon lokaci yayin da alkalin ya sunkuyar da kansa tsayon lokaci sannan ya fara rubutu akan takardan dake gaban sa, zuwa can ya maida kallon sa kan Aysha yace, " Aysha abun da Aliyu ya fada haka ne ko kina da jah?

Cikin sauri ta girgiza kanta.

Abun da Aliyu ya fada gaskiya ne??

Eh ta fada ahankali.

Alkalin ne yace, " Ina Hajiya Umma"

Mikewa Umma tayi ta fito sarari.

Kin gamsu da da bayanin Aliyu?

Nasan Aysha taje gidan mahaifinta tayi wanan kwanakin kamar yadda yace inaso naji daka bakin mahaifin ta Aysha taje gidansa ko bata je ba?

Bayan mahaifin Aysha ya fitone ya tabbatarwa kotu da cewa, tun wani zuwa da Aysha tayi ta kwana daya bata sake zuwa gidansa ta kwana ba.

Sosai Innawo da ma duk wadda yake cikin kotun yai mamaki.

Cike da tsabar takaici da kunya Umma tace toh shikenan, yanzun ya masa yaron yaje ya rainesa ahannun shi.

Rubuce rubuce Alkalin yayi sannan yace, " Aliyu yanzun ka amsa cewa dan da Aysha ta haifa naka ne?

Ranka ya dade naw ne"

Toh Hajiya Umma ta bukaci daka amsa d'an ka,

Ranka ya dade ni bazan amsa shi ba.

Meye dalilin cewa baza amsa ba bayan ka tabbatarwa kotu dan naka ne?

Nawa ne, amman banaso bazan amsa ba, na bar masu.

A'a toh tsaya,, acikin biyu dole zaka zabi daya, mata ko d'an??

Kai tsaye Aliyu yace mata

Ciki da mamaki Alkalin yayi akbara, sannan yace wadda ya dauki uwa ai ya dau  d'anta.

Rubuce rubuce yayi sannan ya dago yace, yaci ace iyayen Aysha dana Aliyu tun ashekarun baya sun ma abun kallo mekyau su masu aure, da ace tunda akaga sunki rabuwa an masu aure da an haifi dan sunnah, amma dake iyaye sun turje gashi abin da ba'aso ya faru, duk da cewa kuna ganin kun raba tsananin su rabuwa me nisa, tsakanin Cameroon da Nigeria,

amman dake rabon ya rantse saida Aysha tayi takkakiya tabishi Nigeria aka dawo gida da tsaraba, wannan ya isheku ishara, ku duba tsayon shekarun amman sabo da soyayya nacinta arai bata manta ba, da wannan nake Kira ga iyayen Aysha dana Aliyu da aje a gaggauta daura masu aure.

Cikin sauri Umma tace ranka ya dade, Ina rokon wannan kotu me adalci datamin adalci kamar yadda ta saba, Aliyu ya karbi danshi kawai ya tafi, domin bana fatan hada zuri'armu da tasu.

Kokarin maga Ummi keyi yayin da Innawo ta ke girgiza mata Kai dan haka ta fasa mgn saidai fuskanta na cike da fushi.

Gyaran murya Alkalin yayi sannan yace, Hajiya Umma wannan shine adalcin, be kamata ace zuwa yanzun kuna jayya ba, Kuma Aliyu bashi da da aibun da za'a hana shi aure auren ta, Kinga na farko yana da sana'a, sannan duk mutumin da zaiyi abu laifi ya amsa cewa eh yayi Kai tsaye da karshe ya nemi abashi auren ta, sannan ita kanta Aysha auren shine mutuncinta, Kuma Aliyu yana son Aysha haka itama Aysha alamu sun nuna tanason Aliyu har yanzun dan haka ku ajeye wani son rai naku agefe, am Ina fatan mahaifin Aysha yana cikin wannan kotun?

Amsawa Daddy yayi sannan ya fito gaba,. Yayin da alkalin ya sake cewa mahaifin Aliyu ba?

Innawo ce tace mahaifin sa ba dan nan bane.

Akwai wadda zai wakilce sa?

Alhaji Umar Innawo ta nuna baysn ya fito Alkalin yace, kotu zata daura auren nan take bisaga wasu dalilai.

Aliyu zaka bada Sadakin Aysha"

Cikin sauri yasa hannun sa duk ya tattaba aljihun sa tare da fadin, " ranka ya dade na mance ban fito da kudi ba"

Alkalin ne ya maida kallon sa ga kotun yana fadin, Aliyu bai fito da kudi ba, akwai wadda zai fanshe shi akotun nan??

Daga can baya wani ya daga hannu, mikewa yayi yayin da Aliyu yaga abukin sa wadda sukayi karatun tare anan Cameroon ne ke fadin ranka ya dade Jaka biyar ce a hannu na.

Juyawa Alhakalin yayi ya kalli Aysha yace,

toke Aysha jaka biyar dinan ta Isa amiki Sadaki dashi?

Batare data dago ba tace, eh

Abokin Aliyu aka umarta daya mikawa Aliyu kudin bayan ya bashi shikuma ya Isa ya mikawa Aysha, nan take alkali yadaura masu aure acikin kotun

Haka haka aka fito kotun yayin da jama'a keta mikawa Aliyu hannu, Umma kuwa kamar iska tabar kotun ita da iyalanta, tuni suka mikawa Aysha yaron.

Mahaifin Aysha ne ya dauketa ita da danta domin mayar dasu gida, shiko Aliyu motar Ahaji Umar suka hau gaba daya har Ummi, sai dai tun da Aliyu ya shiga motar farin cikin sa ya yaye domin Jin Ummi tana raira kuka.

*****

Koda su Aysha suka iya gida tun a gaban Daddy ta su Umma suke zagin Aysha tare dayin Allah wadai da halinta, sosai suka Kara nuna mata tsana da hantara, duk da cewa yau Aysha taji sanyi sosai, gannin yadda Aliyu yai mata hallaci Amman yanzun hankalin ta kara tashi yayi, dukan su rantsuwa suke yi cewa basu ba ita har abadah, mamako ko kallon inda Aysha take batayi barema taji wani kalma daga gareta.

Itako Ummi babu laifi tunda suka dawo kotu tana amsa gaisuwar Aliyu, amman bata son aure Kuma ta fada har agaban Aliyu cewa yaje yayi gantalelan aure.

Yayin da danginta ke nunar mata da cewa wannan shine mafita dan haka tai hakuri dashi.

Bayan Sati daya Aliyu ya Sami Innawo adakin ta zama yayi gefenta, tare da mata sannu, zuwa can yace, " Innawo inaganin gobe zamu wuce fah, yaya za'ayi ne??

Batare data kalleshi ba tace, " Kai dawa?"

Aysha mana.

Au daman haka ake yi?, kawai saikaje kace mata fito mu tafi? ko gobe zamu tafi, aika bari iyayenta su shirya ko? Saurin me kake yi?, yariyar da ma jego take yi.

Ni Innawo bawai zancen haka bane, akwai tafiyar da zanyi banason na wuce gobe anan kuma bana son natafi na barsu, sannan ni banason su bata koman su, da ita kadai zan tafi

Toh nidai nace maka ka bari tukuna, yanxun kaje kayi abun dake gaban ka, kasa ranar da zaka dawo ka tafi da ita, ni zan sanar masu ranar kaza zakazo ka dauki matar ka.

Kawar dakai yayi tare da hade fuska sosai yace, Innawo nifa gaskiya nafi son intafi dasu kawai.

Yanzun kai Aliyu saika iya daukan Aysha da yaron nan ka kaima Baffan ka?

Sosai yaji gaban shi ya fadin, batare da ya shirya ba yace, ni karyar da namasa kadai ke damuna, lokacin da Aysha tazo ce mishi nayi matar aboki na ce ita.

Jimmm Innawo tayi, sannan tace toh Ina baka shawara kabari ya samu Ibrn kafin kaje masa dasu, yanxun idan kaje ta turo min Ruqayya .

Tununani ya shiga akan mgnr Umma, badan ransa yaso ba ya hakura da haka, dan haka da daddare ya nufi gidan su Aysha domin yi mata sallama dan  asubanci zaiyi gobe........

*🕳 BA'KAR  FURA🕳*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍

Episode 52- 53

Kanan kaya yake sanye dasu yayin yayi sallama zauren gidan su Ayaha.

Daukan murya Maman Sadam tayi dan haka tayi Jim tare da kanne idonta guda daya cike da masifa.

Ji tayi an sake rafka wata dan haka tai saurin zama kan kujerar dake bakin kitchen din tana fadin. " Umma ana mgn"

Umma ce ta fito tana fadin Yaya aka yi?

Nuni maman Sadam tai mata da kofar gidan dan haka ta fara fadin, " waye nan?"

Nine"

Sarai ta dauki murya amman saitace Kai wa?

Aliyu ne,  ya fada kansa tsaye.

Himmm lallai, aifa sai Aliyun, Ina kasan inda take, ita jakar dakazo nema, ai sai kazo ka wuce.

Mmn Sadam ce tace, " yazo ya wuce fah kika ce?, ai saidai tafito su tafi, gidan Ubanshi ne da zai shigo?

Magana Umma tai mata kasa kasa adaidai lokacin da Aliyu ya sawo kai cikin gidan.

Kasa yayi da murya yace Ina wunin ku?

Wani irin kallon suka masa tare da kawar dakai batare da sun amsa ba.

Sallama ya sakeyi abakin kofar can kasa yaji ta amsa dan haka ya daga labulen tare dasa kansa ciki.

Kokarin sauke kafarta take yi da alama ta fara bacci, saidai gaba daya fuskarta ta kunbure , zama yayi a kujeran dake gefen gadon yayin da Aysha ta gyara zamanta batare data kalleshi ba tace Ina wuni?

Idon shi akanta yana zuba murmushi yace lafiya Lau ya jiki?

Alhamdulillah"

Lumshe ido yayi sannan yace, " ya khalifa?"

Cikin sauri ta kawar dakanta tare da turo baki ta nunashi da hannun tace gashi nan"

Murmushi sa ya fadada, ganin inda tayi sannan yace idon shi biyu ne?

Bacci yake, tafada har yanxun bakinta azunbure.

Ido ya zuba mata tsayon lokaci sannan yace, Aysha duk kin canza, sannan na kula kinajin haushin yaron nan.

Kuka ta fashe dashi sosai harsu Umma dake tsakar gida suna iya jin sheshekar kukanta, cikin matsanancin kukan tace, banfayi aure ba na haifeshi yaya Aliyu??😭😭

Lumshe ido yayi sannan ya bude su akanta tare da fadin, " aiba lefin yaron bane shi babu ruwansa fah Aysha, kibar yi masa haka kinji.

Juyawa tayi ta dan kalli yaron kadan sannan tace, " wlh banson ganin shi, inajin bakin ciki tare da Dana sani idan na kallesa.

Dana sani ai keya ce, gaba ya gamata mu fuskanta Aysha, sanda abun ya faru naji bakin ciki har nakan kasa bacci tsayon lokacin, ammman daga baya nagane babu yadda zanyi domin dai me aukuwa ta riga data auku, ni abun da nake so dake, ki saki jikin ki kibar takura kanki, wannan kaddaramu ce, Allah yasani Ina iyaka kokarina domin in gujewa zinah, nasani wannan jarabawa ce shiyasa ake son bayan ka tsare kankan ka kara da addu'a mugun gani da mugun ji Allah ya nisanta mu dasu, duk wadda yace shine toh bashi bane, wannan be wuce kan kowa ba, dan abun ba wayaun ka bane ba dibarar ka bace, dan da ace abun dibara ce da danasaki amota bazaki dawo ba.

Cikin sauri ta juyo ta kalleshi cikin idon sannan tace ai da na dawo ba abun da ya dawo dani kenan ba😏 kawai ji nayi kamar narabu dakai kenan har abada.

Murmushi yayi tare da fadin, yauwa Aysha ai nafison bakin ki ya bude, nasani, nasan ba abun da ya dawo dake kenan ba, nine kika dawo kika samu cikin wani yanayi, ai laifin nawa ne, yanzun dai kiyi hakuri abun da ya faru ya riga ya faru shikuma yaron ba laifin sa bane dan haka dan Allah ki kaunace shi.

Shikenan kowa kallon yar iska yake min😭😭😭

A'a Sam, muba Yan iska bane, ki saki jikin ki, kibar takura kanki, mikewa yayi yazo ya durkusa abakin gadon yana kallon Fuskan yaron tare da fadin zo ki gani kama yake dani Sak.

Aina gani.

Eh juyo ki kara gani.

Sunkuyar da kanta tayi tare da nuna bazata yi abun da ya bukata dim ba.

Mikewa yayi ya tura hannun sa cikin aljihun sa duk biyu, kallon ta yayi yana tunanin ta yadda zai gaya mata gobe zai wuce, gaba daya ya rasa da wacce kalma zai fara, agogon hannun sa ya kallah sha daya da kwata yagani dan haka ya maida kallon shi kanta.

Aysha ki fara shiri daga yau, da zaran nadawo kwana daya zanyi sai mu wuce......

Bekai ka rufe baki ba tace,  "yaushe zaka tafi??

Gobe da safe.

Cikin sauri ta juya gaba daya ta bashi gadon bayanta  tare da wasa da yatsunta.

Sarai yasan me take nufin domin tun bayau ba ya fahimci halinta, ahankali yace, Ayaha?

Kin juyowa tayi yayin da ya farajin sheshekar kukanta.

Kuka kike yi??

Tunda fa muka dawo kotun nan, gidan nan babu memin mgn Ya Aliyu, basa bani abinci yadda suke nuna bakin cikin su har gara kafin aje kotun, yanzun ko ruwan wanka basa bani bare ma suma yaron, Ina rasa inda zansa kaina Yaya Aliyu 😭😭😭

Sosai hankalin Aliyu ya tashi matuka, nan danan launin idon sa ya canza daga fari zuwa jah,  cikin wata irin murya me ciki da damuwa yace, ke Kuma har yanzun taurin kanki na nan ko?, baxaki iya basu hakuri ba?

Wlh ya Aliyu Ina basu, daga ranar da sukasan Ina da ciki haryau cikin basu hakuri nake amman abun Kara tsanta yake yi.

Jimmmmm yayi zuwa can yace kicigaba da basu hakuri kinji, naso inje daku Innawo tace im bari tukuna, bazan dade ba zan dawo, Innawo zata dinga leko ku, Husna ma haka.

Ahankali tace toh tare da matso hawaye.

Ganin yana shirin juyawa tace, " Yaya Aliyu?"

Juyowa yayi tare da takowa gabanta yace, Na'am Aysha?

Shekara nawa zakayi kafin ka dawo??

Aysha wanni irin shekara Kuma?

Waccen karon ma haka kace wata uku zakaxo to wannan karon Kuma sai Naga bakama sa lokaci ba.

Murmushi yayi kadan sannan yace, wancen karon Ina sane naki zuwa ai, saboda jikina nabani kina da ciki, insha Allahu bazan wuce sati Uku zuwa hudu ba, ki zama cikin shiri kawai, hannun sa ya mika ya dafa kafanta tare da dagota ta mike tsaye, kokarin hadata da jikinsa yake idon sa alumshe.

Cikin sauri Aysha tasa hannunta duk biyun ta  ture sa jikinta na matsanan cin rawa, yadda take danno kirjinsa da matsanancin karfi yasa ya bude idon sa alokacin da take ture hannun sa dake kafadarta da matsanancin karfi.

Sakinta yayi da tarin mamaki a tattare dashi, ba turesan ke bashi mamaki ba, jikin ta daya dauki rawa yai matukar bashi mamaki dan haka yace, " menene haka?"

Tasallake yaron tayi can bayan shi ta zauna tana fadin kaje toh.

Sakko muyi sallama.

Yaya Aliyu dare yayi"

Agogon sa ya kallah sha biyu saura dan haka yayi saurin sauka hannun sa a aljihu ya ciro kudi masu yawa ya aje mata tare da fadin nabarku lafiya.

Bata iya cewa komai ba harya fice.

Shikuwa Aliyu lokacin babu kowa alayin ya fito ya nufi gida.

Washegari da asuba yayi sallama dasu Ummi ya kama hanya.

*******

Ranar da Aliyu yayi kwana biyu da tafiya Aysha ta fito ta debi abinci a kitchen kamar yadda ta saba, tun bayan fitowanta kotu saidai ita ta fita ta diba, ruwan wankama saidai ta daura tayi sannan ta juye na yaron ta masa, tun bata iya ba har tazo ta koya.

Matar idi ce kawai kan taimaka mata wani lokacin tana tafiya dashi ne tai masa sannan ta dawo dashi.

Maman Sadam ce ta shigo ita da Umma ganin Aysha na kokarin shiga dakin Maman Sadam din tace, " Ke Aysha?, Ashe Aliyu ya koma?

Sororo tayi ahankali ta daga kanta.

Caf dijam, lallai baki da hakali Aysha, tunda kika bari ya tafi ya barki sai a lahira keda ki Kuma ganin shi, badai kince ke yar iska bace?, yanzun kika fara gani.

Umma ce tace ai saidai ta Kuma kwasan kafa ta bishi Amman bazai dawo ba.

To meya hana ya daukeki ya kaiki gun uwarsa idan ya cika son ki yake, wlh wuya yanzun

kika fara gani, Koda yake kinsan hanyar Nigeria sabo da iskanci nacikin kika kama hanya kasar da ko uwarki bata taba zuwa ba.

Mman Sadam ce tace, ai yanzun ko ta koma baxa ta ganshi ba dan wlh bazai tsaya inda zata kanshi ba, ni wlh badan uwarta ba da koranta akayi Dan wannan yariyar za'a iya hada baki da ita duk a kashe mu.

Umma ce tace, nima ai abun dake bani mamaki kenan, inda ace 'yatace da tuni nakoreta amman Naga kamar uwarta tausayin ta take.

Daga cikin dakin taji Muryan Mama na fadin, Umma ba haka bane, duk hukuncin da kuka yanke akan Aysha daidai ne agurina.

A'a nidai tunda kinbarta ta zauna acikin gidan nan, bayan ta zubar Mana da mutunci ta nunawa duniya muba komai bane, taita zama amman bana Kara bata abincina, dan ba wannan gwansamemen katon bane ya kawo min, karki sake tabamin kayana Aysha kinji na gaya miki, gida dai akwai kason uwarki aciki kita zama, amman wlh ko tukunyata kika taba sainaci uwarki.

Cikin zubar hawaye Aysha tace, " Dan Allah kuyi hakuri ku yafe min, wlh nayi nadama, idan nasake ku dauki kowanni irin mataki akaina....

Ai tunda kika amsa Sadakin Jikan Innawo kin fita daga cikin zuri'armu har abada Ayaha, dani da yarana kisa aranki haduwa ce irin ta titi.

Cike da hawaye Aysha ta shige dakinta wannan lokacin bata iya kwatanta bakin cikin da takeji, wani abun da yake bata mamaki mama bata bari ko su hada ido da ita Kuma yanzun tafi zama adaki.

Kamar yadda Umma da maman Sadam suka fada, tun daga wannan ranar bama abarin abincin a inda zata gani bare ta diba, haka Kuma ko tukunya bata gani bare ta daura ruwan da kanta, kwana biyu tayi batayi wanka ba hakama yaron, dan haka yau tun safe yake kuka, ita kanta jikinta yai mata tsami, misalin karfe daya na rana ta leka dakin Umma lokacin mama tana zaune bisa sallaya, cike sauri Mama ta kawar da kanta yayin da Aysha ta kalli Umma tace, " Umma dan Allah kibani aron tukunya yau kwana na biyu banyi wanka ba"

Inbaki aron tukunya?, Mena gaya miki?

Umma nace kiyi hakuri dan Allah.

Lallai kina wasa dani, da ta wuce Kuma baZata dawo ba Aysha, daidai da garwashin rushi kika tamamin Allah ya Isa.

Zuwa wannan lokacin zuciyar Aysha ta fara tafarfasa take dan haka ta juya tabar gidan

batare da tasan inda take saka kafarta ba.

Tunawa tayi da yaron, haka nan taji gabanta ya fadi, bata taba jinsa aranta kamar yau ba, cikin sauri ta shiga gidan iro, halin da take ciki ta gayawa matar iro cikin tsananin tausayawa ta bata ruwan zafi cike da bokiti, cikin sauri ta koma gida saidai tun daga zaure takejin ihun yaron a tsakiyar gidan ta aje bokintin ta shiga dakin, Innalillahi wa inna ilaihir raju'un ta fada lokacin data hangeshi akasa.

Cikin sauri ta daukeshi tana jijjigawa, tsananin tausayin yaron ne ya dirar mata lokaci kuda daker yai shiru sannan tasa masa nono a baki, zuwa can yayi gyatsa dan haka ta masa shin fida akasa sannan tai sauri tayi wanka da dawo, bayan ta shirya a gurguje tai masa wankan ta shirya sa.

Tun daga wannan lokacin saidai taje gidan iro ta roko ruwa ranar da basu dashi kuwa rushi matar iro take bata ta tsuna na tsayon lokaci, sannan ta bata ruwan zafin da zata sha, da Wanda zatama yaron wanka, yaron ko yanayin kwana biyu zuwa uku babu wanka saboda itama matar iro tsoron Umma take ji.

Ahaka har sati hudun da Aliyu ya fada suka cika, gashi komai nata ya kare wadda ya bar mata, ranar da ya cika sati biyar da tafiya Husna da Innawo sukazo da ledoji kayayyakin da suka mata sayayya, awulakanci Umma da Maman Sadam suka amsa gaisuwar su.

Sosai sukaga Ayaha ta fige ta lalace duk alamu ya nuna azabtar da ita sukeyi, yaron ma daganin sa babu wani cikkiyar kulawa a tattare dasu gaba daya, sosai Innawo ta tausaya mata har suka koma gida tanajin damuwan Halin data sameta aciki.

Ranar da Aliyu ya cika sati na shidda Aysha ta tsinta kanta da tsananin haushin sa ganin idan yai alkawari baya cikawa, fushi tayi dashi sosai tare da rasa inda ya dusa, tuni taso ta gudu tabar gidan malam idi da matarsa suka hanata, dan haka yanxun takejin yakai lokacin da zata gudu tabar garin batare da sanin kowa ba barema a hanata.

Cikin dare tai niyayyar barin gidan dan haka tun yamma ta shirya kalifa taimasa wanka bayan kwana uku daya dauka babu wankan, goyesa tayi ram abayanta yayin da zuwa yanzun ya cika bayan nata.

******

Momy gaskiya garin ku da nisa, har yanzun bamu Isa gidan Ummin Uncle Aliyu ba.

Da nisa Sadiya shiyasa kikaga Ina dadewa banzo ba.....

*⚫ BA'KAR  FURA⚫*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

PEN WRITERS ASSOCIATION✍️

Episode   54- 55

Akofar gidan Innawo motar ta tsaya, ahankali suka fara fito da kayan su sannan suka nufi cikin gidan Innawo.

A'a lale lale, kune tafe da yamman nan.

Wlh Innawo tun shekaran jiya muka taso, motar ba sauri.

Afalon suka baje tare da cire mayafin su, Ummi ce tafito daga bayin cike da murmushi ta fada Sadiya tana fadin an girma rabon ki da kasar nan tun kina goye.

Cike da fara'a Aunty Ruqayya tace, aitace girin ku da nisa.

Dariya akayi yayin da Innawo ta juye masu ruwan wanka, bayan sunyi wanka sukayi Sallah magariba domin lakacinta yayi sannan Ummi ta baje masu abinci.

Bayan sun gamaci ne Aunty Ruqayya da 'yarta sadiya suka kwanta nan tsakiyar falon suna hira yayin da Innawo da Ummi suke zaune, hiran suke cike da nishadi suna ta dariya zuwa can Innawo tace, " wai Aliyu ne ya gaya miki ina kiranki koko kawai dai kinzo ne?

Shine ya gaya min Innawo, sau uku yazo musamman ya jaddada min lallai kina son ganina.

Ya gaya miki abun da ya aikata?

Cikin sauri Ummi ta kawar da kanta tare da daure fuska sosai.

A'a me yayi?, nidai yazo kawai yace min ya dawo.

Dan Murmushi Innawo tayi sannan tace ai kanin ki mgn ya dauko mana.

Wacce irin mgn Innawo?, tashi tayi zaune tana kallon Innawo sannan ta juya ta kalli Ummi data hade rai, ko ba'a fada ba tasan Ummi fushi take da Aliyu.

Innawo ce tace, kunyi d'a, danku nan kato nan gidan Umma.

Cike da mamaki tace bangane ba??

Ummii ce tace, yariya yama ciki harta haihu.

Subuhanallahi, Aliyu?🤔

Shifa, Ummi ta bata amsa"

Innalillahi wa inna ilaihir raju'un, wacce yariya kenan?

Innawo ce tace ita dai wannan yariya Aysha da aka rabashi da ita, kinga rabawar ma beyi amfani ba.

Kashhh, abu beyi dadi ba Innawo, toh wai ita yariya ba annan take ba?

Innawo ce ta kwashe komai ta gaya mata duk yadda akayi, kama bakinta tayi tare da fadin, haba, biri yayi kama da mutum, watanin baya Aliyu ya tashi hankalin sa har nima yazo ya daga min nawa, cikin tsananin damuwa yake zuwa ya kwata min ajiki wai in kwantar masa da hankali kamar yadda Ummi ke masa, sannan sau uku yana sa ranar tafiya har yazo yamin sallama amman washegari saina ganshi ya yazo wai shi ya kasa tafiya gabanshi faduwa yake, ba irin tunanin da tunanin da banyi ba.

Aikuwa dai yanzun anbata da Ummi, dan ta kunkunduma masa zagi manya manya ma kuwa, badan Ina tsakani bama inajin tsine masa zata yi, dan naga kamar tayi niyya.

Idon Ruqayya cike da kwallah tace,  ayya Ummi ba halin shi bane fah, dan Allah kiyi hakuri.

Kawar dakai Ummi tayi, yayin da Aunty Ruqayya tace toh aini banga ta zama ba, barin je in dubosu in dawo.

Ki bari saida safe Mana.

A'a Ummi yanzon zani ni daman bansan yariyar ba, yakamata ace komai ya wuce yanzun,

mu rungume yariyar mu nuna mata kauna, tunda yana sonta, wlh Ummi zan iya rantsuwa tsautayi ne, kanina ko acen bashi da rawan kai, Baffah ma fada yaketa masa akan yiyi aure, amman wlh ko budurwa bashi da ita.

Cike da taici Ummi tace, " itafa zai yi rawan kai, bayan ya kala rai nan, ai daman hakane, duk matsalar da abun da mutum zai aikata sai ace tsautsa yi.

Mikewa tayi ta yafa gyalenta sannan tace ma 'yarta Sadiya tashi muje.

******

Tundaga zauren gidan sukejin kamshi, sallama sukayi bayan an amsa musu suka shiga ciki.

Umma ce da Maman Sadam suke cin abin ci, gaisawa sukayi sannan sukace, " Aysha suke nema"

Umma ce tace, au Ruqayya ce, da hannun suka nuna mata dakin tare da fadin, " tana nan ciki.

Dakin suka nufa daga yaddda suka mata tasan ba wani shiri suke da itaba, sallama sukayi daga ciki Ayaha ta amsa, dan haka suka shiga.

Gaisawa sukayi sannan Auny tace, nasan baki sannin ba ko?

Eh.

Ni Yaya Aliyu ce daga Nigeria.

Ayya, sannu dazuwa, fuskarta ta dan sake kadan, kallonta Aunty Ruqayya tayi sannan ta kalli akwatin dake gabanta, hijjabinta na kan akwatin, itako harda takalmi akafarta, ga dukan Alamu dai fita zatayi, dan haka Aunty Ruqayya cikin nazari tace, " fitama zakiyi kenan?

Eh wlh, Aysha ta fada tana kawar da ido.

Toh dan bani yaron ingani Mana.

Mikewa tayi ta kwantoshi ta mikawa Aunty Ruqayya sannan ta koma ta zauna.

Ido Ruqayya ta zubawa yaron fuskanta cike da murmushi, tabbas wannan karamin Aliyu ne, idonta akan yaron tace Ina zakije naga harda akwati?

Kawar da kanta tayi yayin da hawaye ya zubo mata tai saurin sharewa.

Da kallo Aunty Ruqayya ta bita zuwa can tace, kin dai san akwai aure akanki bekamata ace kina fita babu izinin mijin ki ba, ko kuwa ya baki dama kije wani waje ne??

Idonta akasa tace a'a.

Shine kike kokarin fita harda su daukan akwati?

Toh aunty yaushe nasan ranar da zai dawo dahar zanzauna Ina jiran Umarnin sa, bakin ciki ne zai kashi kawai, bazan zauna jiranshi ba.

Kallon Aysha aunty tayi tsayon lakaci, damuwa karara afuskanta tagani dan haka tace, kenan wannan kayan da kika hada garin Zaki bari?

Kawar dakai tayi sannan tace a'a.

Eh Mana, toh Ina zakije da daddaren nan?, kina jira mutane su shiga daki ko???

Dagowa Aysha tayi suka hada ido sannan tai saurin mayar da idonta kasa.

Aunty ce tace, " toh wlh karki fara, nasan aiki ne ya tareshi ba wani abu ba, sanda na tahoma baya garin, kiyi hakuri yana nan zuwa ko Kuma ki shirya sai mu tafi tare.

Kawar da kanta tayi can gefe yayin da aunty Rukayya ta sake cewa ki shirya sati daya zanyi sai mukoma tare.

Ni bazani ba aunty, ai shi yama manta dani yanxun, daman ance min bazai dawo ba Kuma ko naje bazai bari in ganshi ba😭

Cike da Mamaki aunty take kallon Aysha sannan tace, duk wadda ya gaya miki haka ya fadane kawai, Aliyu ba haka yaje ba, ninasan zai dawo ba haka Aliyu yake ba.

Kawar dakai tayi sannan tace, wlh aunty haka yake, wancen karon ma cemin yayi wata Uku, Amman bezo ba saida aka kusa shekara, haka yake, beda alkawari, nasan bazai dawo ba ko zai dawo saina kusan mutuwa da wahala, haka yayi min waccen karon,  amman bakomai ba laifinsa bane, laifinane, da banje gurin saba da yanxun Ina zaune lafiya da 'yan uwana cikin mutunci, kamar yadda yake zaune da nashi, Ina shan wahala arayuwata, gara min mutuwa da wannan rayuwar, kowa ya juya min baya cikin harda Yaya Aliyun......

A'a kam, kicireshi aciki, nasan rankine ya baci, Kuma shi besan halin da kike ciki ba......

Ya sani, saidana gaya mishi, yace min in basu hakuri, Kuma nata basu har nagaji, basa sona, basa son ganina, saidai in fita in sawo abun da zanci, ruwan wanka kuwa sai dai inje makota in

roko, inayin kwana biyu uku banyi wanka ba.

Innalillahi wa inna ilaihir raju'un, aunty ta fada, sannan ta mike ta mikawa Sadiya dake kuka yaron ta koma kusa da Aysha ta jawota jikinta ta rungume, itako Ayaha fashewa tayi da kuka sosai, tana jinta rungume jikin Rukayya rabonta dataji an rungumeta haka tama manta, ashe rungumewa ma rahama ne, Kara shigewa jikin Rukayya take tamkar zata shige jikinta, ahankali Rugayya tace Aysha Ina mahaifiyar ki take duk wannan abun yake faruwa?

Tana nan acikin gidan nan, amman ita bata cewa komai, sai abun da su Umma sukace, nasan ko bataso yadda suke min bazata iya hanasu ba, Kuma itama bazata kulani ba haka take tuni nasani.

Jimmm tayi, sannan tace, toh kishirya rana ita yau zan kaiki gurin mijin ki.

Cikin sauri ta dago daga jikin aunty ni bazani gurin saba aunty ai yana sane Dani yabarni anan.

Amman Aysha ki masa uzuri mana.

Baya ta juyawa aunty tana wasa da hannunta ganin haka aunty tace shikenan nasani Aliyu yayi laifi, be kyauta ba, yanzun abun da nake rokon alfarma wajen ki, tunda ba xaki gun Aliyu ba, ni kibini ki zauna gurina tunda yanzun inma fitan kikayi bakisan inda Zaki ba.

Cikin kuka Aysha tace Aunty bazani ba dan Allah kiyi hakuri.

Ajiyan zuciya aunty Ruqayya tayi har ga Allah ta damu da lamarin Aysha, hannunta ta daura akan gado bayan Aysha, sannan tace, " yanzun kenan inda Allah be kawo ni yau ba garin Zaki bari?, In kin fita kinbar gida yanzun kinsan hannun wa zaki fada ne?, haba Aysha, shikuma Aliyu idan ya dawo akace mishi ba'asan inda kike ba kina tunanin awanni hali Zaki sashi??

Aunty ni babu abun da ya dameni dashi, ba halin da zai shiga, yana sane yake yin haka, ni daman ban sanshiba arayuwata, tunda nasanshi nake shiga cikin matsala gashi kullum kara gaba take, shikuma janyewa yake, garama mota ta takeni na mutu in huta.

Cikin tsananin tausayawa Aunty tace kibar irin wannan tunanin, Kuma ki daukeni kamar 'yar uwarki, koma uwa kika maidani daidai ne, ko ban haifi kamarki ba kadan ya rage nafahimci kinyi fushi da Aliyu sosai dan haka mu aje zancen Aliyu agefe, ba Ina kareshi bane wannan kibarshi a tsakanin ku,  kibini muje gidana ki zauna tare dani.

Amsawa tayi kawai dan takula aunty ta tausaya mata sosai, Kuma yadda take rarrashin ta da Kunya tace mata a'a

Aunty ce ta share mata hawaye sannan tace kin fasa tafiyar ko?

Kai Aisha ta daga.

Yauwa nagode Aysha, yanzun bari muje da Khalifa amishi wanka sai adawo dashi.

Na mishi wanka da yamma ma aunty ko za'a bari da safe?

Toh aini kin banin tsoro ne Aysha, ganin nake kamar idan banje da yaron ba tafiyar ki zaki yi.

A'a ba inda zani Aunty na miki alkawarin bazanje ko Ina ba.

Toh nagode da safe Sadiya zatazo ta dauke shi.

*****

Koda Ruqayya ta koma gida labarta masu halin da ake ciki tayi, sosai Innawo ta tausayawa Aysha, haka kuwa washegari da sassafe Ta tura adauko Khalipa, wanka tamai tamai tana zubar da hawayen tausayin yaron, bayan ta gama shirya shi jikin Ummi ta daurashi tana fadin Ummi ki kalleshi dan Allah kisa mishi albarka ba laifinsa bane ?

Tunda Ummi ta daura idonta akan yaron ta fashe da kuka, shikuwa yaji dadin wanka sai wuntsula kaba da hannuwa sama yake yi, sai rana aka mayar mata dashi, tundaga wanna. Ranar kullum Sadiya take kaiwa Ayaha ruwan wanka sannan ta dauko yaron amasa har suka cika kwana biyar, aranar ne Innawo ta shiga gidan ta kanta ta sanarwa Umma gobe za'a tafi da Aysha gurin Mijinta Nigeria, tana bude baki kuwa tace Allah ya rakata taki gona.

Tun aranar Aysha tafara hada kayan ta, bawani abu me yawa ta diba ba, akwati daya tayi nata Dana Khalifa, haka takejin duk zuciyarta babu dadi, saidai tana matukar son tabar gidan dan ayanzun dataga Umma gabanta har faduwa yake, hakama Maman Sadam garama Aunty Murja mgn ne batayi da ita amman bata gaya mata bakar mgn, washegari ne ya kama ranar da Innawo tace zasu tafi tun safe ta shirya saidai tana balakin son taga mamanta ba gani irin wadda ta saba mata ba, ganinta take son tayi mata ido da ido suyi mgn duk da tanajin zafin yadda take mata amman tana son ganinta.

Sai dai data fita saitaga maman Sadam na mata wani mugun kallo wadda tasan ko taje gaban mamanta indai maman Sadam na wajen bazata mata mgn ba.

Misalin karfe 6 na yamma Innawo da Sadiya suka shigo, a tsakar gida ta samu maman Sadam da Umma bayan sun gaisa tace nazo tafiya da Aysha.

Toh Allah ya taima ka, Sadiya ce ta shiga ta dauko akwatin ta fice yayin da Aysha ta fito sanye da hijjabi Innawo kuwa khalifan ta dauko.

Aysha kuwa kasa daga kafarta tayi daga kofar dakin dan haka Umma tace kije kiyi sallama da maman ki.

Maman Sadam ce tace a'a tayi bacci, Innawo ce tace eh kotana macci ta shiga haka.

Aysha bata jira amsan suba tashige dakin, yayin data samu  Mama kan Sallaya, tsugunawa tayi gabanta, cikin fashewa da kuka, yayin da Innawo take tsaye saman Aysha take fadin, Aysha zata tafi gidan mijinta kisa mata albarka

Ahankali Umma ta motsa bakinta tace, Allah ya bada sa'a.

Innawo ce ta amsa da Ameen, sannan ta dago Aysha suka fito tana waiwayen mahaifiyar ta, suko su Umma har Aysha ta fita agidan maganganu suke marasa dadi wadda ke nuna sun yake zumunta da Aysha har abada.

Sosai Aysha take ganin bakinsu cikin ranta, badan Mamanta da Daddyn taba da zata iya fushi dasu da tace ita da gidan har abada,  gidan Innawo suka nufa, Ummi da Aunty Rukayya ne a falon,, Innawo ce ta mikawa Ruqayya yaron sannan ta nunawa Aysha gurin zama tana fadin, kiyi hakuri kinji ko, insha Allahu wata rana sai labari.

Aysha ta dade kudun dune cikin hijjabi sai bayan Sallan mangariba ta sarara da kukan, saidai ko mgn bata iyawa, washegari sunyin sallah asuba suka kama hanya,  har tasha Ummi da Innawo suka rako su duk da cewa babu fara'a afuskan Ummi amman ta masu fatan sauka lafiya, harma ta ziro hannun ta cikin motar ta gyara daurin hulan Khalipa tana fadin a gyara shi kada iskan mota ya sashi mura, har ma ta Kara da cewa aunty Ruqayya karbe shi ne.

Hanya suka kamo yayin da Aysha takejin babu dadi cikin ranta,  sunyi tafiya me nisa sannan ta tuna da Babanta ko tantama batayi yayi tafiya ne da bazai taba daukan wannan lokacin bezo ba.

*****

Oyoyo Uncle Aliyu.

Tohowa sukayi gaba dayan su yaran maza da mata suka rungume shi, cikin wani irin yanayi yake daga kananan sama sannan ya Isa kujera ya zauna yana fadin, " Inna aunty?"

Wani Dan saurayi ne da bazai wuce shekara 16 yace tana Cameroon.

Lumshe ido yayi sannan yace, " yaushe ta tafi??

Yau kwananta 8.

Ta gaya muku ranar da zata dawo??

A'a

Mikewa yayi yasa hannun sa cikin aljihu ya ciro kudi ya mika ma yaron yana fadin, "kabawa Yaya Fahat Ina sauri ne, idan aunty ta dawo daga nan zuwa gobe da daddare komai dare kazo ka gaya min.

Gida ya koma cike da damuwa saidai yana shiga falon cikin daga murya Baffah yace, " Ina Ruqayya?"

Sunkuyar dakai yayi yace bata nan.

Ina wasa dakai ne???

Wlh Baffah bata nan yaranta ne kadai agidan sunce tana Cameroon.....

https://youtu.be/7ZOCexBfeL4

*⚫ BA'KAR  FURA⚫*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

Episode 56- 57

Komawa Baffah yayi ya zauna yana cike da bacin rai, yayin da Momy take fadin, " kayi hakuri kabi komai ahankaali.

Aliyu kuwa kansa akasa ya juya ya koma dakinsa tare da fadawa kan godo yai ruf da ciki yana fadin, koma me Baffah yake zargina dashi nasan bazai wuce kan wancen auren bane

dan haka sosai yaji hankalin sa ya tashi, addu'a yake Allah yasa aunty ta dawo, domin yasan dole Innawo zata aikota gurin Baffah, sai dai itama besan yadda zata dauki zancen ba.

Washegari tashi yayi da matukar zazzabi sabo da yadda yake Jin damuwa sosai, gashi agobe yake son zuwa Cameroon amman Ina, yana tsoron yadda zai fad'awa Baffah.

Daker ya iya daurewa da yamman ya fito misalin karfe 5, bemasan inda zashiba kawai dai fitowan yayi, motarsa ya shiga ya zauna yana kokarin tadata yaga an bude gate din gidan, motar gidan su aunty Ruqayya yaga tana shigowa, take ya sake ajiyan zuciya batare data sani ba, domin yasan duk yadda akayi aunty ta dawo kenan.

Jira yake yaga danta Abba ya fito amman abun mamaki ita da kanta ya gani tana saukowa.

Cike da zullumi ya bude motar ya sauko, ya nufeta, yayin da tana ganin shi ta sake murmushi.

Dafda ita ya tsaya aunty yaushe kika dawo?

Jiya da Yamma, ance min kaje, Ina ta Allah Allah karka kama hanya.

Gobe nake da niyar  tafiya, wani aikine ya taidani.

Ka makara matarka nata fushi dakai.

'Dan kawar takai yayi domin zuwa yanzun yasan tasan komai, cike da sonji yace, " kinje ne?"

Eh bama sau daya ba.

Sunanan lafiya ko?

Lafiya Lau, to Kai yaushe ka dawo?

Jiya da safe, nadawo ma nasamu Baffah sai fad'a yake yi, yana nuna wai yana zargina bani da gaskiya, jiyan ma shine yace in Kira masa ke.

Dan takatawa tayi da tafiya tana fadin, wani ya kawo masa labari ne?

Shine ban sani ba Aunty.

Jimmm tayi zuwa can tace, " ai yana gida yanzun ko?

Yana nan.

Barin je karka shigo, idan ba kiranka yayi ba .

Amsawa Aliyu yayi sannan ya koma cikin motar sa ya zauna.

Ruqayya ko ciki ta shiga cikin fara'a Momy ta tareta, bayan tace mata gurin Baffah tazo aka kaita har falon sa, Baffah na sauke ajiyan zuciya suka gaisa da Ruqayya, sannan yace mata, daman Ina son ganin ki, jiya na aika Haydar ya kiramin ke yace kinyi tafiya.

Eh Baffah Ina Cameroon, jiya da daddare muka shigo, toh daman Innawo ta bani sako tace Ina dawowa inzo in isar mata da sakonta gurin ka.

Toh toh naji, nima Ina son nai mgn dake, amman kafin nan bani sakon na Mama.

Shiru Ruqayya tayi tama rasa ta Ina zata fara, zuwa can tace, nima zuwa Cameroon din kirana tayi, tunda naji kira nai saurin tafiya, toh daje sai take min bayanin cewa akwai yariya data sauka a agidan nan watannin baya, wadda Aliyu yazo da ita.

Eh tabbas matar abokin Aliyu ko?

Eh toh, Innawo tace kayi hakuri kuma ka fahimci zancen dakyau dan Allah.

Inajin ki, muje, muje Ruqayyatu.

Toh Baffah wannan yariyar ba matar abikon sa bace kamar yadda ya gaya maka.

Innalillahi wa inna ilaihir raju'un, Baffah ya fada sannan ya tsare Rukayya da idon sa yana fadin inajin ki.

Baffah wannan yariya ta dalilin ta Ummi ta koro Aliyu daga can Cameroon ya dawo nan da zama, domin sun nuna suna son juna, Kuma anyi anyi su rabu sunki, a yadda suka bani labari family yariyar ba inda basukai mgnr ba har kotu anshiga, amman sunki rabowa da juna, dan haka ta turoshi gurin ka kawai.

Subuhanallahi, kinji irin abun ko?, amman da Aliyu yazo nan, ba yadda banyi dashi ba inji dalili yaki fada min, daga karshe nabarshi kawai tunda Naga bason fada yake ba.

To Kuma Baffah sai gashi ya kumayin wani kuskuren agaba, domin da yariyar ta biyo shi

nan  kasar bayan shekara biyar da rabuwan su Ya kamata ya sanar maka sabo da abashi shawaran abun da ya sace.

Shiru Baffah yayi yana jinjina zancen, cikin ransa zuwa can yace, " a'a ikon Allah, bana mantawa lokacin na mishi fada akan zuwanshi da ita, amman saiya rufemin baki da fadin ajiyansa aka bashi Kuma ma matar Aure ce, toh abun da yasa ban damu ba lokacin, yariyar cikin su Meenat ya barta, daga baya yace min Mijinta ya dawo, tazo tamin sallama na mata alheri, duk ta saba da yara, yanxun haka ko jiya sunata cewa zasu zasu Cameroon gurin ta.

Ai Baffah da yace maka Mijinta ya dawo mota yasata ta koma gida, Innawo tace dan Allah Kai hakuri karka dauki zancen da zafi dan kafin ta koma gida wani abu ya shiga tsakanin sa da yariyar........

Batakai ga karasawa ba Baffah ya dafa kansa yana fadin Innalillahi wa inna ilaihir raju'un.

Yana rike da kansa aunty Ruqayya tace Baffah dan Allah kayi hakuri abun da suka guda kenan suka turoshi nan, amman dake kaddara ta riga fata soyayya najanta, saida ta biyo shi nan, bayan Kuma ta koma da wata uku iyayenta suka gane tana dauke da ciki, wadda aka rasa inda ta samushi, domin bata kula kowa, Baffah saida yariyar ta haihuwa aka tabbatar d'an na Aliyu ne, domin jinin sa ya nuna sosai Koda yariyar bata fada ba yaron yayi kama dashi kamar an tsaka kara.

Motse baki Baffah yayi idon sa akasa sannan ya dauke gilashin sa dake gefen kujera yasa a idon sa, daker ya iya bude baki yace, shikenan sai ya aureta kawai.

Jimmm, Aunty tayi sannan tace, " eh bayan yaje lokacin ta haihu kotu suka kaishi, nan ta kwashe komai ta gaya masa har tahowan da tayi da yariyar.

Bayan ya gama sauraron Ruqayya yace, " shikenan Ruqayya bakomai, ni musulmi ne dole in amshi kaddara mekyau da mara kyau, ni daman naji kishin kishin din yayi aure a Cameroon, naji daga wani abokina da nake bawa sako na musashi, ganin wani ya sake min mgn nace barin tuntube ki, su Kuma iyayen yariyar ai bekamata suyi watsi da ita ba, wannan auren da akayi shine maganin abun, Kuma wannan ya Isa yasa zuciyar su ta huce, Amman fa laifin na Aliyu ne, inda ya gaya min tunfarko da ke zan nema kisata agaba ki mayar da ita gaban iyayenta,  su Kuma iyayen idan suna da hankali lokacin zasu gane auren shiyafi dacewa dasu.

Ai Baffah iyayen yariyar nan banjin kome za'ayi zasu bada ita.

Toh shikenan, abun da ya faru ya riga ya faru, yanzun abun da za'ayi tunda Aliyu beda gurin zama, besa zaiyi aure ba bare ya nema, wancen part din daman can danshi na gina shi, yariyar tazo ta zauna aciki amman fa duk abun da zanma Aliyu yanzun zan masa domin yariyar ne, domin yariyar ce abun tausayi idan bata samu farin ciki ba akwai matsala dole Aliyu ya riketa dakyau, idan har yana son in huce dashi ya kyautatawa yariyar nan, akanta zan bashi

mamaki matsawar yace zai wulakantata. Tun shine silar lalata mata rayuwarta, Ina da 'ya'ya mata idan aka masu bazanji dadi ba, dan haka itama yariyar nasoko cikin yarana idan ya nemin ya wulakantata zan rufe idon incimai mutunci, wannan shine sharadina.

Cike da farin cike Aunty tace toh mungode Baffah insha Allahu zasu zauna lafiya.

********

Aliyu taganin tahowan Aunty ya fito cikin motar, yadda yaga fuskanta yasashi ya sake murmushi yana fadin, " kungama?"

Eh, ya fahimta, amman kasan dole zaiji babu dadi, ya Kuma ce babu wulakanci, Kuma a kanta zai iya saba maka, yana nufin dai beson rigima, yana son ka rike ta amana.

Ba rigimar da zamuyi aunty, ko munyi ma babu meji kanmu.

Murmushi tayi sannan tace Allah yasa, amman ai koni yanzun najiku, tunda Aysha bakaramin fushi take dakai ba, samunta nayi fa ta hada akwati zata shiga duniya, sabo da fushin da take dakai.

Nashiga uku, ya fada yana zare idon, tare da fadin, har kin Kara min tashin hankali, Anya kuwa baxan tafi yau ba?, toh aunty kinji dai nayau, amman insha Allahu wannan ne nafarko da kikaji kanmu kuma na karshe.

Dariya aunty tayi sannan tace, zafi kowa farin ciki da hakan kuma lokacin ne zan tabbatar daku masoya ne, Aysha kuma daker na dakatar da ita, Amman zakazo gidan mu da daddare ko?

A'a kam, muyi sallama kawai yanxun?

A'a kaxo.munyi da ita zam bada sako ka Kai mata.

Kansan ya sosa kadan sannan yace saina zo toh.

Motar ta shiga suka bar gidan yayin da Aliyu ya koma cikin gida yana sauke ajiyan zuciya.

Misalin 8:00pm Aliyu ya fito da nufin zuwa gidan aunty saidai yana son ya sanar da Baffah gobe zai wuce Cameroon dan haka ya fara zuwa falon sa, da sallama ya tura kofar ya shiga, Islam da Meenat ne suka amsa Baffah ko juyar da kansa yayi can gefe.

Zama yayi agefen sa yana fadin Ina wuni Baffah.

Lafiya, kawai ya iya cewa fuskan sa babu alamar walwala, Su Meenat ne suka gaidashi ya amsa sannan ya sake kallon Baffah yace, "  gobe zanje Cameroon.....

Tun be rufe baki ba Baffah yace, " ka gaishe su.

Kasa tashi yayi domin ba haka suka saba sallama ba idan zaiyi tafiya, ya dade zauna sannan ya tashi jiki ba kwari ya fito.

Baffah kuwa Aliyu ta nafita ya mikawa su Meenat key din part din da Aliyu zai zauna yana fadin, " ku rike wannan masu aiki zasuzo gobe su karba.

Baffah na meye ne key din?

Na wancen part din ne, yayan ku zaizauna aciki da matar sa.

Baffah zaiyi aure ne??

Yamayi a Cameroon.

Idon suka zaro saidai sun kula kamar Baffah bayajin dadi dan haka sukayi cikin gida.

Basu dade da fita ba Momy ta shigo lokacin Baffah yana dafe da kansa, kallon sa tayi sannan tace Alhaji wani Ibr naji abakin yara, wai da gaske Haydar yayi aure a Cameroon??

Eh, yayi.

Amman Alhaji kana nuna min iyakata agidan nan, wato sabo da banice uwar shi ba bazaka gaya min komai da ya shafe shi.

Kiyi hakuri, cikin bacin rai nake, abu me dadi shi kake rawar jikin gaya, Ina wannan yariyar da ya taba sauka agidan nan?

Eh naji matar abokin sa.

Karya yamin kawai matar sa ce.

Innalillahi wa inna ilaihir raju'un, lallai ma Aliyu.

Baffah da beson zancen yai nisa mikewa yayi kawai ya nufi dakin gidan mahaifiyar sa.

******

Ai danaga har 08:30pm baka zoba na dauka baza kazo ba.

A'a aunty, na tsaya gurin Baffah ne, kince ya fahimta amman naga daker yake min mgn.

Cikin ido ta kalleshi sannan tace karka damu da wannan, Kai inda ace da yariyar da 'Dan kazo mishi ai da kun kwasa 'yan kallo, karka damu ai abun ma yayi kyau, kama godewa Allah, har cewa yayi fa ga guri nan ka zauna kafin ka nemi wani.

Karyar dakai Aliyu yayi yana fadin, toh yanzun aunty bani sakon in wuce sauri nake yi"

Toh shiga daki yana nan gefen gado ka dauko.

Mikewa yayi yabi hanyar data nuna masa, be taba shiga dakintaba amman Kai tsaye ya tura kofar.

Babban dakine me dauke da wawakeken gado, idon sa ya sauka akan wani yaro dake ta wasa da kafarsa da hannunsa, sai kushin kushin yake, tsintan kansa yayi da saurin karasawa, saidai idon shi na sauka akan yaron yaga kamar gizo ne dan haka yasa hannun sa yana kokarin daukan yaron tare da saurin juyawa yana Kara kallon yaron.

Cak ya atsaya alokacin da yaga Aysha ta fito daga wanka towel daure bisa kirjinta yayin da ta yafa wani a kafadanta.

Binta da kallon yayi sosai yake mamaki yana Kuma tsareta da ido.

Itako Aysha ganinsa ya sata daure fuska sosai, tasan dole ne yasan tana gidan Amman bata zaci zasu hadu da wuri haka ba, ganin inda yake binta da kallo tundaga sama har kasa yasa tai saurin komawa toilet din yayin da yai saurin takowa tare da mika hannun sa, adaidai wannan lokacin ta bugo kofar tare da fadin, wayyo aunty!!!

Runtse idon sa yayi saboda zafin da yaji sosai kofar ta matse hannun sa, yayin daya kara rike Khalipa dakyau da hannun sa daya yana fadin, "Aysha menene haka?, daman kun taho tare?, Aysha ki bude kofar mana"

Arikece Aysha ke Kiran sunan aunty ganin haka Aliyu yace, " ki bude ki fito, kibar kiran aunty haka.

Nika fita, bana son ganin ka.

Ni din?

Eh.

Haba Ayaha nine fa yaya Aliyu malamin ki, daman d'aliba tana fushi da malaminta ne???

Toh bakai bane saikamin alkawari baka cikawa dan kawai kaga bana gurin, ka manta dani😭

Nidin?, akasi ake samu Aysha, tayaya zan mance ku, arana bana iya kirga so nawa nake tuna ku, kiyi hakuri kinji.

Ni ba kalmar da zaka gaya min.

Toh naji, yanzun fito ki amsa Khalipa.

Ka ajeshi inda ka ganshi.

Toh zan ajiyeshi, sai yaushe zan ganki to??

Ni karka sake min mgn.

Kawar da kansa yayi daga kallon kofar, Khalipa ya zubawa ido sannan yace, naji bazan sake miki mgn ba, amman kibani rana da lokacin da zan miki mgnr.

Jinta shiru yace mgn nake fah.

Ni babu ruwana dakai

Lumshe ido yayi sannan yace, aure muka yi fah Aysha, kinta ganin mata tace babu ruwanta da Mijinta alhalin tana karkashin ikon sa??

Wannan karon batace komai ba,dan haka yaci gaba da cewa, ," baya ga haka Kuma ke dalibata ce, Kuma har yanzun ni malamin ki ne dan haka ki fito kawai.

Yana gama fadin haka ya koma bakin gadon ya zauna yana me zubawa kofar ido, zuwa can yajita cikin kasa da murya tace, " ka dan miko min hijjabina.

Akwai yaro a hannuna kizo ki dauka.

Ka ajeshi mana

A'a, ya fada sannan ya dauke kansa yana cigaba da fadin, Idan sabo da nine na juya baya na ki fito abun ki.

Lekowa tayi taga ya juya bayan kamar yadda yace, dan haka ta fito tai saurin daukan hijjabinta ta sanya, shiryawa tafara, yayin da Aliyu ya maida hankalin sa kan Khalipa tsayon lokaci sannan yace, " idan kin gama zan wuce.

Can kasa tace nagama.

Juyawa yayi ya kwantar da Khalipa tare da tufa masa addu'a sannan ya mike har ya wuce ya miko hannunsa ya jawota ya hada ta da kirjinshi ya rungume.

Sosai ya rungumeta tamkar wani zai kwace ta, ajiyan zuciya yake saukewa da karfi yayin da numshin sa yake sauka a tsakar kanta lokacin daya yake kewaye duk ilahirin jikinta, nan danan taji jikinta na amsawa, bata so ta sauko da wuri haka ba dan haka ta kokarin ta dake, daker take iya turesa take kaimasa duka.

Duk inda ta nemi ta kubce rokota yake, gashi tanayin abun ne cikin kuka gaba daya.

Aysha kiyi hakuri, bason bacin ranki nan, gaba zaki tabbatar da haka, Ina tsananin sonki fiye da tunanin ki, kuma zanyi kokarin insaki farin wadda ba'a iya kwatantawa, kibar zargina akan rashin cika alkawari, na farko nasan da gangan nayi, saboda tun ranar da kika gayamin jiya kika gama al'adarki na rubuta na ajiye, Kuma saidana kirga wata tara sannan na kamo hanya, amman wannan karon akasi aka samu, dan Allah ki nutsu ki gaya min matsalar ki ayanzun dani, nikuma zanyi kokari in gyara komai, zama nake son muyi mekyau, Ina son ki bani hadin kai, ya kasance ni dake har abada babu mejin kanmu, ko wani abu ya faru tsanin mu ne kowa banson wani yaji, nasan halin ki kinsan nawa, nasan kina da taurin Kai, ni Kuma ina da zafi idan raina ya baci, yanzun kinsan me nake so dake???

Tana kwance akirjin sa ta kirgiza kanta.

Bani shawaran hukuncin da zan dinga miki idan kin kureni da taurin kanki, nikuma zan baki shawaran abun da ya kamata kiyi idan fushina ya tashi har kika rasa inda zakiyi dani......

https://youtu.be/Mt6vnqmJOxM

*🕳 BA'KAR  FURA🕳*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

Episode 58- 59

Tsintan kanta tayi da sakin murmushi tana kwance a kirjin sa, saidai ta gaza cewa komai.

Ganin haka Aliyu yadan dagota yana me kura mata ido yace, " inajin ki, kibude baki mu nemi mafita kinji.

Kwace kanta tayi ta koma ta kwanta jikin shi, ahankali tace, ni bani da taurin Kai yaya Aliyu.

A'a, banson sonkai Aysha, ni na yadda Ina da zafi, idan raina ya baci, kema ki yadda da taurin kanki sai mu nemi mafita kawai.

Jimmmm tayi, zuwa can tace to ai abu me saukine ya Aliyu, kawai cemin zakayi dauko littafin ki cikin buga irin wannan tsawar taka dake rudar dani, danaji haka zan shiga hankalina.

Murmushi yayi sannan ya Kara rungume ta tare da sumbatan Kumatun ta, sannan yace, "cemin zakiyi danaga kin fara tirjewa sai in hade fuska in koma Malam Yaya Aliyu?

Kai ta daga tana mejin wani farin ciki na shiganta cikin zuciyarta, ahankali tace kaifa ya zan yi dakai toh.

Kanta ya rungume sosai akirjinsa, yana Jin saukan numfashin da take har cikin zuciyar sa, sannan ya fara fadin, " idan Kinga raina ya baci har na fara fada, kinsan me zakiyi??

Kaita girgiza tare da fadin, " a'a"

Ahankali yace, " kurma zaki zama, duk abun da zance karki kulani, idan Kuma tambaya ce nayi, amsa kawai zaki bani, iyaka gaskiyar ki, har sai kin Bari na gama sai kice Allah ya huci zuciyar ka mijina abin alfahari na.

Cikin sauri Aysha ta dago ta kalleshi cikin idon, Yaya toh ai wannan wayo ne kamin, idan Kuma maganganun ka sun sauka daga kan layi fah???🤔

Eh duk da haka dai hakurin Zaki bani, idan akwai kalmar da kike ganin batai miki ba, bayan kin tabbatar da na huce saiki same ni da ita, nikum insha Allahu zan miki a dalci.

Ciki da gamsuwa tace shikenan.

Yauwa Aysha  barin zo inje gida Kinga dare yayi sosai, gobe zan zo, me zan kawo muku??

Babu"

Akwai, kiyi tunani da kyau.

Allah babu, idan Kuma akwai goben sai in gaya maka.

Amsawa yayi, cike da gamsuwa ya  saketa sannan ya juya ya fita.

Koda ya fito falon Abba kawai ya samu, tambayan sa yayi Ina aunty, amsa ya bashi da tana falon Abban mu, dan haka yace masa kace mata na tafi da safe zan dawo.

****

Gida Aliyu ya koma cike da tunanin Aysha, sosai yakejin nutsuwa na shigarsa mara iyaka, rabon da yaji irin sa ya manta, bacci yayi me dadi, hakama bayan ya dawo sallah Kara kwanceya yayi wadda har ya dauke sa 11:30 sannan ya tashi, wanka yayi sannan ya shirya cikin manyan kaya da hula, fitowa yayi da nufin zuwa gidan aunty, saidai yana fitowa suka hadu da Baffah, cikin sosa kai ya gaida shi bayan ya amsa ya wuce ya shiga motarsa ya zauna, harya tada motar yaji Baffah na cewa Hajiya na neman ka.

Amsawa yayi da toh sannan ya fito agidan.

Kai tsaye gidan Hajiya ya wuce, afalon ya sameta cikin tsananin Jin nauyinta ya gaidata, fada ta fara masa akan baya kula mutane ko zuwa gidan ta yanxun baya yi, yayin da ya bata uzurin aikin sa ne baya bashi daman haka akarshe yace zai dinga kokartawa yana zuwa.

Jinjina Kai tayi cike da gamsuwa sannan tace, jiya Babanka yazo min da wani labari mara dadi, duk da cewa kaddarace amman babu dadi Sam, Kuma baka kyautawa iyayen ka ba damu baki daya. Kaga na farko daga mahaifin ka har mahaifiyar ka sun jaka ajiki, suna nuna maka kauna, basuki su mika komai nasu agareka ba dan me zaka rufe su?, Ran Baban ka ya bacci, amman natunatar dashi cewa idan ka gaya mishi Yaya za'ayi agujewa kaddara, nabashi hakuri dan haka kaima ka sameshi ka bashi hakuri, dan kayi kuskure gaskiya.

Kawar dakai yayi ya fesar da ajiyan zuciya sannan yace, " toh nagode Hajiya, na karma kuskurena kuma Ina tabbatar maku ba abun da nayi da gangan kawai na tsinci kaina acikin kaddara ne,  insha Allahu zan kiyaye.

Allah ya baka iko, dan Allah ku dinga neman shawara, yanzun acen matar taka tana gidan Yayarka ko?

Eh tana can.

Toh ya kake gani, babu matsala?, Idan da matsala ka kawota nan ta zauna dan gaskiya yariyar tana bukatan kulawa.

Babu wata matsala Hajiya insha Allahu.

Allah yasa, duk wadda yai maka fada cikin 'yan uwa kabashi hakuri, domin jiya Baban ka dun ya tarasu yace masu kayi aure har matar da haihu babu sanin sa, wasu daga ciki ransu ya baci nima nayi fushe dakai lokacin saidaga baya yamin bayani, dan haka duk ma wadda yazo maka fada ka saurareshi kawai bayan ya gama ka bashi hakuri.

Nagode Hajiya.

Toh shikenan, Sai Kuma mgn ta gaba, Abbas yace baka taba lekawa gidan shiba tunda yai aure?

Juyowa yayi ya kalli Hajiya sannan yace, " lallai ma yaron nan ya raina ni, me zanje gidan shi inyi?, auto zuwan da nake ma gurin aikin sa mu gaisa be ishe shi ba har ma so yake Kuma in dinga zuwa gidan shi.

A'a to meye dan kaje gidan nasa?, Baka so kuyi zumunci ne??

Haba kanina ne fah Hajiya..

Wani irin kallo ta masa sannan tace ta yaya ya zama kanin naka?,🤔 kenan Kai baka da azumunci.

Ni ba haka bane Hajiya gidan sane dai bazanje ba, duk sanda nabi ta office din su in shiga, amman kawai saina tashi gotai gotai dani inje gidan sa.

Waini Tsaya in tambaye ka kaita Abass din waye gaba ne??

Cikin sauri yace, nine Hajiya.

Bakai bane, ai inajin Abbas yayi shekara da watanni yana shakar iskan duniya sannan aka haifika.

Wai da gaske Hajiya??

Sosai ma kuwa, kaje ka tambayi iyayen ka, shi bece ya girme ka ba yake son zumunci sai Kaine zakace wani wai gotai gotai son girma kamar gyanbo.

Dariya Aliyu yayi sanan ya mike yana fadin karma ki gaya masa wai ya girmeni dan Allah Hajiya, idan na samu lokacin zanje.

Da haka sukayi sallama da hajiya, masallaci yaje daganan bayan yayi sallah ya wuce gidan aunty yana me cike da farin ciki.

Tun kafin ya shiga falon yakejin muryanta ita da Sadiya suna hira cikin fulatanci dake aunty najin yasa itama Sadiya ta iya, sallama yayi ya shiga, yayin da duk suka waigo suka kalleshi cikin girmamawa, Aunty ya gaida yayin data amsa cike da sakin fuska, itama Sadiya gaidashi tayi yayin daya sata kallon Aysha dake durkushe gaban aunty tana rufe wata roba.

Kawar da idon sa yayi adaidai lokacin data ce Ina wuni?

Lafiya Lau ya fada kansa agefe yayin da yaci gaba da cewa Aunty me kuke hadawa ne naga duk hankalin ku ya dauke?

Kanina turare ne irin na wuta, jiya kuma saika wuce babu sallama bare godiya.

Murmushi yayi sannan ya maida da hankalin sa kansu yana cewa, "aini aunty baki taba sani farin ciki kamar yadda kika Sani jiya ba, sai jiya na dada tabbatar da cewa lallai bakaramin so kike min ba.

Dariya Anuty tayi tare da fadin, " gara daka gane, ai Ina son ka, Kaine kaita shareni agarin nan, Kuma abun da yasa ban gaya maka ba, Aysha cewa tayi indai gunka zan kawota bazatazo ba, dan tana fushi dakai....

Satan kallon Aysha yayi sannan yace, " aunty wannan mgnr fa babu ita, an dade da wuce gurin ko Aysha??

Satan kallon Aunty Aysha tayi sannan ta sunkuyar da kanta.

Cike da murmushi Aunty ta dubi Aysha tace wai babu ita Aysha??

Cike sauri ta kawar da idonta sannan ta daga Kai.

Aliyu ne yace da baki Zaki gaya mata.

Cike da Kunya Aysha ke buye fuskanta yayin da aunty tashiga tafa Hannu tana fadin, "yanzun duk wannan uban fushin da kikayi tashi daya kanina ya rugujeshi🤔

Shiko Aliyu fadi yake, "Aysha ki bude baki kiyi mgn, ganin tana kara boye fuska ya mike yana kokarin zuwa gurin su, ganin haka Aysha tai saurin mikewa tana fadin nafa amsa.

Ai dakai kika amsa bata gani ba.

Cikin kukan shagwaba tace, ai tagani so kake kawai inji kunya.

Dariya Aunty tayi tana fadin, " Kanina rabo da ita.

Komawa yayi ya zauna ganin tana shirin guduwa, gaban aunty ta koma yayin da aunty tace, " dazon munje Asibitin da Aysha, yanayin wankan jegon datayi ne ban yadda dashi ba.

Cikin kawar da Kai yace, sannu Aunty Amman to ba matsala ko?

Babu insha Allahu sundai bata wasu dan magani.

Sadiya ya kalla dake goye da Khalipa yace, bacci yake ne?

Eh Uncle, tun da aka masa wanka yake bacci

Agogon hannun sa ya kalla, kusan daya da rabi ake nema dago kansa yayi yace ma Sadiya toh baccin nan na lafiya ne kuwa?

Lafiya Lau, yaji dumi ne kawai.

Toh ai yakamata a tada shi, Sadiya kawo shi.

Zuwa Sadiya tayi gurin ta sauke shi a hannun Aliyu yayin da Khalipa yai saurin ware idon shi tare da kuka gaba daya.

Cikin yamutsa fuska Aliyu yace Kuka Kuma, kujimin yaro, nifa banson kuka, a kafa yasashi yana fadin, " yi shiru mana"

Hmmmm ai tunda ka tasheshi Kuma saiya sha nono tukun ko zaiyi abun arziki.

Zaiyi shiru Aunty, mikewa yayi yana mishi wasa saidai karama tsandarewa da ihu yake dan haka ya Karasa gaban Aysha ya mika mata shi yana fadin, " bashi Nono.

Amsan sa tayi sannan ta sashi cikin hijjabinta, tsayon lokaci.

Zuwa can Aliyu ya kalleta yace," ya haka ne, kin wani takureshi babu ta inda numfashin sa ke fita.

Juyawa ta karayi domin kaucewa ison Aliyu yayin da Aliyun ya shiga fadin, " aunty wai haka take yi ne daman ko ganina ne??

Haka take Aliyu, ai Naga kanwar tawa akwai kunya.

Kawar da zancen Aliyu yayi da fadin, aunty naga an fara gyaran fah.

Cikin kallon idon Aliyu tace, " da wuri haka?, koda idan an gama sai arufe duk ba matsala bace,

Bangane sai a rufe ba aunty?

Eh mana, kafin lokacin da za'a yaye Khalipa.

Dariya Aliyu yayi harya fitar da sauti, sannan yace' " haba Aunty, kina nufin bazataje can gidan ba sai anyi shekara nan gaba? ai wannan bama abun da zai yiyu bane.

Au haba?

Allah aunty, ni ko yau banki mutafi ba.

Jin haka Aysha ta mike tabar falon yayin da aunty da Aliyu sukaci gaba da tattaunawa tsakanin su.

Hakace ta cigaba da kansacewa kullum da yamma Aliyu ke zuwa gitan aunty, hira suke sosai tsakanin su, dan haka shakuwa takara shiga me karfi, yayin da ya dada sabawa da aunty Rukayya da yaranta hakama Fahat.

Satin ta Uku a Nigeria, Daddyn Ayaha ya yazo ganin inda take, gidan aunty Rukayya ya sauka kamar yadda Innawo ta bashi adireshin farin ciki Ayaha ta shiga mara misaltuwa wadda har saida ta fara kwalla, sai dare Aliyu yazo ya kaishi gurin Baffah sannan ya fita ya basu guri.

Tattaunawa sukayi ta fahimta tsakanin Baffah da Daddy, inda akarshe ya dauki kudi daidai gwargwadon iyawarsa ya bawa Baffah acewarsa a sayawa Aysha kayan daki, nan Baffa ya shaida masa ya saya mata komai amman duk da haka yaki karba.

Washegari Daddy yayi sallama da Baffah cikin girmamawa da mutunta juna, Aliyu ne ya dauke sa ya sake komawa dashi gidan Aunty sukayi sallama da Ayaha sannan yakai shi Tasha.

Bayan kwana biyu da tafiyan Daddy Aliyu yazoyiwa Aysha Sallama dan washari zaiyi tafiya wadda sun gama tsarawa da aunty yana dawowa zata tare.

*********

Yaushe zaka dawo??

Sati 6

Zaro ido Aysha tayi cikin baccin rai tace nifa banson tafiye tafiyenan, Kuma yaya Aliyu har sati 6??

Kanta ya rike da duk hannun sa biyu, sannan yace, " kiyi hakuri yanayin aikina ne, ki shirya dana dawo ko kwana daya bazan bari ki karaba zamu wuce gidan mu, nakosa na ganki cikin farin ciki.

Yaya Aliyu ko yanzun bana cikin damuwa ai, damuwata daya Mamana.

Karki damu mucigaba da addu'a insha Allahu za'a daidaita, hannun sa yasa ya cire mata kwallar data taro agefen idonta sannan yace, " kimin murmushi karkisani in tafi da damuwa.

Dagowa tayi daga jikinsa tana murmushi me kama da yake tare da lankwasa hannunta.

Ganin haka Aliyu ya mika hannun sa ya ruko nata, kibar dan lankwasa hannun nan, wannan karon bazan Kara kwanakin ba insha Allahu, sunbatanta yayi sannan yace kimin addu'a.

Adawo lafiya Allah ya tsare.

Ameen ya fada sannan ya saketa ya juya.

Tunda Aliyu ya tafi aunty gyara Aysha take dan ta kula ya zaku ta tare, har mamakin Aliyu aunty take, gashi dai Aysha goyone da ita amman rawar kafar da yake akanta bashi da banbanci dana wadda za'akai masa sabuwar amarya dal, abu daya ke kwantar ma aunty da hanka idan ta dubi Aysha taga yadda Allah yayi mata surah mekyau, babu me kallonta yace wai ta haihu, sau daya aunty ta taba ganin nonon Aysha yayin da tayi mamakin kamar ba shayarwa take ba, sosai ta yaba hallitan Aysha wadda take tunanin ko kyanta ne ke ruda kanin ta, yaron ma ba me kallon shi yace nata ne kasancewarta fara tass shikuma baki, gashi bata nuna wani damuwarta akanshi.

Ranar da Aliyu ya cika sati 3 da tafiya Aysha ta tashi da kewanshi sosai, gani take kamar shekara yayi, Kuma wai yanzun nema yayi rabi, kwalla ta share sannan ta debo kayan Khalipa ta fito tana kokarin wankewa, kallonta Sadiya tayi dake bakin fanfon tace, " Aunty Aysha ki

barsu na wanke.

Barin wanke Sadiya, nagaji da zama ne.

Tahowa Sadiya tayi suka shiga wankin tare sunayi suna hira, tas suka wanke sannan suka shiga dauraya.

Jimmmm Aysha tayi, Sadiya naji Karan mota ta shigo gidan nan.

Nima naji aunty halan Abbanmu ne tunda Uncle baya na......

Cak ta tsaya ganin Aliyu tsaye a bayan Aysha yayin da taga yasa mata Hannu abakin shi alamar tai shiru.

Kokarin sunkuyawa take domin tacigaba da daurayan yai mata nuni data koma daki da hannun sa, dan haka cikin sauri ta maida kayan cikin bahon tana fadin aunty Ina zuwa.

Aysha da batasan me yake faruwa ba ta cigaba da wankin ta, shiko Aliyu bokitin ruwan dake bayan Aysha ya sunkuya ya dauka ahankali sannan ya koma nesa da ita ya rage ruwan akasa sannan ya juyo ya daga bokitin ya shikoshi jikin ta.

Shiiiiiiiiiiii, wayyo Allah na, Ayaha ta fada tare da gantsarewa, runtse ido tayi tanajin sanyin ruwan na ratsata, yayin da doguwar rigarta ta dame jikinta gaba daya surarta ta baiyana, cikin tsananin mamaki ta juya bayanta dan sanin dalilin zuwan ruwan nan jikin ta.

Aliyu tagani rike da bukiti yayin da yake kashe mata ido cikin fara'a sosai yake kare mata kallo.

Kaikakai lalalala wlh bazan yadda ba cikin saurin ta wuwuri bahon da kayan gaba daya tayi kanshi yayin da yai saurin daga hannun sa sama yana fadin, " yi hakuri, yi hakuri, karki jika ni, cikin dariya yake maganar ganin ta nufoshi yasa gudu, cikin dariya sosai, saidai be aune ba yaji ruwan da ka kayan ajikin shi dan haka ya tsaya cak yana kallonta tare da riko rigar kakinsa ta baro jikin shi.

Karan gudun Aliyu da dariyar da yake har yanzun yasa aunty fitowa tsakar gidan cikin zare ido.

Cak ta tsaya tana kallon gidan, duk ya jike ga Aysha sharkaf, hakama Aliyu, kasa ta kalla taga kayan Khalipa akasa, baho, bokiti nan danan gidan ya hargitse.

🕳 BA'KAR FURA🕳*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

Episode 60- 61

Yau naga abun da ya ishe ni, Aliyu menene haka?

Daker ya iya danne dariyar sa aunty wai daka inai mata wasa shine ta shi'ka min ruwa.

Shine ya fara aunty bukiti days ne ya juye min shi ajiki.

Jikin Aysha aunty ta kalla tayi tsamo tsamo sannan ta kalli Aliyu wadda gaban rigar shine yajike tace, " lallai akwai aiki, Aliyu daman haka kake?🤔

Wasa fa na mata Aunty.

Tsugunawa aunty tayi tana kwashe kayan yayin da Aysha ta shiga tayata, aunty kuwa fadin take, " dan Allah ji, yanzun wannan haukan zakuje kunayi agidan naku, naso da ace Ummi taga wannan haukar taka.

Dariyarsa ya fadada tare da fadin, Allah sarki Ummi na.

Nan danan yaji tunanin Ummin sa ya dirar masa , cikin sauri ya juya aunty natafi inyi wanka daman banje gida ba.

Mikewa aunty tayi tabi bayan shi tana fadin ajike zaka tafi?

Toh yaya zanyi aunty, banso yara su ganni ajiki.

Har bakin motar aunty ta biyoshi, yayin da ya shiga motar ya zauna aunty tace, "amman dai bayau bane tarewar taku,  yau satin ka Uku da tafiya.

Yaune Mana aunty.

Sati fah shidda kace zaka yi.

Eh amman Aunty Aina gaya miki nadaina gaya mata gaskiyar ranar da zan dawo karawa zan dinga yi saboda gudun matsala.

Eh toh amman duk da haka ka Kara mana ko sati daya ne.

Ya mutsa fuska yayi, haba mana aunty, ko tausayina bakiji, yanzun idan wata tafiyan ta taso min nan da Sati  daya natafi kuma kikasan yaushe zan dawo?, Nidai anjima zanzo mu tafi inyaso idan San tafi saina kawota ku karasa kafin indawo.

Murmushi aunty tayi tare da fadin, " ai indai ta riga ta tare shikenan Kuma, jeka anjima zan rako ta.

Aunty gara dai inzo ke zaki iya dadewa baku zoba har nagaji da jira.

Juyawa aunty tayi dan takula Aliyun bawata kunya gare ba, fadi take nidai nace karkazo zan kawo ta.

******

Misalin takwas da rabi na dare Aysha ce Da Aunty Ruqayya acikin dakin Hajiya mahaifiyar Baffah.

Khalipa rike a hannun Hajiya tana kare masa kallo idon ta cike da kwallah take fadin, "bawan Allah, Allah yama rayuwarka Albarka.

Ameen aunty ta fada yayin da Aysha tai kasa da kanta ko iya dagowa bata yi.

Hajiya ce ta cire kwalar dake idonta  sannan ta kalli Aysha tana fadin, "to ki dago min fuskarki inganki mana ko matsoraciya ce ke me tsoron kishiya.

Sosai Aysha ta karayin kasa da kanta tare da wasa da hannun ta tana zaune cikin hijjabi yayin da take zuba kamshi.

Aunty ce tai dariya tana fadin, Ina ba tsoro sai dai kunya hajiya.

Kunya ko Kuma kishi dai, Kinga ni bana kishi, ki saki jikin ki, nan ma gida ne, Allah ya zaunar daku lafiya ya baku zuri'a masu albarka.

Ameen aunty ta sake fada, yayin da hajiya tafara daga murya tana Kiran sauran jama'ar gidan, babban gida ne sosai Kuma duk family ne, nan danan kuwa suka iso yayin data masu nuni da Aysha tana fadin, ga matar Aliyu, ga Kuma d'anshi sun iso.

Cike da farin ciki suka amsa d'an yayin da kowa ke tofa albarkacin bakin shi, yaron yayi kama da Aliyu sannan suka koma kan Aysha, nan ma ca suka mata yayin da da yawan su suke fadin Masha Allah yariyar son kowa, abokan wasa kuwa suka shiga janta sai dai Aysha ta kasa sukuni, kauna suka nuna mata sosai kamar zasu lashe ta yayin da wasu daga cikin su suke fadin, " su Aliyu suke Nima suci kaniyar sa dayai aure har matar ta haihu be gayawa kowa ba sai kace muna makiyan sa.

Hakuri aunty taita basu, cikin raha da wasa da dariya ganin dare nayi aunty ta masu sallama suka fito.

Har motar aka masu rakiya daker suka bada Khalipa, bayan sun kamo hanya aunty ta kalli Aysha tace, Wannan hajiyar Itace maman Baffah kakar Aliyu kenan, sauran Kuma duk iya lanta ne, basu da matsala ki saki jikin ki dasu, Amman ki iya bakin ki, na kula basu San komai ba, hakan bakaramin  dadi yamin ba, dan Allah kiyi wasa da dariya da kowa amman Banda sakin cikin ki.

Nagode aunty zan kiyaye.

Lokacin da suka Isa gidan Baffah kuwa kai tsaye cikin gidan ta nufa da ita, yayin da duk ta samesu duk  afalon,.

Cikin mutunci nan ma aka taryesu, yayin da Baffah yai mata nasiha cikin hikima, Momy ce take ta dan dandaure fuska Islam da Meenat kuwa tuni suka koma kusa da Aysha suna janta da mgn saidai ta kasa sakewa sabo da Baffah.

Daga falon Baffah kuwa part din dasu Aysha da zasu zauna suka nufa, cikin rakiyar momy, dasu Meenat, wadan da farin cikin su yaki boyowa.

Sosai yanayin tsaren da akama wajen ya burgesu, kaya ne masu kyau da tsada aka zuba, daki biyu ne aguri sai madaidaicin falo.

Duk gidan suka leka saidai suna tura kofar dayan dakin suka hangi Aliyu aciki, Cikin sauri su Islam suka juya Momy ma joyowa tayi,  aunty Ruqayya ce kawai ta shiga.

Momy kuwa tana fitowa falon tace dasu Meenat kuzo mu tafi.

Aysha kadai ta rage agurin, misalin 10 sannan aunty ta fito, au ke kadai ce, su Momy duk sun koma ne?

Amsa ta bata da eh, yayin da aunty tace ton Nima barin tafi dare nayi, Allah ya zaunar daku lafiya ya albarkanci rayuwar ku, Aliyu dake bayan Aisha ne yake amsawa da Ameen, har mota Aliyu ya raka Aysha yayin da Aliyu ya nufi cikin gidan su, Baffah zaune kadai afalon dan haka ya tsuguna agaban Baffah bayan ya gaishe shi yace, " Baffah nazo ne in Kara baka hakuri dan Allah kayi hakuri ka gafarceni.

Dagowa Baffah yayi ciki da fushi yace, " nace ma wani abu ne?, Konama baki ne??

A'a Baffah, nidai nasan kana fushi Dani ne.

Toh Ina zuwa Aliyu, barin tambaye ka, zakaji dadi danka da kake tsananin so kake jansa ajikin ka yai maka abun da kamin?

A'a Baffah bazanji dadiba,Kuma bazan soba Baffah, nasan ban kautaba shiyasa nake baka hakuri, wlh Baffah tsintan kaina kawai nayi acikin matsalar.

Shikenan, kaje kawai dare yayi, kabar yariya ita daya, agurin da bata saba ba, ni ban rike ka arai ba, amman abun na bani takaici, sharadi daya ne zan gaya maka, tunda ka raba yariya da iyayenta karka wulakanta ta, nagaya ma Rukayya ma, banson ka wulakanta yariyar nan, ko kace zaka juya mata baya, kasa aranka amanar ta nabaka.

Insha Allahu Baffah zan kiyaye.

Mikewa Baffah yayi yana fadin Ina zuwa.

Dakin sa ya shiga sa nnan ya fito ya dawo ya zauna tare da mikewa Aliyu wata leda yace, " wannan kabawa matarka Babanta yabani in saya mata kaya, dan haka ka danka mata ahannun ta.

Zuciyar Aliyu fari Kar ya karba yayi godiya sannan ya koma part dinsa ya samu Aysha zaune cikin yanayin tagumi.

Kafar ya kulle sannan ya dawo kusa da ita ya zauna, cikin fara'a yace Yaya dai.

Kawar da kanta tayi cikin wani irin yanayi daya bijiroma ta, bada jimawa ba.

Aysha meyasa na ganki wani iri?

Fashewa tayi da kuka ya Aliyu Ina tunanin Mamana sosai.

Kiyi hakuri komai zai wuce, yau ranar farin ciki ne agare mu, idan zuciyan su yayi sanyi zan kaiki ki basu hakuri.

Hawayen ya share mata sannan ya karbe Khalipa dake hannunta yace, " tashi muje d'aki"

Mekewa tayi har yanxun tana cike da zullumi da tunani.

Gadon yara dage gefen gadon sa ya Isa ya saka shi tare da tofa masa addu'a tsayon lokaci ya dauka yana kallon sa sannan ya waigo ya kalli Aysha da har yanxun take kwalkwal da ido

Kallonta yayi yai murmushi sannan ya nufi toilet, alwala yayi ya fito, tsaye yayi gaban Aysha yana fadin, abar tunanin haka kije kiyo alwala.

Mikewa tayi babu musu, Koda ta fito har ya hau kan sallaya, nuni yai mata data matso sunyi sallan a hankali ta karasa, sai dai duk jikinta a sanyaye yake.

Bayan su idar ya kama kan Aysha yayi addu'a sannan ya sauke hannun sa yana fadin Allah ya kade fitina a tsakanin mu yabamu zaman lafiya da kwanciyar hankali.

Idon Aysha cike da hawaye tace Ameen.

Kallonta yayi yaga duk inda jikinta yayi sanyi yace, " Allah ya sanyayawa Mama zuciyarta, ya kuma sa ta fahimci wannan al'amarin kaddara ce bayin kanmu bane......

Cikin sauri tace Ameen Yaya Aliyu, 😭 hawayen da take makalewa ne suka zobo yayin da take fadin, " abun na damuna yaya Aliyu sosai.

Jikin sa ya jawota ya rungume, yana fadin, " kibar sa abun azuciyar ki yana damun ki, wannan rayuwar ba mutum bane yake tsarawa kansa, wlh Aysha Ina kyamar zinah tun Ina karatu, nasamu damar da zan iyayi amman sabo da nasan haramun ne banta ba ko da wasa. dan haka da abun ya sameni na dauke shi kadara tace, nasani akwai damuwa akwai kunya, duk naji su, amman dole na dake, dan haka kema ki dake ki maida komai ba komai ba mu rungume kaddarar mu, Kuma Ina ganin nan gaba kadan komai zai wuce insha Allahu.

Ya Aliyu, bana tunani komai zai wuce, yayyen Mamah suince sun cireni acikin su, sunce basu bani inaji ajiki kamar indai Umma na raye mmn Sadam na raye bazasu sake bari na taka cikin gidan nan ba bare ma har Naga mama.

A hankali yake shafa bayanta, yana sauke ajiyan zuciya tsayon lokaci sannan yace, " muje mu kwanta., Ki Kuma bar irin wannan tunanin, asalima bana son kina Kira min sunan Umma ko mmn Sadam anan, ni babu ruwana dasu, kema Kuma Ina son kibar sasu cikin lissafin ki.

Dagata yayi yana rike da hannunta suka Isa bakin gadon, sakin hannunta yayi sannan ya rage kayan dake jikin sa, juyowa yayi ya kalli Aysha data hada kanta da guiwa yace"

Kigan bana son haka fah, tashi ki rage kaya kizo ki kwanta dare nayi.

Mikewa tayi kamar yadda yace, " cikin hikima ta shirya sannan ta koma can gefe ta kwanta, tare da mike hannunta ta rike gadon da Khalipa yake kai.

Kallonta yayi yai murmushi har cikin zuciyarsa yakejin tausayin ta, gasu kwance inuwa daya amman zuciya ta rasa nutsuwa, yana kwatanta yadda takeji cikin ransa, saidai yasan dole ne su jurema hakan, har zuwa lokacin da abun zai lafa, dan haka ya fara matsawa gareta ahankali har ya Isa ya rungumeta, lumshe ido yayi yana mejin dumin jikinta tsayon lokaci, ahankali ya fara sarrafa hannun sa jikinta cikin kwanciyar hankali.

Aysha bata yi yin kuren hanawa ko gardama ba, saidai har yanzun mamanta ne cikin zuciyarta dan haka ta kasa nutsuwa.

Ahankali yace, " Aysha menene haka?, Na rakokeki dan Allah ki dawo da hankalin ki nan, dan Allah koma me ke damun ki kicire shi cikin ranki ki ajeshi gefe.

Jin haka tayi kokarin bashi hankalin kamar yadda ya bukata, yayin data lura ya shiga cikin wani yanayi domin zuwa wannan lokacin jikin sa har wani rawa yake yi, hadin kai ta bashi suka shiga faranta ran juna, Aliyu daya susuce gaba daya yayin da yai wurgi da rigar sa kasa ya fara zame kayan Aysha.

Adaidai wannan lokacin Khalipa ya farka cikin wani irin tsandara uhu, lumshe ido Aliyu yayi tare da fadin, Subuhanallahi kashhhhh ahankali kamar me rad'a

Cikin sauri ya sauka yayin da ya nufi toilet, sannan ya dawo  ya dauki rigar sa ya sanya, gurin gadon Khalipa ya nufa ya daukeshi sannan ya dawo bakin gadon yana fadin, ki tashi mana.

Toilet din ta nufa, itama sannan ta fito tazo ta zauna gefen Aliyu cikin sauri da karfi yaron tana fadin toh ya Isa, shiko Khalipa ne rufe bakin ba har saida ya runtasa nonon sannan ya kama mamula babu kama hannun yaro, da ido Aliyu yabishi tare da fadin lallai ma yaron nan, kallon Ayaha yayi yana fadin yanzun Kuma har minti nawa zai dauka yana sha??

Awa biyu ne zuwa uku, tabashi amsa tana Satan kalon shi, yayin da ya tabe baki yace, lallai, gadon ya kwanta ya daura sandar hannun sa kan fuskar sa.

Satan kallon sa tayi, sannan ta d'anyi dariya har ya fitar da sauti.

Yaya dai?, Aliyu ya fada cikin tsareta da ido

Babu. Aysha ta bashi amsa.

Akwai, naga kina min dariya ne.

Ba dakai nake ba.

A'a, dani kike, kuma nasan ne kike ma dariya.

Toh meye?

Kina min dariya ne saboda Khalipa ya tashi.

Dariya Aysha tayi wadda har tasa Aliyu ya dara yana fadin, " zan kamaki Aysha yau dinan basai gobe ba"

Dariya ta sake yi, idan Khalipa ya yadda ba.

Zaima yadda Bari ki gani, Kuma daga yau hakan bazata sake faruwa ba insha Allahu.

Kana nufin bazai sake farkawa ba da daddare?

Eh.

Cikin dariya tace, " maganin bacci zaka bashi ne?

A'a amman bazai sake shiga hakkina ba.

Rufe ido Aliyu yayi be sake cewa komai ba, tsayon awa daya Khalipa ya dauka sannan ya koma bacci, mikewa tayi ta kwantar dashi sannan tahau gadon, ahankali ta kwanta sai dai tana numfasawa taji saukan hannun sa jikinta.

Yaya Aliyu bakayi bacci ba.

Waya gaya miki sabon ango na bacci, bayan yana son ya amsa hakkin sa.

Lumshe ido tayi tana fadin, " nafa gaji ya Aliyu.

Dan Allah fa?, Khalipa ne ya gajiyar dake da tsotso ko?

Kanta ta daga.

Toh bari in sauke miki nawa sai kiyi baccin gajiya gaba daya.

Ni a'a Yaya Aliyu kabari sai gobe.

Aysha bazan iya ba, tsoron me kike?

Zafi ya Aliyu.

Kokarin cire kayan jikinta yake yana fadin bari bazai miki zafi ba wannan karon

Yana kokarin kai hannun sa jikinta Khalipa ya sake farkawa, wannan karon ma cikin kuka sosai, Hannu Aliyu yasa ya dafe kansa tare da sake fadin kashhhhh

*🕳 BA'KAR FURA🕳*
_A true life story_

*Na*
_Fadeela Lamido_

Episode 62- 63

Dariya Aysha tayi kafin ta dauki Khalipa
Shikuwa Aliyu a gogo ya kalla sannan ya rufe idon sa, tsayon lokaci Aysha ta dauka tana shayar da Khalipa sannan ta kwantar dashi gefen ta ita ma ta kwanta, tundaga lokacin Kuma be sake barkawa ba, sai da asuba bayan Aliyu ya dawo daga masallaci ya tarar dashi yanata wasa da kafarsa da hannun sa.

Cikin murmushi ya leka fukan yaron yana fadin, " me wayo' waton kaikadai ne baka yadda ka kwana ba, sai dai kusa da Aysha kanajin dumin jikin ta ko?"

Kamar Khalipa yasan me Aliyu ya fada ya fara dariya dan haka yasa hannun sa ya daukeshi yaci gaba da mishi wasa, shikuwa dariya yaketa yi.

Bayan Aysha ta idan da sallah ta nufo gadon ta dauki yaron yayin da yai saurin waigawa

yana kallon Aliyu, ciki da Mamaki tace, " ya Aliyu ji inda ya bika da kallo.

Ai gara hakan tunda Naga nema kike ki rabani dashi, kina zuwa kika dauke shi.

Toh aini na dauka sauki zaka samu ne dan karya dame ka.

A'a, nifa na daukeshi ba bani shi kikayi ba.

Cikin sauri ta daurashi jikinsa, sannan ta koma ta kwanta, tanajinsa yaita masa wasa misalin takwas da rabi data barka kuwa ganin su tayi suna bacci Khalipa akan kirjin sa.

Misalin karfe Tara ya tashi, lokacin Aysha tayi wanka tayi duk wani yan gyare gyare dan haka wannan karon ruwan wanka ta hadawa Aliyu, sai dai A lokacin da yake kokarin zame Khalipa shima Alokacin ya tashi, Dan haka ta fara tube masa kaya, kafin Aliyu ya fito wanka ma kokarin shirya shi take yi, cikin kayan sanyin sa.

Misalin goma kuwa Meenat ce ta kawo masu abun karyawa, ganin haka Aliyu ya fito da Khalipa a hannun sa yace mata kije dashi ki goya shi.

Cike da dauki ta karfe shi, jikinta har rawa yake, hakama baya taje dashi gida fada suka shiga yi ita da Islam kowa na cewa shi zai goya.

Aliyu kuwa awannan lokacin ne ya samu lokaci ya sake da Aysha harma suka shiga cikin wata sabowar duniya wacce ba a iya kwatantawa, awannan rana Aliyu yaga Aysha Aysha ma taga Akiyu, sun nunawa junan su tsananin soyayyar da suke yi ma juna, yayin da akarshi suka kare da kukan farin cikin kasancewar su Abu daya, kusan wuni sukayi suna soyewa Aliyu yana makale da Aysha ranar duk sallah agida yayi su, sabo da samun makara kafin ya fito wanka an fara sallah.

Hakama Khalipa dake acen yau be samu wani bacci ba sabo da wasan da suke dashi yana masu dariya, ganin ma basa son maidashi gurin Baffah suka amsa kudi suka sawo masa madara suka dawo sukaita dirka masa yana dariya.

Momy ce ta gayawa Baffah kudin da suka amsa madara suka sawo masa, dan haka Baffah yayi Kiran su yace waye ya aiki ku, kuntam bayi maman shi ana bashi ne??

Baffah yana so, gashima kaga sha yake, kallo yayi yaga yadda yadda kamo hannun Islam yayi dariya tare da fadin toh kila suna bashi.

Dan haka Koda daddare ana komawa dashi gida nono kadan yasha yai bacci, agajiye take hama Aliyu da Aysha anci soyayya da rana dan haka da daren ma said ya zame masu gurin hutun su.

Hakace taci gaba da kansancewa ko wacce rana, Aliyu zai bawa su Meenat Khalipa su Kuma suci soyayyar su.

Duk bayan Sati biyu Aliyu ke komawa Garuruwa daban daban, yayin da kowanni lokaci yake karawa akan kwanakin da yake tunanin zaiyi, dan haka basa wani samun matsala har aka dauki tsayon lokaci.

Zama suke me cike da tsafta da birgiwa, mata da mijin sosai, babu fada, babu rima, har suka dauki tsayon shekara uku, zuwa wannan lokacin komai ya canza, Khalipa ya girma yana takawa ko ina, aduk lokacin da Aliyu zaisa kaya saiya nemi irin nashi sannan yake saya, yayi kama da nashi sosai, wani irin shakuwa ne tsakanin Khalipa da Baban shi mai katfin gaske, duk dabi'un Aliyu Khalipa yana dasu, ka kokari amakaranta,  su Meenat sunyi sure wata biyu da suka wuce, an samu canjin rayuwa da dama cikin harda wayar hannu data bazo a hannun al'uma, Kuma Aliyu yaje Cameroon so biyu kenan, kowanni tafiya Aysha na bashi Sako ya kai ma Mamanta, sai dai duk lokacin da da yaje Umma bata barin sa ya taka mata gida da balaki take tare da zage zage take masa har da maman Sadam wadda ta dawo gidan da zama gaba daya da Mijinta da yaranta.

Hakura Aliyu yake ya dawo dan wannan lokacin sulhu yake nema Kuma kullum Innawo nace masa ya daina masu rashin kunya wata kila yadda yake masu yasa suke ganin bakin sa dan ita dai bazatace ga dalilin rigimar tasu ba.

Idi yake bawa sakon idan sun hadu ya bawa Mama, yace inji Ayaha Kuma bayan ya dawo.suna waya da idi yana sanar masa sakon ya Isa, Kuma mama tace ta gode tana gaida Aysha.

A daidai wannan lokacin, wata rana Aliyu ya dawo da yamma  ya samu Aysha bata da lafiya sosai, amai taketa shekawa, duk tayi taushi, ganin ta wani iri ya kasa gaya mata abum da yazo dashi, da daddare misalin 11 ya kasa jurewa bayan ya matsa mata taci abinci yace, " akwai abun da zan gaya miki, dan Allah karki tada hankalin ki, kinsan dai duk me rai mamaci ne ni zan mutu kema Zaki mutu.......

Bakai ga rufe baki ba Aysha ta mike cikin daura Hannu akai ta fasa ihu, shikenan Mamana ta mutu nashiga uku.

Mikewa Aliyu yayi ya rike Aysha yana fadin, a'a wayene yace miki mamace, Umma ce ba Mama ba.

Innalillahi wa inna ilaihir raju'un wannan shine rabuwata da Umma ta har abada nashiga uku banji dadi ba.

Cikin son ya rarrashe ta yake cewa, Aysha menene haka?, Bazakiyi hakuri ba, wanni irin abu

ne kike har haka.

Hannun sa ta ture daga jikin ta, cikin fada take fadin, duk kaine kajamin, tunda na sanka muka fara fada da Umma gashi bamu shirya ba har ta koma ga Allah😭😭😭

Kallo yabita dashi, toh naji nine naja miki, yanzun dai kiyi hakuri.

Cikin matsanancin kuka take fadin, ni tafiya zanyi bazan zauna ba, akwatinta ta fara hadawa cikin sauri kamar ba itace mara lafiyar nan ba, dan haka Aliyu ya tsaya kawai yana kallon ta, kokarin fita take yace, " ke dawo nan ki zauna.

Tafiya zanyi Ina son inje gida.

Ke kike da kanki kenan?, idan har a karkashin ikona kike karki fita, faloma ki dawo anan ki zauna.

Cikin sauri ta saki akwatin tana fito da kayan ciki tana jefan Aliyu dashi, koda kayan suka kare akwatin ta jafa masa, shidai yana zaune yana kallon ta harta gama haukata dakin da jefan sa, da abubuwa, ganin komai ta jefeshi dashi yasata fashewa da kuka cikin surutun shine ya rabata da dangin ta, ganin inda take tone tone Aliyu yayi kasa da murya tare da fadin, " dakata Aysha, Alfarma daya neke nema agurinki, kibar daga murya kar wani yajiyo ki, indai har ni kikemawa ki dawo kusa dani kiyi zaifi, dan banson kowa yajiki.

Bazan dawo ba, Aysha ta fada cike da masifa.

Wani irin tsayawa ya buga mata  wadda yasata fadawa kan gadon batare data shirya ba, yayin da ya Kara da cewa dauko qur'anin ki muyi karatu.

Kin motsawa tayi daga inda take, yayin data shiga maida numfashi tsayon lokaci ta dauka sannan yaji tana fadin, " yi hakuri Yaya Aliyu"

Yawuce Aysha, kiyi bacci da safe zamuyi waya da Daddy zan gaya mishi kina son zuwa danni yace min karkije

Sabo dame?

Yace sunce basa neman ki karki zo.

Kamar yadda Aliyu yace da safe ya Kira Daddy yayin da ya Kara Jadda masu kada Aysha tazo kawai.

Har aka dauki tsayon sati biyu Aysha bata cikin wata walwala, yayin da a kaita zuwa mata gaisu, ita ko mutane gani suke cikin da take laulayi ne ya hanata zuwa.

Bayan wata tara Aysha ta haifi Mubarak yana da wata Uku su Innawo da Ummi sukazo bikin Sadiya, gidan aunty suka sauka, shima Khalipa tunda bikin ya taho ya koma can, sosai Khalipa ya shiga zuciyar Ummi komai nasa irin na Aliyu ne sai yake ganin sa kamar sanda yana karami.

Saidai wani abu da Aliyu ya lura dashi har akayi bikin Sadiya aka gama Aysha bata sakin fuska gaban Ummi, dan haka ranar da zasu zo gidan su ya sameta da mgnr cikin hikima yace, Ummi ta huce, yanzun kam, kullum saita tambaye ki ko, ko awaya ne kuwa, zuwanta nan kuwa na fahimci tana son Khalipa da Mubarak, ko kema kin fahimci haka??

Kawar dakai tayi tare da fadin, " Eh"

Bani labarin yadda kika fahimta kamar yadda Nima nabaki yadda na fahimta.

Ni dai abar maganar.

Me kike nufi?, gaya min menene damuwar ki.

Babu.

Akwai, ki gaya min kawai.

Cikin kasa da murya tace nida ba Sona take ba.

Bangane ba son ki take ba?

Eh Mana, tuntuni bata sona ai.

Kina nufin yanzun kema baki sonta kenan???

A'a, ni ba nufina kenan ba, ai Ina gaishaita hakan ma ya isa..

Cike da bacin rai yace, toh bazai yiwu ba Ayaha, Ashe baki da Kunya, Ummin tawa?, ni wani irin zagi ne dangin ki basu min ba, wanni irin kiyayya ce basu nuna min ba, mena musu??? Kakar ki babu sunan da bata kirani dashiba, tuntuni take azabbatar dani, takaini can takaini can, duk ta gama bata min suna ta zubar min da mutunci, ta jefamu acikin wani hali, amman duk da haka bayan na aureki ban sake mayar mata da mgn ba, soboda darajar ki da nake gani, duk wani wadda ya shafe ki dole na girmama shi......

Toh ya ai Nima.......

Cikin tsawa yace karki gaya min mgnr banza, zan miki duka yanzun nan.

Shiru tayi bata sake mgn ba, yayin da yaci gaba da cewa da wannan maman Sadam din ni mafa inajim zafin su har yanzun, sabo da yadda suka tsane ni, mamace kawai bana ganin laifinta, bakuma Dan bata dashi ba, saidan Ina mata kallon mahaifiyata kwatankwacin yadda nake kallon Ummi, Amman itama tana da laifi, bata nuna miki soyayyar da yakamata uwa ta nunawa danta, yanzun Ummi nama aina mata laifi, da rashin Jin mgn, ta nuna fushinta amman nabasu hakuri gashin tun suna nuna fushin ahakali tana hucewa ce, meye laifin ta?, ninasan halin Ummina, kiyayyar da 'yan gidan ku suke nuna min yasa tai miki abun da tai miki, badan komai ba, sai dan a zauna lafiya, Mama ko haryau bata nemiki ba, duk da nasan cewa makusanta ta ne basu da kirki, Umma na neman kusan hada shekara da rasuwa kenan meyasa bata nemiki ba??, ai tasan kinyi kokarin zuwa Umma tace karkizo, kenan tana nan tana cigaba da bin Umarnin Maman Sadam, su ya kamata kiyi fushi dasu ba Ummi ba.

Cikin share hawaye tace toh nafahimta, kayi hakuri, bazan Kara ba.

Kima Kara kika abun da zan miki, kema ai ke kika dada jagula abin, nasa ki amota kika dashi kika dawo.

Wanni irin kallo ta masa sannan tace, " Allah ya huci zuciyar ka, ganin yaci gaba da mgnr ta cika kofi da ruwan sanyi ta mika masa tana fadin Kai hakuri mana ya Aliyu sai mgn kake ko bagaji bakai.

Kurban ruwan yayi sannan ya tashi ya fita.

*Game bukatar katin gaiyata kowanni iri, inayi, na aure ko suna, saukan Qur'ani mai girma, katin sa ranar aure, kati dai kowanni iri, zaku iya tuntuba na ta wannan number 07014197556 Fadela Lamido, cikin farashi me sauki, Harda Video me motsi, da Kuma wadda zakaga alamar hannun na rubutawa, ku garzayo kuyiwa 'yan uwa da abokan arziki, babu tsada👌🏻*

Su Ummi kwana biyu sukayi agidan ita da Innawo, sosai Aysha ta tarbe su cikin mutunci da fara'a ta saki jiki da Ummi sosai itama Ummi taji dadin haka, aliyun sosai yake Jin dadi ganin yadda Ummi ke kula da Aysha fiye dashi kansa, aranar suka koma Cameroon, bayan sun dawo daga rakiyar su ne Aljyu ya kula Aysha fushi take dan haka bayan sun dawo gida yace, " Aysha akwai alamar nayi laifi ko??

Wani irin kallo ta masa sannan ta dauke Kai.

Ina Jin ki gaya min.

Kaine ranar dasu Unmi zasuzo kace min, wai kasani amota na dawo, nina jawo komai.

Ajiyan zuciya yayi sannan yai murmushi yace, bake kijaba nine na jawo, matso kibani kunnen

ki kiji wani abu, kunnen ta bashi kamar yadda ya bukata,  mgana yayi sannan Aysha ta dago ta kalleshi tayi murmushi tana fadin, " ai da na dawo ba iskanci bane ya dawo dani Kaine na dawo na same ka.... Kasa karasawa tayi tare da fashewa da dariya.

Shima Aliyu dariya yayi tare da fadin karasa bana.

Cikin saura tace a'a wlh bana iya karsawa kunya nake ji.

Kunyawa?

Nidai na yafe, Yaya Aliyu wlh baka da Kunya.

Dariya yayi kamar yadda Aysha ma tayi dariya, sannan yace duk ranar dana Kara ce miki haka zaki min, karkiji kunya.

Bayan shekara goma, Aysha ce da Sadiya zaune amotar su ta tafiya Cameroon, Khalipa Mubarak Ahmad sai dan auta shahit duk suma suna zaune dukkan su yaran Aysha ne, Sadiya danta daya Kuma batazo dashi ba.

Gidan Innawo suka sauka yayin da Ummi taita nan nan da su, sai dai wani abun tashin hankalin tunda ta sauka suke sunturin zuwa kofar gidan Umma amman Maman Sadam ta hanata shiga, ita da yaranta gaba daya da sauran dangin mamanta, musamman aka zaunar da yaran maman Sadam akofar gidan dan karsu barta ta shigo, saidai Aysha ta kasayin hakuri kamar yadda su Ummi sukace tai hakuri kawai kullum saitaje kofar gidan, suma yaran kirarin dukanta suke matukar ta taka masu gida.

Idi ne ya sanar Aliyu halin da ake ciki Dan haka ya kira Aysha awaya yace ta dawo gida kawai, duk da haka Aysha bataji ba saida taje gidan Babanta suzo tare nan na dai fitowa yayi yace mata mam tace taje kawai tana mata addu'ar Kuma zai sameta duk inda take, tayi hakuri, shima Daddy hakuri ya bata yayin da Aysha ke kuka sosai.

Ranar da Aysha zata dawo saida ta koma gidan gida sannan ta tura matar sa tace ma Mama dan Allah tazo nan su gaisa amman sai ganin matar idi tayi tana fadin, " Aysha kiyi hakuri wlh har mun kawo zaure da ita Maman Sadam ta biyomu cikin masifa ta rufeta da fada wai ai tasan gurin ki zataje.

Kuka Aysha tayi sosai sannan ta amshi number matar Idi tace mata dan Allah ta amsan mata number Mama ta turo mata.

Ko bayan sun koma gida Koke koke Aysha taitayi, rarrashinta sosai Aliyu yayi mata tare dayin duk wani abun dazai kwantar mata da hankali.

Bayan sati daya matar idi ta turo mata da number Mama, tun daga wannan lokacin suke gaisawa da mama cikin sirri babu wadda ya sani cikin yan uwanta, Daddy kuwa baya iya hada shera batare dayazo ya dubata ba, wani lokacin harda kannenta yake zuwa su mata kwana biyu, sannan yana kawo mata sako inji mamanta, itama tana saya mata abu akai mata amman har aka sake kwashe shera goma bata ga mama ba, wadda yai daidai da shekaranta 20 a Nigeria duk da cewa abubuwa sun faro da dama cikin harda rasa Innawo da Ummi, lakacin rasuwar Innawo Aliyu da aunty Ruqayya ne kawai suke je, yayin da lokacin rasuwar Ummi har Baffa da su Islam ma sunje, Aliyu kuwa gaba daya yaran shi ya tarkata amman beje da Aysha ba dan har wannan lokacin yana samun labarin irin kalamin maman Sadam akan Ayaha, Kuma duk rasuwar nan da akayi masu babu wannda yazo gaisuwa daga dangin Aysha sai Daddy, tundaga yaran nan hudu Aysha bata sake haihuwa ba, Khalipa ya zama saurayi meji da gayo wadda ya dauko halin baban sa sak, zuwa wannan locin Aysha ta saki jikinta ta saba da mutane musamnan Sadiya, dan itace akayi komai gaban ta.

A yanzon Suna waya da Mama duk sanda taso, abangaren Aliyu kuwa, har wannan lokacin yana tsananin Jin Aysha cikin ransa, sannan duk wani wadda zai kawo masa sukan Aysha daga ranar sun raba jaha dashi, shera 20 kenan babu wadda ya taba Jin kansu, sosai Aunty Ruqayya ke mamaki wadda ayanzun ita ta zamewa Aliyu uwa, har take kasa Hakuri tace wai Kai Aliyu kuna fada kuwa kaida Ayaha, yakan bata amsa ne da fadin, Munayi mu biyu amman kasa kasa muke da murya dan kada wani yaji mu.

Sosai aunty take farin cike da haka, tare da Kara masu addu'a zaman lafiya, Yaya Fahat kuwa yana nan yadda yake duk da cewa har yanzun magani ake amman babu wani canji

Aysha kuwa tun wannan sallaman da tayi da mahaifiyarta tun lokacin da Innawo tazo daukanta domin tafiya Nigeria basu sake haduwa ba, saidai tana nan azaune gidan Mijinta wadda yake tsananin bata kulawa da nuna soyayya ta hakika fiye da tunanin me karatun, zuwa wannan lokacin Khalipa yana marantar gaba da Secondary yana da shekaru Ashirin aduniya.

Alhamdulillah
07014197556

Anan na kawo karshen Labarin BA'KAR FURA, Ina rokon Allah ubangiji ya sake hada fuskar Aysha da Ummin ta, tana raye basai ta mutu ba.🤲